[3/28, 11:47 AM] UmmuHabibah□□❤: KꞋALLABI...!

A tsakanin Rawuna..

<Babi Na Ɗaya>

~FREE BOOK~

Na

Mai_Dambu

EWF

Har ila yau SADAUKARWAN taku ce Aminan kwarai a gudu tare a tsira tare

Zahran Addah Ramlah

Da

UMNASS din Mai_Dambu

GODIYA TA MUSAMMAN GA SANAH MATAZU

Shimfida.

Kasar gobir na ɗaya daga cikin kasashen hausa na ainihi, ance ita ɗin tsohuwar daula ce kuma wata babbar kasa ce da tayi iyaka da Agades daga arewa, tayi iyaka da Zamfara daga Kudu, tayi iyaka da Mayali daga Gabas, sannan kuma daga yamma tayi iyaka da Konni.

Amma magana anan itace, asalinsu ba hausawa bane tunda wasu nacewa asali waiy daga gabas ta tsakiya suka fito musamman ma Misira, inda ake da yakinin cewa Sarakuna ukku daga cikin sarakunan Misira gobirawa ne.

Sarkin Gobir Mai daraja Alhaji Abdulhamid Balarabe Salihu ya taɓa faɗar asalinsu a wata fira da jaridar 'Daily Trust' tayi dashi, shine yake cewa:
Gobirawa sun zone daga misira (egypt). Har Yace su jikokin Annabi Nuhu A.S ne kuma sun bar misira saboda wahalar mulki na sarakunan lokacin. Shine suka sauka a wani wuri mai suna Gubur. Daga nan ne suka samo sunan Gobir.

Yaci gaba da cewa daga baya sun isa Yemen, sunyi yaki sosai a kasar saboda su suna da jinin yaki da jarumta. Daga nan kuma sai suka isa libya, a haka suna matsawa har suka zo wani gari mai suna Azbin inda yanzu mutanen Taureg suka mamaye.

Da suka bar Azbin sai suka shiga sahara, har suka kafa wani gari mai suna Magali, daga baya sai suka bar garin izuwa wani mai suna Surukul

(dukkansu yanzubsuna jamhuriyar Niger ne). A hankali suka riski birnin lalle da gwararramu a karni na 15 zuwa na 16. A lokacin kuwa, Sarkin zamfara Abarshi ke mulki wanda yake da zama a Katanga, kuma an samu har ya auri ɗiyar sarkin Gobir mai suna Fara, wadda ta haifi Sarkin gobir Ibrahim Babari..

Kafin Babari ya zamo sarki, ai sai dayayi faɗa da Sarkin Zamfara na lokacin kuma yaci karfinsa. Akan haka sarkin Zamfara ya kuduri niyyar halakashi, amma sai yayarsa ta maido dashi kasar mahaifiyarsu watau Gobir, a haka kuma har ya zama sarki (Watau yayi gado ta wajen Uwa).

Babari ya roki Sarkin gobir ya bashi wuri a yankin Zamfara inda zai zauna, amma sai aka gargaɗi sarkin Zamfara da cewa kul ya baiwa Babari gurin zama domin nan gaba zai iya mamaye zamfara dukkan ta, ai kuwa daga bisani hakan ne ya faru, da yaki ya ɓarke a wajajen karni na 16 zuwa na 17, sai da Goburawa suka cinye har Alkalawa da yaki. (abinda ke nufin inda suke zaune ayau asali kasar zamfara ce)
Sarkin Gobir Abdulhamid ya kara da cewa " A lokacin Sarkin Gobir Bawa Jan Gwarzo (Karni na

17), ance an ruwaito cewa Ko zakaru basa cara sabida jarfin tsafinsa, kuma aduk yake-yaken da sukeyi, gobirawa basu taɓa mika wuya ba. Ance sunfi gwammacewa a kashe su akan su mika wuya, shiyasa ake musu kirari da 'Gobir gidan faɗa'.

Sarkin yace " Bawa jan Gwarzo bai taɓa yaki da Shehu Usmanu ba A zamanin jihadi, maganar gaskiya ma itace shehu ya koyar da 'ya'yan Bawa, ciki harda Yunfa, Atiku, Bello da Mayaki. Ance ma saida shehu yayi musu nasiha da kada su bari a samu rarrabuwar kawuna a tsakanin su.
Sarkin yace " Mutanen dake kusa da Bawa sune suka haɗa kiyayya a tsakanin su, wanda yayi silar shehu yabar Alkalawa, daga baya kuma yaci gaba da jihadi a sassan sokoto.
Dan gane da tsagun gobirawa, Sarkin yace asali basu da tsagu a fuska, amma sabili da yake-yake ne yasa suka rinka tashi daga nan zuwa can, don haka suka ɓullo da tsagu domin su rinka shaida junansu.
(Bari mu daura labarin)

(Yau Laraba/11/ ga watan Rabi'ul Auwal 1809. Karni na goma sha takwas)

Da gudu Mahayi ya shigo masarautan tare da rike wasikar hannun shi, ya shiga har farfajiyar masarautan. Tsare shi sarkin Fada yayi tare da cewa.

"Ilu dan Audu, Audu dan Uwaisu. Farin me farin aniya, baka zama jakadan alkhairi sai ta sharri"

Dira yayi a kan dokin sannan ya wuce fada Sarkin fada yana biye da shi. Ilu dan Audu, dan sako ne duk wani sakon da zai zo fada toh ta hannun shi yake zuwa, kasancewar masarautan sun tafi yaki da wasu kabilar da take gabashin masarautan kuma babban abun damuwa shine karfin da wadancan kabilar suke da shi idan suka samu karfin ta hanyar kabilar Fulani waɗanda ake kiran su Rumada.

Kasancewar suma Rumada bayin Fulani ne, kuma suna da matukar tasiri da karfi amma basu cika shiga abinda babu ruwan su ba, abinda ya kuma fusata masarautar Gobir ba kome bane sai yadda kabilar da suke kara samun ƙarfi sama da kowacce ƙabilar. Kasancewar su din kabilar sun fito daga kwararrafa ne, ana da yakinin Banza Bakwai ne, da suke da makotaka da Zamfara. Kafin Gobirawa su kwaci mulkin Sarkin Zamfara. Wanda shi da wadannan kabilun guda uku suka cure domin yaki da gobirawa.

Zubewa yayi a gaban Sarkin rikon kwarya, wato Sarki Bello na biyu.

"Allah ya taimaki mai martaba! A can filin dagga ana fama da yaki kamar yadda Yayanka mai Martaba sarki Ibrahim ya tafi wakilta wannan masarautan." Shiru yayi lokacin da Zakaria ya shigo. Sunkuyar da kai tayi kafin ya d'ago kai yana kallon Sarkin Bello me rikon kwarya ya ce.

"Sai hakuri, domin sarki Ibrahim ya kwanta dama" a wani irin zabure mai martaba sarki Bello ya Mike. Jikin shi yana rawa.

"Karya kake bawa! Karya kake bawa! Taya Jarumin sadauki irin mahaifina ba zai mutu a banza ba" wani irin kuka ya sake tare da kallon Sarki Bello cikin shashekar kuka ya ce.

"Wallahi ba zan yafe hakkin mahaifina ba" riko shi sarki Bello yayi cikin matsanancin tausayi yana bubbuga bayan shi yana cewa.

"Kayi hakuri, Allah ya gafarta mishi."

Abin tausayi baki daya masarautan ta kare yaran kabilar Gobir da suke mulki sun kare sabida yakin da suke da kuma faffatawa.

"An binne shi a can, amma mun samu nasarar farattakar mayakan da maciya amana, sannan mun dauko wasu yan tawaye zamu tawo dasu da bayin da aka kama"

Cikin wani irin shashekar kuka Zakaria,.ya mike tare da nufar cikin gidan sarautar. Wanda izuwa yanzun labarin mutuwar mai martaba sarki Ibrahim ya karade cikin gidan. Kasancewar yana da ƙarancin shekaru yasa ta zama abin tausayi. Mikewa Sarki Ibrahim yayi sannan ya kalli Chiroma.

"Idan kome ya lafa zan ba shi mulkin shi tunda na shine ni rikon kwarya nake" ya fada cikin sansayar murya wanda dama halin shi.

"A'a Mai Martaba, idan har kai aka bawa mulkin muna da yakinin yaki ya kare, idan kuma aka bawa wani tabbas yanzu aka fara domin yakin bai kare ba" inji Galadima. Domin yakin har da Wazirin masarautan aka tafi.

"Wannan maganar gaskiya ce, matukar muka sake ka bar mulkin baki daya masarautan Gobirawa zai zama tarihi. Amma idan muka barka akan mulkin nan ba mamaki zamu samu salama da nutsuwa, sannan Allah ya albarkaci da abubuwan cigaba. Idan kuma aure kake bukata zamu nima maka auren daga ya'yan manyan masarautu. Da suke zagaye da mu har ketaren mu." Inji Chiroma.

Duk yadda Sarki Bello ya so kauce musu, haka suka mishi dabaibayi da mulkin. Har aka dawo da mutanen da suka tafi yaƙi. Inda aka dawo da Waziri cikin wani mugun hali. Domin kuwa ya jikata sosai dan dole aka kai shi gidan shi Jinya.

A cikin gidan sarauta kuwa akwai yaran Sarki Ibrahim marigayi, uku mace daya, maza biyu Zakaria shine Babba mahaifiyar shi me Suna Gambo, baiwa ce kafin sarki Ibrahim ya yantatta. Sai matar shi Ajuji wacce ya haifi yara mata biyu. Fulani Kyauta domin an tabbatar da ta jima kafin ta haihu har ana mata gorin haihu. Sai na biyun su Yakubu ana kiran shi sarkin yaki,. kasancewar an haife shi ne a wani rangadin da Sarkin yakin sarkin musulmi yazo Zamfara zai wuce sokoto. Shine ya tsaya a masarautar Gobir. Inda yana isa aka ce ai mai dakin sarki tana kan gwiwa. Shine yayi tofi aka kai mata ai kuwa tana sha ko minti ɗaya ba a kara ba ta haifu danta namiji. Koda aka kawo yaron fada, Sarkin yakin sarkin musulmi yayi mishi addu'a.

Sannan ya wuce anan mai martaba da manyan fada suka yanke hukuncin yiwa Sarkin yakin sarkin musulmi wato Sarkin Bauchi a lokacin.

Sai sauran dakunan kuwa kwarkwarori ne, kuma basu haihu ba.

Duk wannan yanayin da aka gaya musu labarin yasaka jikin kowa yayi sanyi musamman da masu kishin akan danta ne zai yi mulki, sai gashi an fitar da sanarwar labarin Sarki Bello za a rantsar. Kasancewar Yarima Zakaria shekarun shi sha takwas ne, sai Yakubu me Shekara sha biyar, Fulani Kyauta. Tana gab da za a aurar da ita ne.

Wannan tsarin da akayi ya fitar da tashin hankalin da ake samu tsakanin Gambo da Ajuji, dan dole suka rungume ƙaddara. A lokacin Sarki Bello yana da shekaru talatin a duniya, babban damuwar shi yayi rayuwa ta yanci da walwala yana son koda zai yi aure baya son ya auri yar mulki domin zata iya saka shi ya bukaci mulki shi kuma abinda ya tsaya nake nan.

Bayan wasu watanni aka shirya bikin nadin sarautar sarki Bello, wanda aka kai gayyata ga sarakunan yankin gaɓar kogi Chadi zuwa bainuyo, sannan aka kai har zuwa kwara kasancewar tarihi ya tabbatar akwai milawa Fulani ne kuma Gobirawa ne, sannan aka kai yankin kasar Gombe inda Sarki Muhammad kwairanga yake mulki.

Sannan aka kai masarautar Kano, zuwa Yola inda Modibbo Adama yake mulki. Sannan aka kawo Bauchi ga Sarkin yakin sarkin musulmi. Kafin aja wuce da na zaria, domin shine nadin sarautar da za ayi na Muhammad Bello na biyu. Wannan nadin sarautar ya tara al'ummar sarakuna daga manyan yankunan arewacin kasar. Sannan an kai sakon gayyata har maradi domin can ma akwai wata masarautan Gobirawa. Kuma sun tabbatar zasu zo ayi bikin da su.

Lokacin da za ayi nadin Sarkin Musulmi da kan shi, ya halarci taron nadin sarautar, yadda mutanen Fada suka gayawa sarki Bello, sun roke shi da ya fada ba zasu kuma yaki ba, idan ma za ayi yakin toh sai ta hanyar yad'a kalmar Allah. Wato jahadi.

Haka kuwa ya kasance, mulki aka bashi bayan nadin sarautar da kwanaki Allah ya amshi rayuwar Wazirin sarki Ibrahim,me suna Musa dan Musa. A lokacin yaran Waziri sun so a basu sarautar gidan su, amma kasancewar akwai sauran sarakuna sai suka bada shawarar a bawa Zakaria waziri duk da lokacin shi din Yaro ne, haka Sarki Bello ya janyo shi har cikin fadar. Sannan yaki kallon Zakaria a matsayin dan Yayan shi, kallo yake mishi irin na wa da kani.

Shima kuma Zakaria yana mugun ganin girman Sarki Bello, idan ka cire Yakubu da kiri kiri yake adawa da sarki Bello. Tare da gaya kishi cewa.

"Ka bar murna karen ka ya kama kura! Inda rai da rabo wata rana kallo zai koma sama shawo ya dauki giwa" domin wani irin masifaffen kishin sarki Bello yake sannan ba iya shi ba hatta dan uwan shi Zakaria. Sai da Yakubu ya farmake shi kamar zai kashe shi.

Wannan yasa aka saka Idanu akan Yakubu domin adawar shi tana kazamta. Sannan bai da burin da ya wuce ya nufi Katangar bayi ya saka ana ware mishi kyawawan yan mata ana kai mishi dakin shi. Yana tarayya da shi kuma mai Martaba yaji labarin bai da ikon ya hukunta shi domin a cikin wannan yanayin baya son a samu rabuwar kai...

Hello' Fanmily dama na gaya muku zaku iya samun posting kafin Azumi... Karku manta labarin FREE BOOK ne... Comments da Voting shine price na labarin.

And inshallah zai na zuwa muku sau uku a sati Daya.. Saturday. Monday. Thursday inshallah.... Sabida ina da abubuwa dayawa kuma ina typing paid book so.

#Freestory

#mai_Dambu....

[3/28, 11:47 AM] UmmuHabibah□□❤: KALLABI....!

A tsakanin Rawuna

<Babi Na Biyu>

~FREE BOOK~

<Babi Na Biyu>

Masu iya magana kan ce wanda ya riga ka kwana zai rigaka tashi haka.. inji Malam BAHAUSHE.

Abinda ya faru kuwa duk yadda Sarki Bello yaso had'a kan Yayan Wan shi abun ya ci tura musamman yadda Yakubu yake kara baudewa,yana kara fusata ga kuma yadda yake illa a cikin katangar bayi yasa Sarki Bello ya taka har wurin Ajuji.

Tunda ana gaya mata sarki yana iso gare ta, ta gyara zaman alkyabarta ta, sannan tayiwa Jakadiya Rama magana da cewa.

"Jakadiya zai iya shigowa"

Duk da bata sannan me ya kawo Mai Martaba sarki Bello ba, amma tayi imanin cewa ya kara mata daraja a cikin gidan duk da ba a bawa danta mukami ba, amma tabbas haka ya nunawa Mutanen cikin masarautan cewa ai tana da kima.

Cikin sallama ya shiga babban zauren ta, wanda yake dauke da bayi mata suke mata hidima. Zubewa duka yi tare da gaishe shi. Jakadiya ta amsa.

"Mai Martaba ya amsa, kuma yana son magana da uwar Dakin ku zaku iya fita"

Fita suka shiga yi daya bayan daya, dakin ya rage sai Jakadiya.

"Me ke tafe da Sarki Bello?"

Murmushi yayi cikin dattako, sannan ya ce mata.

"Nazo ne domin kece kika fi dacewa ki gargadi Yakubu. Barnan shi a cikin masarautar nan tayi yawa. Idan ya cigaba da haka abun ba zai mana dadi ba? Kin san da naga ake gane zurfin ruwa, kuma idan har akwai sa'a toh tafiyar ba zata zama mara amfani ba"

Ya cire mulki yayi mata magana ba fahimtar juna. Amma sai bata ce kome ba, asalima tayi na'am da yadda yazo mata domin tasan ba karamin al'amari bane a Kore Yakubu daga masarautar.

Dan haka bayan tafiyar shi, ta saka aka kira mata Yakubu da yake dakin shi yana masha'a da wasu bayi mata. Sai da ya gama abinda yake sannan ya saka aka fitar da baiwar. Yayi wanka ta shiga cikin gidan sarautar. Dakin Mahaifiyar shi ya nufa. Sannan ya zauna yana kallon kayan marmarin da aka ajiye mishi. Tab'awa yayi tare da cewa.

"Iya kiran me kika min?" Shiru tayi kafin ga fara cewa.

"A yayinda Duniya ta juyawa fatake baya, zai yi wuya ya fahimci inda ya dosa, ba zan tsawaita nusar da kai zafin da yake cinkushe cikin sahara ba, sai dalilin me matukar muhimmanci ya iske ka."

"Kenan an samu baragurbin da ya fitar da tsumammiyar ma'ajiyata? Lallai dan Mutum mugu ne, yayinda yake take laihin shi ta hangi na wanin sa!"ya fada cikin matsanancin fushi,

"Ke Tallafi bani ruwan randan kasar nan ko zata sanyayya zuciyar Yarima na! Kome yayi tsannanin sauki yana tare da shi. Ba a kashe zafi cikin ruwan sanyi. Koda ciwo ne da zafi ake kashe zafi." Mika mishi ruwan tayi tana cewa.

"Duk iyawar me iyawa matukar zai kai tufkar hanci dole a canza launin farautar... Kasan yadda ake farautar Zaki? Dan haka karka sake a kuma ɗibo gurbattani a kawo min domin ba zai mana dadi ba, kuma zasu zantar da duk hukuncin da yayi musu. Ka tausayawa Yayarka ta samu majingini a tare da kai"

Wannan abin yayi mishi tsauri amma babu yadda ya iya dan dole ya hakura da gargadin da ta mishi. Har zai fita ta Kalle shi ta ce mishi.

"Ban sani ba ko akwai wani darajar bayan haka a cikin fadar shi. Amma naji yana faɗin ba zai taba wanzar da zamanin shi ba tare da ku ba, shi din ma kamar wata damar ce da ta wanzu a gare ka. A koda yaushe zaman lafiya yafi zaman dan sarki idan ta kama da shi sarkin da kan shi. Haka ya ce nai"

Gyada kai yayi kafin ya fice daga zaurenta.

***

Kasurgumin daji ne mara kan gani me ɗauke da manyan kwazazxabai da kurmi. Hadi da manyan duwatsu, dan tafiya kadan zaka yi zaka taradda wata korama, sauka suka yi akan dawakan su. Sannan suka daure dawakan kafin suka isa bakin koramar wacce take fitar da wani sirrintacciyar zafi da dumi. Daukar wasu fararran duwatsu suka yi sannan suka watsa a cikin koramar.

"Ga bakin gida, ga irin mutanen karni ga masu bukatar biyan bukata." Rabewa ruwan yayi suka wuce ta kan hanyar da ruwan yake, babban fili ne iyakar ganin ka idanun ka.

A hankali suke takawa har sun ka isa wani wawwakeken lambu, shiga cikin lambun suka yi tare da tsinkar ɗaɗɗan itacce, suka fara sha. Wani irin hadiri ne ya gangamo kafin kace me garin yayi matukar duhu.

Dariya wani dan tsabubburin mutum ya saka tare da durowa gaban su, kamar dan biri.

"Akan mulkin masarautan ku! Ai ku koma daga nan zuwa shekaru goma ku dawo. Amma ba makawa wasu shudadden al'amarin zai faru. Imma a mutu Imma ayi rai sakon daga kai da kai ne. Kƴwayoyin halittar bil'adama tana bisa ga muradin dan haka ga wutar can. Gutsira dan itaccen ka kashe kiyayyar ka... Amma ba zaka tab'a soyayyar da take cikin dinbun zukatan al'umma ba. Akwai Sa'a amma zama haka na tsawon shekaru goma akwai barazanar ko ta kwana wannan hangen dan tsinbura ne maza a tafi ayi ta aikin ba tare da kallon abinda zai dawo ba. Domin har yau taurarin ba zasu yi gamayyar halitta ba. Wannan a saka a cikin babban magudanar ruwan masarautan.. Sa'a tana gare mu"

Fitar da sulallar zinari yayi kafin ya zuba mishi.

"A cikin matan da suke cikin masarautan bayi ayi kokarin tara su a kara gine katangar masarautan da su... Kamar yadda muka yi bayanin karnin da ya gabata"

Godiya suka Mishi sannan suka juyawa tare da barin dokar dajin.

"Kana ganin idan har aka yi haka babu wata matsala?"

"Gaskiya babu domin na yarda da shi sama da kowa bani tab'a yarda da aikin kowa sai dan tsinbura"

Duk da kasancewar Muslunci tana wanzuwa a cikin masarautan amma kuma sha'anin bokanci yana kara samun damar wanzuwa a cikin masarautan.

**

Bayan kwanaki Yarima Yakubu ya cigaba da zuwa fadar ana zama dashi sai dai zaman babu wani alkhairi. Domin kiri kiri yake karta rashin arzikin shi. Idan ran Waziri Zakaria yayi dubu b'aci yake. Yau ma ana zaune ana fadanci ya shigo cikin fadar daidai magatakarda yana karanta sakon Sarkin Gombe.

Kallon Sarki Bello yayi kafin ya kalli magatakarda ya ce.

"Kai tafi can! Ka koma ka gayawa Sarkin Gombe cewa shi wannan baffan nawa kasancewar jimawa da yayi yana zama basir ta cinye mai kuzarin shi"

"Tir da halin ka wallahi." Kallon Zakaria yayi tare da cewa.

"Gaya min uwanai ta min baki na? Ko ubanai ya min baki na? Kaga ba zan iya dundduke ina zaman jiran gawon shanu bayan nasan me bisa kai nai. Imma ka yarda an ci amanar mahaifin mu imma ka zauna zaman karen farauta sa" ya fada yana kwabe fuska.

"Hattara dai kasan me zaka fadi a gaban Mai Martaba sarki Bello."

Wani makawa Sarkin Fada yayi harara.

"Kai kunshe min bakinka. An ce maka kowa maroki ne? Sai manyan suna zance a bisa sha'anin mulki ku da kuke karakad'anna karan kad'a miya kuna tsomma bakin ku acikin zancen mu"

Cikin fushi Waziri Zakaria zai magana , Mai Martaba ya d'aga mishi hannu.

"Da kabarni na gyara mishi zama, me bakin zuciya kawai. Allah kadai yasan Meye zai iya aikatawa dan fuskar shi ta nuna rashin amincin shi"

Wani irin kallon banza yayi tare ba mikewa yana kallon Sarkin Zagi ya ce mishi.

"Ka gayawa musu duk wata tafiya tana bisa hanya ce amma tashi tafiyar da ya hana kara faɗin kadada zata iya fadawa cikin hatsari dan haka a yi nazarin dakatar da yaki."

Shiru fadar ya dauka, shi kan shi sarkin Zagi kasaka magana yayi dan yasan tabbas Mai Martaba yaji abinda ya faɗa Yarima Yakubu ya faɗa.

"Me yasa ba za a dakatar da shi ba!" Murmushi mai martaba yayi tare da kallon Galadima. Mikewa zai yi fadawan da suke tare da shi suka mike tare da kare shi da babban rugunar su, suna faɗin.

"Gyara kintsi mai martaba zai tashi" haka ya tashi suka buda mishi hanya ya wuce fadawa na take mishi baya, har shashinsa.

Kallon Sarkin gida yayi sannan ya ce mishi.

"Ka min magana da Waziri da Galadima da waibai da Chiroma"

"Allah ya baka nasara an gama" ya juya ya fita, bayan kamar minti talatin sai gasu, basu shiga ba sai da Jakadiya ta musu iso. Yana zaune a jikin tuntun, ya ɗan yi kwanciyar hutawa.

Zama suka yi sannan suka kuma gaisawa. Shiru suka yi kafin ya sauke ajiyar zuciya ya ce.

"Me kuka gani da sakon Sarkin Gombe? Sai batun wancan sakaran nasan ya bakanta muku, amma akwai gaskiya a maganar shi. Irin su ba a hana su fadar albarkacin bakinsu. Domin akwai gaskiyar da gyaran da suke sun a cimma."

Ya fada yana wasa da wukar hannun shi. Gyara zama Waziri Zakaria yayi tare da cewa.

"Duk da na kasance yaro ma kananun shekaru ina ga Baffa ka amshi auren ta ko Baba Chiroma ba Galadima"

"Kwarai kuwa Zakaria nima nayi na'am da wannan sakon Sarkin Gombe. Wanbai baka ce kome ba kai da Chiroma" inji Galadima, ajiyar zuciya suka sauke.

"Mun amince, sai dai kasan cikin gidan dama akwai kishin da ake na kujeran da kake kai,ka nusar da ita gaskiyar kujeran domin akan ta Yarima yake wannan shaguben" inji Wanbai.

"Tun fil azal bana jin zan iya zama dindindin akan karagar domin ga me ita nan. Idan al'umma suka bukaci a bashi duk daya ne, sannan ita matar da zata zauna a kasata bana jin zata samu karfin shiga cikin hayaniyar masarautan nan"

"Allah ya baka nasara, batun ka dawo da mulkin ba zai yiwu ba, domin ko al'umma sun bukata. Ba zan taba iya rike wannan muƙamin ba bayan dan uwana Yakubu Yana bukatar shine ɗan haka kai din nan dai kai ne zaka rike mana shi" shiru zauren ha dauka domin dukkan su, sun yarda fa Abinda Waziri ya fada koda an bashi mulkin Yarima Yakubu ba zai taba yarda ba, gwara mulkin ta cigaba da zama a hannun Baffan su domin haka ne zai saka a zauna lafiya.

Sannan ya gyara zaman shi ya ce musu.

"Batun fadada kadada fa?"

"Gaskiya akwai maganar ba zamu yi yaki ba, idan zamu fadadda kadada kuwa dole sai mun gina zaratan mayakan mu sannan mu tafi da'awa idan ba amshi mulkin ba muna da ikon fadadda kadadar mu, a gani na ko da zamu fadadda kadada dole zamu tura yankunan da suke jikin mune domin su cure a cikin mu yadda babu wanda zai mana tawaye. Sannan kuma akwai damar da mai martaba yake dashi bayan an daura auren shi da Fulani Aminatu yana da damar niman kwarkwara daga wadannan yankunnan da zasu shiga cikin masarautar mu."

Girgiza kai yai kafin ya ce musu.

"Bana sha'awan kwarkwarah, mace daya nake bukata sai dai idan halin haka ya taso zan kara aure"

"Toh Allah ya tabbatar da Alkhairi, haka yayi Wallhi" anan sai suka ajiye maganar ba za ayi yaki ba, kuma maganar aure, an shirya manyan daga masarautan suka tafi har Gombe da kome da kome, suka tafi dan har da mata da har da Jakadiya, idan aka ce sai an tafi an dawo ba zai yiwu ba sabida nisar tafiyar.

Duk da haka sai da Yarima Yakubu ya sake ce wani abu.

"Duk matan da suke cikin masarautan nan babu mace sai an tafi har zuwa wata nahiyar an dauko mace gaskiya wannan shine kwaba"

Babu wanda kula da zancen shi domin sun fahimci, lamirin shi babu ta arziki sai ta tsiya kuma da za a bashi damar haka ba zai iya ba, zunzurutun ya kular da kowa ne, shi din gashi nan dai,kamar me almatsutsai, kuma babu abinda yake damun shi.

Ko shi kan shi sarki Bello yana jinjina rashin mutuncin Yarima Yakubu, sannan batun bin yan matan bayin kuwa bai fasa ba, domin har yau yana bin su, kuma idan yayi abinda yake so dasu yai musu barazanar zai kashe su haka yasa musu matukar firgice da mugun tsoron shi....

Ban sani ba gaskiya uzuri sun dan sakoni a gaba idan na kammala maybe Saturday Insha Allah zamu sake hadu amma babu Alhamis.....

#Freestorie

#Mai_Dambu

[3/28, 11:47 AM] UmmuHabibah□□❤: KꞋALLABI...!

A tsakanin Rawuna

EWF

FREE BOOK

Mai_Dambu

<Babi Na Uku>

~Masu azancin harshe sukan ce dakan d'aka shikar d'aka....masana harshe kuwa suka karasa azancin da da tankad'en bakin gado.... Inji Masana harshen Hausa~

Wannan haka yake domin sarakunan baya suna daukar ɗiyoyin su mata masu daraja su hawa wata masarautan, ba dan kome ba sai dan kulla alaka me kyau, sake raya zumuncin su.

Ko nace masarautan buba Yero! Masarautar ce da Fulani suka kafata,karkashin jagorancin Mujaddadi Shehu Usmanu danfodiyo, inda ya turo wakilin shi Muhammad Kwairanga. Ita kanta Gombe an samo ta ne daga wasu kabilun.

Tarihi ya nuna a karni na 13 aka fara sanin garin Gombe, sai dai kafin wannan lokaci an yi wadansu mutane masu karama da sarauta da ake kira ‘Soninke Mandigos’, wadannan mutane su ne suka samar da tsatson garin Gombe, kuma littafin ‘Tarekh-el- Sudan’ (Tarihin Kasar Bakake) na musu lakabi da ‘Fararen Shugabanni’.Wadannan mutane ana kuma kiransu da ‘Kaya- Manga’. Sun mulki yammacin Sudan na wasu karnoni da dama. A cikin Kaya-Manga an samu wani mutum da ake kira Bin-Kaya Mob, wanda sarki ne a wata masarauta da ake kira Mande, a yammacin Sudan din, wanda kuma wannan sarki ya ci zamaninsa a cikin karni na 10.

Sarki Bin-Kaya Mob yana matukar ji da jikansa Bin-Abubakar, wanda har ta kai ko kuda ba ya so ya taba shi. Ya mayar da shi dan lelensa kuma shafaffe da mansa. Hakan ce ta sanya Kaya Mob ya bai wa jikansa wani bangare na masarautar tasa da ake kira Ukuba. Bin-Abubakar kaka ne ga Aliyu Ukuba, wanda shi kuma yake mahaifi ga Usman. Aliyu Ukuba shahararren malami ne, ya haddace Alkur’ani, wanda daga baya aka hada shi aure da ’yar gidan wani attajiri a garin Tibati, inda kuma suka haifi Usman. Zuri'ar Usman ta rayu na wasu tsawon karnoni har zuwa lokacin da suka tashi daga yankin gombe.

A cikin shekarar 1913 Hedikwatar Gombe ta tashi daga garin Gombe zuwa Nafada, wanda a cewar Nasarawa Nafada ta fi saukin zuwa daga manyan garuruwan Arewa irin su Kano da Bauci da Maiduguri da sauransu. Har ila yau a wannan shekarar aka girke sojoji masu lura da shige-da- fice a kan iyaka. Sarkin Gombe Umaru ya halarci wani hawan daba da aka yi a Kano, lokacin da sarki Edward na III ya kawo ziyara Kano. Bayan sarki Umaru ya dawo daga Kano ne, ya sake zabar wani gari da ake kira Doma karkashin Akko. Inda a shekarar 1919 aka

sake rada wa garin suna Gombe-Doma.

A kuma wannan shekarar ce aka mayar da Gombe- Doma zuwa

masarautar Bauci, sannan aka rage mata dagatai zuwa 3, wanda

a da take da 13. Daga nan kuma sai aka dawo garin Gombe.... Takaitaccen tarihin masarautar Gombe.

_____

Masarautan Gombe

Kallon Kanin shi jibril wanda suke kira Babayo, yayi cikin nutsuwa sanna ya ce mishi.

"Jibril ina ganin kamar ba zasu amshi tayin ba?" Shiru yayi kafin ya sunkuyar da kan shi cikin ladabi da biyayya.

"Hamma Shehu, babu inda ba zasu so tayin ka ba, sabida Fulani Aminatu tana da nagarta, kuma kai ma nagartaccen mutum me, sannan idan yadda ka hango ne, Sarki Bello ya dace da Fulani Aminatu, kuma idan kayi nazari a da tarihin shi yana daga cikin sarakunar gobir da suke kin tashin hankali ba laifi bane idan aka bashi tunda har aka yi nad'in sarautar babu wanda yayi yunkurin bashi mace. Haka yana nufin cewa sun gaji da bawa mazan masarautar mata ne sabida.."

Shiru yayi yana kallon kasa, gyara zama Mai martaba Sarkin Gombe ya ce.

"Babayo kana hidima da Aminatu domin Buba ne ko kawai dan ni ne?" Haƈe hannun shi yayi cikin tsannanin tsoron da tashin hankali kan shi sunkuye ya ce.

"Ina yi ne dan Fulani Amrah" d'ago kai Mai Martaba Sarkin Gombe yayi ya kura mishi ido. Sannan Babayo ya cigaba da cewa.

"Nayi mata alkawarin tsayawa Aminatu, bakwai dan Abubakar yana son ta ba, sai dai muna duba Gombe mu ne kafin mu zartar da hukunci. Sannan idan na duba ita kanta kafin ta san Meye soyayyar ya dace a fitar da ita daga cikin masarautan yanzun take da shekaru goma sha biyu. Daidai ta tashi a hannun mijinta. Sannan haka zai saka ta taso da soyayyar mijin ta da kuma sanin sha'anin mulki."

"Na yarda da kai, ku shirya kome yadda zai tafi" ya fada,

"Allah ya taimake ka, Ubangiji ya baka nasara Allah ya kare ka gaba salama baya salama"

Lumshe idanun shi yayi tare da jinjina kai, ba wai yana da zabin ba da auren Yar shi karama bane sai dai bai da yadda ya iya ne kawai, sannan tun lokacin da yaji ra'ayin Sarki Bello yaji a ran shi Aminatu ta dace da shi sabida tashin da tayi a cikin gidan sarautar a ware, kasancewar mahaifiyar ta kabila ce ba bafulatana bace kuma uwa Uba baiwa ce a cikin masarautar sarki ya yantatta. Sannan duk cikin masarautan tafi shiri da Babayo kasancewar shine mutum na farko da ya fara nunawa dan uwan shi dacewar ya shigo da ita cikin masarautar a matsayin kwarkwarah mana. Kuma Sarkin ya amince.

Mahaifiyar Aminatu ta kasance daga cikin bayin da aka kamo cikin ganimar yaki, kuma aka kai su shashin Fulani kilishi, maketaciyar mace mara imani, ga cin zarafin bayi kamar me.

Kasancewar Babayo yana yawan kai sako yake ganin yadda ake cikin zarafin bayin, yaso shi ya nemi Amrah, amma sai yaga koda ya nime ta, ba zata samu sauki ba a gidan shi domin shima lokacin matar shi tana da Masifar kishi. Amma idan a Kwarkwarah ne sarki zai d'aga darajar ta da kimarta. Da wannan ya bawa Dan uwan shi shawara kuma yayi na'am da shi.

Za a iya cewa table rabo ne ya tsaga bata jima da tarewa, sai ga ciki a lokacin sarki Shehu yana da mata hudu, kuma dukkansu yaran su manya.

Uwargidan Mai Martaba itace Fulani Shatu yar Sarkin Yola, sai Fulani Habibah daga masarautan kano,Hajiya kilishi daga nan yar wazirinsa ce.

(Ga masu bukatar Wata Alkaryar 300 uku me zasu iya tuntubar wannan number 08130269641)

Sai Fulani Maimuna daga daga nan cikin masarautan yar Kanwar mahaifin Sarki Shehu ce, sannan suna da yara kusan kowanni daki, babban abinda da yake faruwa su sauran matan basu kai Kilishi azababben kishi ba, domin ita baki daya gani take

itace ta dace da Mai martaba ba su ba, haka yasa kowa take ganin zata taka, su kuma sauran suka ce basu iya ji ba, kalmar nan ne da ake cewa Haushin kaza huce kan dami, shine ana kawo Amrah ta sakata a gaba dama kuma tun can haka ne ta tsani Yarinyar tun farkon kawo ta. Amrah ta sha bakar wahala a hannun kilishi.

. Haka yasa koda tazo haihuwa ita da kanta ta haihu domin Kilishi ta hana kowa shiga cikin dakin ta, koda ta haihu an ji kukan jaririya, amma ba a ji motsin uwar ba. Dan haka baiwar da take tare da ita Innayoh itace ta shiga ta ga rai yayi halin shi. Ga jaririya a gabanta. Abin tausayi haka Innayoh ta dauke jaririyar ta kaita wurin Fulani Shatu. Babu laifi ta amshi yarinyar amma ranta bai so haka ba.

Lokacin da Mai Martaba yaji labarin mutuwar Amrah, da sakon da ta bawa Babayo, yayi kuka kamar zai yi yayya anan ya shiga bincikar dalilin da ya hana Jakadiya, kasa fadar gaskiya suka yi karshe Innayoh ce ta gayawa Babayo, wanda a lokacin shine mafi kusanci da mai martaba, amma yaki amsar mulki. Domin yace a bar shi lafiya da dan uwan shi. Shi ya gayawa mai Martaba abinda ya faru, shi kuma ya rantse ko za a bar shi a duniya shi da kilishi ne ya yafe ba zai kuma zama da ita ba, wannan dalilin ya kuma haifar da tsannar Aminatu a ran Kilishi.

A hankali yarinyar ta taso babu soyayyar kowa sai ta Innayoh, domin shi kan shi Mai Martaba ya tsani yaji sunanta ko ganin ta, wanda bayan rasuwar Mahaifiyar yake mugun kaunarta. A hankali aka wayi gari baya son ko ganinta, haka yarinyar ta zama kamar yar tsakar gida. Tana da Shekara biyar suka saba da Buba dan gidan Babayo, wanda shi yana da shekaru goma sha biyar a lokacin.

Haka ya taimaka mata sosai har take jin kamar shi ne kome nata, ana cikin haka Mai Martaba suka tafi wani gari garin numan, bikin kamun kifi ana ya hadu da wani mutumin da yaga sarkin Gombe yayi ta bin tawagar shi har ya samu ganin shi.

"Allah ya taimaki mai martaba, hmm kana raye amma shukar ka tana bushewa, ko baka bukatar bishiyar tayi yabanya ne? Zanen ƙaddara tayi tawo mugama da wasu manyan manyan alamura. Faruwar wasu abubuwan zasu biyo bayan kyakyawar yanayi me ɗauke da manyan ginshikai. Masu biyu zasu kasance a danbar kowacce ƙaddara, idan har zaka daka ta tawa, domin samun alaka me karfi ka gwada mika yasashen tsiron nan da yake gidan ka, amma bari na gaya maka bai zama dole haka ya zama karshen wasu abubuwan ba, kamar haka itace tushen wasu matsololin sannan karshen wasu matsalolin. Hawaye zai ta zuba, domin share duk

wata cutar bayan kasa dole wannan tsiron na gidanka zata fitar da manyan manyan alamura. Kayi kokarin nan da shekaru bakwai masu zuwa ka gaggauta habaka yabanyar ka"

Daga haka yayi tafiyar shi, shiru suka yi daga shi har Babayo. Kafin suka kalli juna.

"Hamma kaina ya kulle" inji Babayo,

"Nima haka, Allah yayi mana jagora,amma abun da duba yanayin maganar shi domin yayi maganar cikin gaurariyar hausa ce." Inji Sarkin Gombe, shiru Babayo yayi sannan suka wuce inda zasu zauna kafin a fara bikin.

Bayan sun dawo suka samu yarinyar bata da lafiya, abin tausayi haka Uban ya wuce, kasar zuciyar shi yana jin zafin wofatar da ita da yayi, tun daga lokacin. Babayo ya mai da hankalin shi kan yarinyar, har zuwa lokacin da suka fahimci shakuwar so Buba, hankalin su ya tashi, domin bayan nan sun kuma cin karo da wani mutum a lokacin wani bikin sallah, ana bikin sallah, shima ya gaya musu haka amma sai basu dauka da gaske Ba.

Sai da aka yi karo na uku zuwa wani yaki da aka yi da wasu maguzawan dutse, da suke gaban shi garin Gombe suka sake jin irin wannan maganar, tun daga nan hankalin shi ya tashi ya shiga niman masarautan suka kasance masu kwazo da rashin tsoro, a lokacin sarki Ibrahim ya tab'a zuwa da wannan batun sarki Ibrahim ya ce mishi.

"A kullum kabilar mu suna facaka ne cikin jini, sannan mu bamu kasance masu tsoro ba,kullum kwayar jinin mu barandami ne, bamu fita niman aure dan mun san ba bamu za ayi ha taya zaka kawo yarinya me daraja cikin mu? Shin kana ganin yin haka ba zai hanata fuskarta takaba bane? Duk wani namiji a masarautan nan an hore shi da yaki ne! Dan haka ba zan maida maka Y'a bazawara ba ka kai ta wani masarautan."

"Naji abinda kace ko yaranka maza ai xaka iya nima musu auren tunda itama Yanxun take da shekara bakwai" domin lokacin shekarun ta bakwai ne, kuma Sarkin Gombe ya kagu ya dauke ta a cikin masarautan sabida yadda take Fuskar ta yawan rashin lafiya da yanayin takurawa.

Koda matan Sarki suka ji labarin ana nima mata babban gida a cikin gidajen sarautar kasar nan abin yayi musu zafi dan haka suka hasala...

Hi guys barka dai Wayyo kuka ta kira cigaba cigaba... TOH gashi nan thank you 😍

#Mai_Dambu

[3/28, 11:48 AM] UmmuHabibah❤: KꞋALLABI.....!

A tsakanin Rawuna.

EWF

Na

Mai_Dambu

https://www.wattpad.com/1201408229?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=share_published

<Babi Na Huƈu>

Soyayyar gaskiya tana faru ce a bisa wasu manyan ginshikai! Imma ƙaddara ta haƈa imma kuma lokaci ya haƈa sai dai mafi girman soyayyar gaskiya ita ce ƙaddarar da zata zo bazata

A hankali rayuwa ya cigaba da tafiya tare da fatan samun daidaito akan Al'amarin Yar shi, har tsawon kwanakin da basu kirguwa. Kwanaki sun rikide zuwa makonnin,. Da tafiya ta mike makonnin sun rikide zuwa watanin. Watannin sun juya tare da curewa wuri guda inda suka haifar da shakaru.

A cikin wannan yanayin Fulani Aminatu tana da shekaru goma sha,, gefe guda kuma Kilishi ta sakota a gaba, inda take ganin kamar ai ita da take da Yarinya mace budurwa ta dace Mai Martaba yayi magana akan ta, amma ya karkata ga Aminatu dan hakan suka hade kan su kaf matan mai martaba idan ka cire Fulani Shatu itace kawai taki shirya al'amarin su domin ta fahimci wani abun da basu fahimta ba, na

Mai Martaba yana kokarin fitar da ita ne dan halin da take fuskanta. Shi yasa bata takurawa kanta da azababben kishi akan Aminatu ba.

Sauran matan sun gama ajiye magana daya akan Fulani Aminatu, dan haka Fulani maimatu ta same Mai Martaba a babban zauren shi na hutawa. Cikin nutsuwa ya Kalle ta domin yasan matukar zata zo gaban shi da nata bukatar zata zo, dan haka ta zuba mata ido.

"Allah ya baka nasara, dama akan batun Fulani Aminatu ce,Mai Martaba kana ganin a dauki Yarinya karama a bada ita aure babu wani abu? Sannan wani masarautar ce za a bada aurenta ga Yayunta Mata Fulani Barirah da Fulani Saudatu, ga Fulani Sakinatu duk Yaran da suka fito cikin jinin sarauta ne ita kuma Yar yantacciyar baiwa ce fa"

Murmushi yayi tare da cewa.

"Bakar Saniya...

Mai fidda fararr Madara ta samar da ita taya zan iya juyawa ƙaddarar ta baya? Masarautan da za a kaita aure kiyi hakuri lokaci zai nuna mana ko ina ne" ba haka taso ba, taso taji ina ne za a kai Fulani Aminatu.

*

Tawagar Gobirawa.

Sun yi tafiyar tsawon mako uku zuwa hudu kafin suka isa garin Kano, inda suka samu kyakkyawar tarba daga Sarkin Kano, shi kuma yayi musu tanadi na musamman, inda ya bada wakilin shi tare da wasu manyan mutanen Fadar shi. Tare da rubuta wasika izuwa Sarkin Hadija, dan haka babu b'ata lokaci aka sake tadda dawakai da kayan Alfarmar tare da akwatin gwala-gwalai izuwa masarautan Gombe.

Tafiya ce wacce aka yi ta a cikin kwanaki biyu rak,Mai Martaba sarki hadeja ya basu wasu mahaya kasancewar tafiyar har da rakumai kusan guda saba'in shima kuma Mai Martaba Sarkin Hadeja ya bada wasu manyan munduwar zinari ga amarya sannan ya kuma kara wasu manyan dagatai da zasu yi rakiya har fadar Gombe.

Kafin su baro garin haɗeja, Sarki Abdullahi na Hadeja ya bada wasika ga amintattacen mahayin shi kamar yadda Sarki Muhammad na Kano yayi mishi. Ya bada wasikar a kai ga Sarkin Bauchi, tafiya ce ta tsawon kwana biyar.

Kuma a yadda aka san masarautun arewa suna da kyakkyawar hadin kai da taimakon juna, haka yasa suka marawa Masarautan Gobir bayan, domin a tarihi ya tabbatar da cewa babu masarautan da suke sa karfin jarunta da kuma yawan sadaukai. Ko yayya suka shiga yaki ba a kada su, sannan dayawan masarautun suna kokarin Niman taimakon su tare niman goyan bayan su a yaki, haka yasa dayawan mutane ke tsoron wanda zai bude baki ya ce yana da alaƙa da masarautar Gobir. Sabida karfin mulkin su. Da kuma iya sarrafa yaƙi.

Sannan sauran masarautar suna kokarin inganta zamanin lafiyar al'umma su,ba dan kome ba sai dan kar a fara yakin da za a yi asarar rayuka da duniyoyin alumma. Sannan babban abinda kunya ce ka shiga yaki baka da masu taimaka maka, masarautar Gobir ita ɗaya ke idda yaki babu mataimaki sai Allah wannan yasa kowacce masarautar ta shafawa kanta ruwan sanyi.

Baya haka haka kamar yadda sukewa Masarautar Gobir hidima itama masarautar da zasu shiga wani abu tabbas zasu iya taimakawa, wannan shine ake kira da karfin zumunci da dangantakar dake tsakanin masarautun.

Koda mahayin ya isar da sakon Sarkin Bauchi, aka fara shirin tarban bakin masarautar Gombe,. Sannan aka musu kyakyawar tanadi, kasancewar masarautar Bauchi tana cikin manyan Masarautun da Shehu Usmanu danfodiyo ya kafa da kan shi inda ya turo wakilin shi yakubun farko haka ya haifar da wani irin daidaiton tsari a garin da masarautan baki daya.

Bayan kwana shida suka iso masarautan Bauchi, kuma Alhamdulillahi sun samu irin tarban da ya dace dan dama tun fil azal mutanen Bauchi akwai karamci da amsar bakon su,. A ranar Sarkin Bauchi ya tura sakon zuwa ga sarkin ga bakin shin nan zuwa. Kuma tafiyar kwana ɗaya ce da wuni. Dan haka ya gaya musu zasu taso nan da kwana biyu.

.....

Masarautan Gombe.

Tun daga yanayin gyaran masarautan tare da kula da wasu manyan bangarorin cikin masarautan yasa kowa ya sha jinin jikin shi. Tabbas duk inda ake tsammanin za a kai Aminatu babban masarauta ce me karfin iko da mulki. Kaf masarautan babu wanda yasa inda za a aurar da Fulani Aminatu, amma Innayo ta sani, .haka Jakadiya Jebu tayi ta bugun cikin Innayo amma bata taɓa bude bakinta domin magana ba. Baya kadan a cikin masarautan.

Ana tsakiyar fadanci Mahayin barci yazo, cikin girmamawa ya isa gaban mai Martaba. Ya zube.

"Sako daga masarautan Bauchi, domin isa da bayanin jibi insha Allah baki suna nan zuwa"

"Ku bashi sulallar zinari, sannan akara mishi dawakai uku, a bashi bayi mata biyu, tukwaici ne ga sakon da ka kawo"

"Allah ya kara girma da daukaka, Ubangiji ya jibanci al'amarin ka"

"Sarki Ya amsa" sannan Mai martaba ya kalli kanin shi Babayo ya matsa kusa da shi,.ya fada mishi bakin da suke zuwa.

"Masha Allah, surukan mu na wannan masarautan mai albarka zasu taso jibi talata, zasu huta Laraba da Alhamis, ranar Juma'a Insha Allah muna fatan daurin Auren a cikin masarautan nan" inji Babayo, kafin kace kwabo Sarkin gida da Sarkin Zagi sun isa cikin gidan sun sanar baki daya hankalin kowa ya tashi daga wata masarauta ce? A cikin gidan kuwa tun da aka yi sanarwar Innayoh ta saka Fulani Aminatu a daki ta hanata fita sabida tasan zuwa kowa ya wasa wukar shi da fitinar shi dole a shirya ta, dan ma an kawo mata jike-jike Baffanta Babayo idan ba haka ba ai da yarinyar ta kad'e har buzun ta.

Tun daga ranar da aka sanar bakin Gombe na zuwa aka kara yawan tsaro aka kara yawan kulawa ba musanman, sannan shi kan shi Mai Martaba Sarkin Gombe Alhaji Shehu Usmanu, babban Addu'ar shi a fitar da Aminatu lafiya haka zai daka shi jin wata irin nutsuwa.

**

Rana bata karya kamar yadda aka sanar ranar Laraba talata da magariba, bakin Gobirawa suka iso. Sannan suka yadda zango a wajen garin gombe tare da tura bayi mata karkashin Jagorancin Jakadiya Rama. Tun kafin su iso aka shiga fadar da labarin ai bakin. Daga masarautar Gobir ne, kafin kace me labarin ya karade cikin gidan, take kowacce mace ya kama kanta da Yaran ta, tare da ganin adalcin da Mai Martaba yayi na aurar da Fulani Aminatu ga masarautan da kullum cikin shirin mutuwa yayi ya kyauta (shi fa Mahassadi kullum haka yake da zaran yaga can bai ci ba toh gaba zai ci kamar ba anan ake son sanin ina ne za a aurar da ita ba yau kuma ana ganin adalcin Mai Martaba)

_____

Hey gashi nan babu yawa. Amma da za a kara comments da Voting maybe na kara wani abu wannan labarin ba zance zai kai kwarkwarah ba amma ba mamaki suyi kunnen doki please share it

#Mai_Dambu

[3/28, 11:48 AM] UmmuHabibah□□❤: KALLABI...!

A Tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

https://www.wattpad.com/1202777502?utm_source=android&utm_medium=link&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=Mai_Dambu&wp_originator=%2FTkRLP2mVOiOibQOmSAZomlKU5lZCJrKgGsadyz5zbb1oHJQIrUZmlujwcmwOYjvR2oNox9TifPEUZMrn51misnMzQo8zFd8GVZXdYgFwL3EV0XzHOhA8qWeZfnQs9hF

<Babi Na Biyar>

EWF

```Wannan shafin gaisuwarki ce Mammyn Afreen ki more pagen da gasken gaske... Ina son COMMENTS ɗinki na musamman ne😍 Nagode```

Mai yiwuwar tafiya ce mikakkiya! Domin duk zaren azabarin da zaka kulla sai ka samu yana sarkaffe da al'amurra mabanbantan ra'ayi! Mai yiwuwa kuma gajeruwar tafiya ce me kunshe da kaddararren al'amari! Ban sani ba amma matukar alkalami na Ya bani dama ba mamaki muyi fidda asalin kalmar kamar yadda muka saba cin karo da kowacce tafiya Nagode Mabiya ƘALLABI A TSAKANIN RAWUNA...Son so daga Mai Daraja😍

A hankali labarin Auren Fulani Aminatu ya zama mafi girman labarin da ta wanzu cikin masarautan da kewayar ta, ya kasance ko Innayo ce ta gfta gulmarta ake da ya feccenta. Kasancewar Innayoh ba karamar mace bace domin akalla tana shirin dosar shekaru Talatin. Amma a kasancewar ta baiwa mafi kusanci ga Fulani Aminatu dayawan mutane suke kiranta da Jakadiyar alkhairi. Musamman ma bayi yan uwan ta, domin ta kai kololuwar sanin Darajar kanta da kimarta.

Mace ce da ta fahimci abinda take, kuma su din can bayi ne na amana, wanda tarihi ya nuna tun da aka kafa masarautan zuri'arta take cikin masarautan kuma suke aikin Bauta, gashi ana hasashen Mai Martaba Sarkin Gombe zai barta da Fulani Aminatu. Kasancewar kamar Uwa ce a wurin Aminatu.

Tana zaune Jakadiya Bimbi tazo cikin tsananin son jin wani abu daga Innayoh ta ce mata.

"Jakadiyar alkhairi, wai da gaske uwar dakin ki. Sarkin Gobir zaa aura mata?"

Murmushi tayi sannan ta mike, bayan ta tattara zaren da take yin adon fure a jikin farin mayafin siliki, wata yadi ce da ake zuba da shi daga nahiyar gabas. Mai tsantsi da yauki, sannan yana wani irin daukar idanu kamar karanmiski, sai zaren audigar da take kadi da shi, wanda idan ta cire y'ay'an audigar take zama yayi kadin zaren. A hankali ta karkade mayafin sannan ta kalli Jakadiya ta ce Mata.

"Jakadiya kenan, ai idan ba aji mutuwar sarki a bakin bafade ba, ai ba za aji a bakin wawa." Tana gama fadar haka ta juya tana bin bayan Innayoh da harara, har ta kusan kulewa ta ce mata.

"Mai Martaba yana niman ki"
```

"Toh" daga haka bata kuma juyawa ga Jakadiya ba, domin matukar ta juya gare ta, zata iya magana maganar kuma da zata yi bata son ya zama kamar fidda amo ne daga danyen karfe.

Tana shiga ta samu Fulani Aminatu, dauke da dan zomonta, a duniya Fulani tana masifar kaunar dan zomon ta da ta saka mishi dan dalago, wanda Hamma Buba ya bata shi kafin ya tafi sokoto karatu. Dan duk abinda ake Buba bai sani ba.

"Innayoh" ta kira sunanta a wani irin shagwababben murya. Kafin ta cigaba da cewa.

"Dan dalago yaki cin kome" yadda tai maganar gwanin ban sha'awa ce, domin irin Yaran nan ne da matukar suka samu gata da kulawa za ayi tabararrun yara ne masu cike da hutu.

"Toh ranki shi dade, ya zanyi da dan dalago tunda yaki cin kome, ba mamaki azumi yake?" Innayoh ta fada mata haka, d'ago kai tayi tana kallon Innayoh kafin ta sunkuyar da kanta ta ce.

"Innayoh!"

"Na'am ranki shi dade, kiyi hakuri mai martaba yana kirana, idan na dawo xan saka dan dalago ya ci abinci ko kuma yau na saka Sarkin gida ya yanka mana dan kai da kunnuwa"

"A'a Innayo kar ya yanka min abuna, zai tashi" ta fada kamar zata yi kuka, fita Innayoh tayi da sauri ta nufi babban shashi, da sallama ta shiga tana me zubewa akan gwiwar ta.

"Allah ya baka nasara, Allah ya baka lafiya! Allah ya tsare ka da tsarin shi Uban Aminatu Uban Sakina." Murmushi mai Martaba yayi, Sarkin Fada yana cewa.

"Mai Martaba ya amsa Jakadiyar Alkhairi, Mai martaba ya kuma amsawa Uwa ga Fulani Aminatu"

Jibril ne ya gaya Zama wato Babayo, ya fara magana cikin dattako.

"Innayoh, Mutanen Aminatu sun iso,za a daura auren Ranar Juma'a, gobe kuma bamu sani ba ko zaku yi wani abin da ya shafi al'ada irin taku ta mata. Akwai sako daga masarautan elkaname wato masarautar borno na turare. Anan cikin gida

kuma Balkisu ta gaya min wai ana wanka da madara da wasu al'adu, gobe insha Allah zata zo tare da Fulani Shatu zaku tsaya akan al'amarin Aminatu."

"Insha Allah zan tsayar da hankali na da nutsuwa ta akan kome ba Fulani Aminatu" ta fada kanta a sunkuye.

Gyara zama yayi tare da cewa.

"Ban sani ba ko akwai yan dabarbarunku na mata, ki samu Fulani Shatu zata miki karin bayani"

"Inshallah zan same ta Yarimar gambawa" jinjina kai yayi,sannan suka sallame ta, bata koma shashin su ba, sai ta wuce cikin gida anan ta samu ana ta aiki kamar yau ne bikin. Saukewa da daurawa na manyan tukwane. Jakadiya ta tsaya akan kome kamar me, wuce su tai sabida yadda bayi suke kaunarta duk inda ta wuce mika mata gaisuwa ake. Har ta isa shashin Fulani Shatu, tun daga bakin kofar tayi karo da Kilishi. Cikin girmama ta zube tana gaishe ta.

"Rike gaisuwarki Innayoh, ai yanzu tsakanina da ku sai Alkhairin tunda Naji mai Martaba yar lelen shi a takaba zata kere"

Murmushi Innayoh tayi bata ce kome ba, daga can dakin Fulani Shatu ta ce.

Hmm Kilishi kenan, dan tsakon da uwar shi ta kasa ai Allah ke ci da abin shi, ai Aminatu ta zama kainuwa. Idan ana faɗin mai rabon ganin badi toh ko da jinjibi Aminatu ta ketare iyakar kowa"

Dariya Kilishi tayi sannan ta ce.

"Zuciyar mutum birnin sa, ai ba sabon abu bane carar zakara da tsakiyar rana, sai dai abid'a Sa'a da tagomashin alkhairi."

"Sa kai yafi bauta ciwo, wani da barci wani da munshari. Toh bari mu ga waye me sa'a a tafiyar da babu guziri" inji Fulani Shatu.

"Ina niman tsari ga kukan Jaki, ai a nan nake da iko a can kuwa zaman takaba ya isa haka" tana fadar haka ta juya zata bar wurin. Fulani Aminatu ta ce.

"Da alamu dai tsayuwa bata karewa me shirin gyaran wata ba, bari mu jira muji ra bakin ki" a fusace ta juya tana kallon Fulani Shatu, kafin tayi kwafa. Kallon Innayoh Fulani Shatu tayi sannan ta ce mata.

"Ki dauka naji dadi da mai Martaba ya amshi bukata na, na barin ki a wurin Aminatu. Domin ba zata yi maraicin Uwa ba, ke din kamar wata Alkaryar ce a gare ta. Ki nuna mata yadda ake magana da yadda ake mu'amala da kowa. Kʼarki sake ta zama matattarar sharan kowa ki nuna mata babu Maraya sai rago, ki tsawatar mata, ki nuna mata kuskuren abu. Yarinya ce karki ce zaki barta tayi wasa kamar yadda take so, nan da shekara daya ba mamaki ta fara neman zama mace, domin idan ta samu kulawa kashin girma ne da ita. Kʼarki manta mareniya ce, Gwargwadon abinda kika bata gwargwadon yadda zata kula da kanta da ahalinta. Masarautan da zata shiga babban masarauta ce me ɗauke da manyan alamura ban sani ba ko zata iya dauka bazata iya dauka ba, amma na had'aki da Allah ki nusar da ita abinda ya da da domin da shi zamu yi alfaharin mu basu Y'a. Kʼarki sake abin kunya ya dawo Masarautan nan domin zai fi kyau a ci mu da yaki sama da a wayi gari masarautar mu tana fuskarta barazana da tsangwama sabida kuskuren wasu mun."

Mika mata kayan tayi tana gaya mata yadda zata yi amfani da shi, da ku taimakawa Aminatu. Sannan ta ce mata.

"Akwai baki a cikin gidan nan ba mamaki zasu iya zuwa domin neman ganin Aminatu wannan hurumin ki ne a ganta yadda ya dace hurimin ku ne ki barta yadda zasu tafi da kowa, amma ki sani muna da kyakkyawan yakinin cewa ke mutum ce guda ba bari ba, Aminatu tana hannun Allah tana hannun ki duk abinda ya dawo ke ce me mafi girman laifi."

Gyada kai Innayoh tayi, a yau wani nauyin ne ua kuma hawa kanta sama da koda yaushe, kuma a tsarin sarakuna babu abinda suke gudu kamar abin kunya basu kaunar su ji an shi a cikin masarautan su. Ga kuma Aminatu da kowa yasan yadda ta taso a cikin matsue da tsangwama ya isa ya karya zuciyar Innayoh.

Haka tayi ta godiya sannan ta fita daga shashin ta nufi nasu, koda ta isa shigar da Aminatu kewaye tayi ta ajiye ta tana faɗin.

"Kiyi shiru bari na Miki wanka" ta fada a hankali, fita tayi ta haɗa ruwan zafi sannan ta kawo madaran turare da Kwababben sabulu da lalle ta shiga wanke Aminatu da shi, tana gurje mata jiki.

Fulani Aminatu fara ce kyakyawar gaske bata dauko kalar fatar mahaifiyar ta ba, sai ta dauko na Baban ta, sannan yanayin kyanta da jikinta na Mahaifiyar ce. Haka yayi saka mutanen gidan tsanarta domin itama Uwarta sabida kyanta ya kara rura wutar kishinta, a wurin Kilishi da sauran matan, sai da ta mata wanka sosai sannan ta fito da ita zuwa dakin su, ta shirya ya tsaf kafin ta shafe mata jiki da turare. Bata gama kimtsa ta ba, aka musu sallama daga bakin kofar shashin su....

_____

Ayi hakuri ban gama ba idan na gama zaku ji ni insha Allah a kai kai... Nagode sosai da jirana da kuke

#Mai_Dambu

[3/28, 11:48 AM] UmmuHabibah□□❤: KꞋALLABI...!

A Tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

<Babi Na Shida>

https://www.wattpad.com/1204063012?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=share_published

Wannan pagen gaisuwar taki ce Momyn noor Nagode kwarai da gaske 😍

A dan rude suka kalli kofar dakin, babban mayafi ta rufawa Fulani Aminatu. Jakadiya Jebu ce da wasu manyan bayi mata suka shigo cikin dakin, dauke da manyan manyan tasa na damamiyar lalle da yaji turare. Kallon su Innayoh tayi kafin ta sake murmushi ta ce musu.

"Daga ina haka?" Wani irin kallo Jakadiyar tayi mata sannan ta ce mata.

"Ana babbakun giwa wake na zomo, Malama bamu hanya mu wuce, Fulani Aminatu zo ki cire kayan ki za a miki wanka da.."

Bata kai aya ba Innayoh ta ce mata.

"Haba ai ko min saurain unguwar zoma ta jira haihu ko? Ki mai da shi an rigada an gama bamu bukatar na kowa sai na Allah" dariya takaici Jakadiya tayi kafin ta ce mata.

"Kina wasa da ni ko?"

"Jebu ke kudi tara ta ce da zan yi wasa da ke? Ko ke Kanwar kakata ta ce da zan dara dake? Ga hanya nan. Kika sake wani abu ya same ta toh wallahi da baikon Sarkin Gobir akan ta ki jinjina girman rundunar mayakan su mana" murmushi tai sannan ta koma gefe ta tsaya.

"Me furcin ki yake nufi?" Inji Jakadiya Jebu, murmushi Innayoh tayi sannan ta nuna mata hanya.

"Kowa ya ci tuwo dani hmm miya yasha. Ni jakar kaza ce sai na shiga sauran kajin suke shi Innayoh inda rai da rabo zaki biya bashin da kika ci" inji Jakadiya,

Dariya Innayoh tayi sannan ta ce mata.

"Haba? Gaske toh ai kafin ayi ɗaran akayi kwanɗi, dan haka ki ajiye a hannun ki wata rana ba mamaki Masha ruwa magirbi" a fusace suka fita da kayan. Murmushi Innayoh tayi sannan ta cigaba da shirya Fulani Aminatu..

**

Masarautar Gobir.

Ana cikin fadanci sunkuyar da kai Shamaki yayi sannan ya ce.

"Allah ya baka nasara, ya kuma taimaka dirken gobir" jinjina kai Sarki Bello yayi yana sauraron Shamaki dan yasan akwai magana a bakin shi.

"Sarki ya amsawa shamaki" inji Sarkin Fada, cikin wani irin shakka da abinda zai fito bakin shi Shamaki ya ce.

"Allah ya huci zuciyar Barden Gobir" "Sarki ya Amsawa Shamaki ya fadi abinda yake bakin shi" Sarkin Fada ya kuma faɗa, ganin Shamaki na gumi yasa Sarki Bello kara jinjina abinda yake son fada ba karamin abu ba ne. Caraf Sarkin Zagi ya fara magana.

"Allah ya baka nasara da nisan kwana, Shamaki ya kasa magana ai abinda yake son fada ba kome bane yaji rad'e rad'en da yake yawo a cikin masarautar nan ne akan Sarkin Gombe zai baka auren Yar shi ne dan ya fidda fulanin da suke cikin masarautan nan" ya fada yana muxurai. Dama shi sarkin Zagi an tanade shi domin sake kowacce irin magana da tayiwa kowa nauyi toh shi ko a gaban waye zai fade ta sai dai idan Sarkin ba adali bane yasaka a zage sarkin Zagi.

Shiru fadar yayi kowa yana jiran aji me Sarki Bello zai ce. Har ya mike ya zai bar fadar aka shiga cewa.

"Gyara kintsi mai martaba zai tashi" a hankali ya mike ya bar fadar, bin bayan shi da ido Shamaki yayi yana sauke ajiyar zuciya, domin abin da bai zata bane. Kallon Sarkin Zagi yayi tare da mai da hankalin shi kan kujerar da Sarki Bello ya mike.

"Barka da arziki" Chiroma ya fadawa Shamaki, girgiza kai yayi.

"Kana tsammani da Iro ne tuni ba a sauke min rawani na ba" murmushi yayi shima ya bar fadar yana dariyar Shamaki.

Haka dayawan dattawan fadar suke mishi barka da arziki, domin kuwa ta tsallake rijiya da baya.

--

A can turakar Sarki Bello, zama tayi yana cire kayan shi, Sarkin gida yana bakin kofar shiga.

A yau yana jin tsohuwar al'adar shi tana kuma yawo a ranshi. Gyaran murya yayi Sarkin gida ya shigo tare da zubewa kasa.

"Tashi bana son kana min haka." Tashi yayi ya zauna yana murmushi.

"Allah ya baka nasara." Kallon juna suka yi kuma suka sake murmushi lokaci guda.

"Ina son shiga dawa" ya fada yana kishingida, a saman gadon shi. Gyara zama sarkin gida yayi yana faɗin.

" Ba dai da rana nan ba? Wani ya bata maka rai ne?" Yayi mishi tambaya biyu lokaci guda, sai kuma ya gyara zama sannan ya cigaba da ce mishi.

"Tsohuwar al'adar ka ko? Amma me zai hana kayi rubutu, ko kuma kayi barci yadda suka zama al'adar ka"

Murmushi yayi yana faɗin,

"Maza a shirya min baka" mikewa Sarkin gida yayi ya fara kokarin fita.

"Karka manta har da kai a tafiyar" juyawa yayi cikin girmamawa ya gyada kai.

Wato Sarki Bello yana da wasu al'adu guda uku, da kowa a cikin Masarautar yake kokarin kiyayye shi. Al'adar shi ta farko ita ce farauta, duk wani fatar dabba daji da aka kawa da ita a cikin masarautan Sarki Bello ya kamo ta, kuma shi daya, tun yana Yaro yake fita dawa. Al'ada ta biyu ba kome bane facce rubutu, Sarki Bello ya kasance hazikin marubuci da yayi shura a nahiyar da babu irin shi, idan wannan dabi'ar ta motsa mishi wanda jama'ar masarautar suke mishi lakabi da al'adun, toh kafin ya zama Sarkin rikon kwarya yana iya zama yayi kwanaki yana rubutu ko kukan tsuntsayen ba a son su gifta ta inda yake sabida yana bawa ƙwaƙwalwar shi damar nazari da rubutu, kuma yana rubutun ne da ajami.

Sai al'ada ta uku, duk ranar Laraba baya zuwa fada ba dan kome ba sai yana ware wannan kwana ɗaya yayi barci da wasu abubuwan da suka shafi rayuwar shi, Allah ya zubawa Sarki Bello fasahar magana domin matukar zai bude baki yayi magana Insha Allah sai ya sauke hankalin mutane, wannan halin na shi yasa dayawa talakawa suka yi na'am da shi a matsayin sarkin rikon kwarya.

Yan mata dayawa suna kaunar Sarki Bello, tun kafin ya zama sarki Ubangiji ya saka mishi farin jinin yan mata, dan ma idan zai shiga cikin gari ko wani wurin yana yawan rufe fuska shi da rawani, sabida kambun idanu.

Shi da Sarkin Gida Aminai ne na kud da kud, tare suke samartakar su. Wanda sunan shi Jafar, duk da wannan yanayin Sarki Bello bai tab'a zuwa yaki ba, domin

yasha fada shi matukar zai samu damar da kowa yake samu toh shi ba zai yi yaki ba, yakan fada cewa.

“Matukar takobi ba zata sauya al'umma ba toh tabbas alkalami zata iya sauya su” wannan maganar ta isa har kunnen mahaifin su tun yana raye, yayi baƙin ciki sosai da ya haifi dan da bai damu da yaki ko zubda jini ba. Koda mahaifin su ya kira shi a irin baiwar da Allah yayi mishi yayiwa mahaifin su magana irin ta hankali sarki Jatau ya kwana da maganar Bello toh ya za ayi su yaki kamar a jinin su yake gudan jinin su duk digon barandami ne. Yaki da nasara suka sani babu ruwan su akan kome zasu yi yaki.

Lokacin da Sarki Jatau ya tashi yaki, aka kashe shi kafin ya mutu sai da ya tuna da kalaman Bello.

“Baba karka manta yakin da za aka tafi bai zama dole ka dawo ba, idan kayi hakuri kuka janye yakin Alummomin da suke iyaka da masarautar mu zasu kwana cikin salama. Idan ka duba yakin nan bai sama dole ayi nasara ba ka duba lamarina" sai da ya gayawa Sarkin yaki abinda Bello ya gaya mishi. Haka lokacin da Ibrahim zai tafi sai da ya Bello ya nusar da shi illar yake yaƙen da suke amma ina su din wasu irin halitta ne masu matukar taurin kai da taurin zuciya, kuma duk abinda suka daka a gaba sai sun same shi.

Wannan kenan a cikin al'adar Sarki Bello,

Shiryawa yayi cikin kayan farauta, sannan ya dauki mayafi ya rufa, daidai shashin sa bayi ne mata da kunyagi suka taru, suna gud'a daidai fitowar shi, gud'a suke har ya fito ya haura saman doki, Sarkin gida ya kama dokin shi ya fara ja, amshi linzamin yayi ya kad'a kan dokin shima da sauri Sarkin gida ya haura na shi suka fita da gudu. Da sauri sarkin gida ya cimma shi. Sannan ya mika mishi jimammiyar fatar barewa. Wanda aka yi rubutu a ajami a cikin shi.

Ka gaya mishi ya kula

Kumshe Idanu yayi masu wani irin sheki kamar an diga musu mai a cikin su, ya kuma zaburar dokin shi suka nausa dawa. Tun daga nesa yake shakar kamshin ana bin su, dan haka ya kalli sarkin gida, yayi mishi alamar su kara gudu, haka suka kara gudu sosai wanda har suka b'acewa masu bibiyar su, ta wannan ɓangaren gare abokai guda biyu sun yi zarra domin sun iya sukwa akan dawakai.

Bayan sun shiga cikin dajin, suka daure dawakan su a kasar wata bushiyar loko, suka shiga cikin dajin sai da ya daure jejen sosai yadda babu wanda ya isa ya shiga

musu. Tafiya suke amma babu wanda yayiwa dan uwan sa magana sai da suka isa gaban wata korama, wacce take bawa rafin masarautan ruwa.

"Allah ya baka nasara akwai abinda yake damun ka" murmushi yayi sannan ya kalli gaban su inda wata gada take shan ruwa.

"Kaga gada" sarkin gida ya kuma Magana, saka hannu yayi a bakin shi, har tasha ruwa zata wuce sai kuma ta kalle, dan haka ta rab'a gefen su zata wuce.

"Baka yi..." Dake hannun shi Sarki Bello yayi. Shiru yayi har ta wuce juyawa yayi ya ga ta b'ace.

"Ba gadar da kasaba gani ba bace." Kallon shi yayi kafin ya ce mishi.

"Kamar ya? Ban gane ba?"

"Ita din yar aike ce, ta riga mu shigowa dajin rufe mata kofar da muka yi kasa ba zata iya isa waje har ta bada labari ba!" Inji Sarki Bello,

" Na razana!" Inji Sarkin gida,haka suka ci-gaba da farauta, har suka isa wani kurmi.

"Ranka ya dade ba a shigowa nan domin akwai wata zakanyar da take farautar." Bai kai aya ba suka ji gurnanin zakin, kallon Sarkin gida yayi. A hankali ya zaro wani guru (am so sorry da wasu abubuwan da zaku ji ko zaku yi karo da shi labarin it's was about 200 yrs ago ne wato kamar a ce ancient ko? Toh akwai gurru akwai laya akwai baka, akwai maita akwai kambun idanu, akwai baiwa irin ta da kamar a ce supernatural ban san yadda zan muku bayani ba amma akwai tsohuwar al'adar can da jimawa ayi hakuri da abinda xa a gani kafin musulunci ta shiga cikin al'umma ne labarin amma zamu kiyayye abinda zai tab'a kimar al'adun Hausawa da ita kanta hausar Nagode)

Sarakuna da Yaran su a wannan lokacin, suna shirya kan su ne musamman Gobirawa wanda kaf tarihi an san su da zallar jarumta da iya yaki, yana daukar gurrun ta saka a cikin Aljuhun rigar sarkin gida,. Cikin wani irin zafin nama, ya falla da gudu aikuwa zakanyar tana najin haka ta fito da gudu ta rufa mishi, sai da yayi gudun fitar hankali suna ratsa kwazazxabai, ya samu damar zaro kibiyar shi. Kafin ta cimma shi ya zabga mata harbin da ya ratsa cinyar ta ya maka ta sa kasa, bata iya tashi ba komawa tayi ta kwanta, zuwa yayi kanta ya tsaya, sannan ya ciro takunkumi ya daure ta da shi,. Sai lokacin ya lura da ashe namiji ne.

Shafa gurrun sa yayi tare da dafata, sai gashi a wurin da ya ajiye Sarkin gida.

"An gama farautar yau! Taya kasan da zakanyar?" Sarkin gida ya tambaye shi.

"Amma ranka shi dade kaji dalilin da yasa Sarkin Gombe baka Yar shi!" Da wutsiyar ido ya kalli sarkin gida, sannan ya saka hannu a bakin shi yana girgiza kai.

"A bakin mutane!"

**

Masarautan Gombe.

Shiru Kilishi tayi tana kallon Jakadiya Jebu, kafin ta ce mata.

"A nimo min amintattun bayin masarautan gobir, su zasu min wannan aikin"

"An gama uwa mabada mama koda uba nai sarki ne" inji Jakadiya, da sauri ta fita ta nime wasu bayin biyu suka tafi har inda aka saukar da baki mata aka tawo da wasu mata biyu. Suka isa dakin Kilishi.

A yau Alhamis aka saka Fulani Aminatu a lalle, cikin wani kyakkyawan shiga ta jajjayen karanmiski, wanda ya fidda hakikanin kyanta da kankantar shekarunta. Dake Fulani suma suna da al'adun aure, an yi mata babu iyaka.

Washi gari juma'a bayan sallah asuba aka daura auren Fulani Aminatu da Muhammad Bello Sarkin Gobir, inda aka bada sadaki mafi girma da daraja...

---

*Hi ya kuke! Alhamdulillahi na gama rabin aikina Insha Allah zaku na jina duk bayan kwana ɗaya! Yau nayi Insha Allah dai friday ku amshi wannan yanayin da farin ciki 😍 ko ya haduwar Fulani da Sarki zai kasance 😍 Nagode sosai keep yourself in this journey ba zaku yi danasanin karantawa ba gaba kadan zaku fi kowa bukatar shi ma kamar yadda muka tafi a Bororoji *

#Mai_Dambu

[3/28, 11:48 AM] UmmuHabibah❤: https://youtu.be/0_JKoaXCVOc

KꞋALLABI...!

A tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

<Babi Na Bakwai>

Godiya da fatan alkhairi son so daga Mai Daraja😍

Barka da Juma'a#

Masarautar Gobir.

Mai Martaba Sarki Bello, yana tsaye a saman masarautan, wurin an ware shi ne domin shan iskar sarki da iyalin shi ko kuma baiwar da ya yantatta da zama sad'akar shi. Wurin kamar tsarin gidan sama ne amma ba gidan sama bane anyi yar rumfa me ɗauke da wasu kyawawan mayafai, wanda ya kara kawata wurin. Asalin kasar wurin an shimfida mishi wasu irin kilisai tare da wasu irin dardumar yar gata. Sannan an saka wasu matasai tare da wasu abubuwan kamar katifa da ya sha adon sarakunan kasar Hausa.

Sarki Bello zaune cikin wani irin nishadi da nutsuwa, yana kallon tafin hannun shi. Sanye yake da shigar sarakunar dake ranar yau ya kasance juma'a. Murmushi yayi yana kallon tsuntsayen hasbiya da suke dan dandamalin da aka jera wasu kyawawan tukwanen shuka da furanni masu kamshi me dad'i.

A lissafin da aka yi dangane da daurin auren shi yau aka daura, daddin daddawa yanayin Nahiyar ya tabbatar da haka, duk da basu samu labarin daga can ba, dan tafiya ce ta tsawon kwanaki kafin a iso ga raƙumi kenan, ga hangarman doki zai iya kwashe satittka kafin ya iso masarautar. A hankali ya cire rawanin kansa yana kara sauraron tamburan da ake bugawa a masarautan baki ɗaya. Uwa Uba ga tashin algaitu da kakaki, haka kawai yake jin tsigar jikin shi yana mikewa wanda ya haifar da tashin gargasar jikin shi. A hankali ya mike yana me isa yar dandamalin yana kallon yadda ake shiga da fita a cikin harabar masarautan. Tsintar kan shi yayi da nad'e hannu a kirjin shi yana jin wani irin daidaiton nutsuwa na shigar shi. Yana jin wani irin kemawa da kamala na shigar shi na asalin igiyar aure da ya hau kan shi. A

hankali ya juya cikin natsuwa ya zura kafar shi a saman kyakyawar takalmin fatar da yake kofar mashigar wurin shan iskar.

Juyawa yayi ya hango rawanin shi, murmushi ya sake sannan ya koma ya dauki rawanin ya daura akan shi, yana me juyawa a sanyayye cikin taku irin na asalin sadaukan maza, irin mazajen da suka san me ake kira da jarumta. Wanda galibi basu damu da nunawa duniya su din wasu bane , sai dai aikin su ya nuna haka.

Tunda ya fara saukowa Sarkin gida ya tare shi da bayanai.

"A bisa yakini da lissafi ana tabbatar da an daura auren mai martaba da Fulani Aminatu, sannan ana saka ran nan da makwani biyu sun iso cikin birnin nan. Sarakunan da suke karkashin jagorancin masarautan nan sun kawo maka ziyara. Akwai kyakkyawar liyafar da aka shirya domin tayaka murna.

Sannan manyan manyan Fadar ka sun baka hutun wata guda domin amarci."

Ban san yadda zan muku bayanin irin yanayin da mai martaba sarki Bello yake ciki ba amma yana cikin yanayin nan ne da Bature ke kiran shi(romantic moment) shi kan shi murmushin da bai san yanayi ba yake sakewa. Idan da zaka kalli kwayar idanun shi zaka fahimci yana cikin wata mahaukaciyar yanayi ne me matukar daukar hankali. Sai da suka yi tafiya me tsawo har zuwa shashin sa sannan ya tsaya cak yana kallon kofar shashin da aka mallakawa Fulani Aminatu. Kallon Sarkin gida yayi ya nufi kofar, da sauri ya bude mishi ƙatuwar zauren da aka kawata shi da kome kalar zinari da ratsi-ratsin Ja. Sannan an kawata zaurenta (wato a can baya ana kiran Falo da suna Zaure zamu dauki haka a matsayin zauren kawai ba)

A cikin zauren kuwa shirya wasu irin mayafai masu matukar kyau da ɗaukar hankali, wasu shara-shara wanda zai zama hijabi ga mazan da zasu tawo ga Fulani ba sai sun isa cikin zauren ba, daga can zaka iya magana. Kuma zata baka amsa sarki Bello kawai yake da hurimin wuce mayafan kuma tsarin shine haka yace baya son Fulani tayi cuɗanya ga wasu mazan musamman bayi ma.

"Allah ya baka nasara,.tsarin yayi ta gabas maso arewa nan turakar Fulan..." Sarkin gida bai idda maganar shi ba, yaji sautin muryan Mai Martaba ya ce mishi.

"Shiiii!" Sannan ya cigaba da wuce mayafan, bayan ya dakatar da Sarkin Gida ga bin bayan shi.

Yana zuwa ya bude kofar dakin da aka ware domin ita Fulanin. Murmushi yayi sannan ya fito izuwa wurin Sarkin gida. Suka fita har zuwa shashin sa, ya zauna kallon Sarkin gida yayi sannan ya shiga cire rawanin shi.

"Jafar kai da waye kuka yi aikin?" Cikin girmamawa Sarkin gida ya ce mishi.

"Allah ya baka nasara, da nisan kwana ni da wasu bayi biyar ne" saka hannu yayi a kunnen shi yana me kishingida a inda ya zauna. Jijjiga kunnen shi yayi.

"An gama ranka shi dade, an cika umarni."

Mikewa Sarkin gida yayi da sauri ya fita daga cikin shashin Mai Martaba, ya nufi Bai wato gidan bayi. Yana shiga ya kira bayin nan maza da suka yi aiki ya musu magana, cikin matukar farin ciki suka zube a gaban shi suna masu godiya da sakawa auren albarka. Anan suka tattara iyalan su, suka bar masarautan bayan Sarkin gida ya basu dawakai da guziri masu yawa ya ce.

"Sarki Bello yayi muku afuwa, kuma ya baku damar ku tafi kuyi rawa inda kuke so, amma kar ya kuma ganin fuskar ku a cikin masarautan wannan shine daidaiton adalcin da ya muku"

"Mun gode kuma mun yi na'am da wannan halin girman da yayi mana, a isar mana da sakon godiya, Allah ya albarkaci rayuwar shi da Fulani Aminatu." Sannan suka bar masarautan ta kofar Bai, wato kofar bayi nan.

Sarki Bello ya dauki matakin haka ne, domin wasu dalilai irin ta gidan sarautar su, amma idan da lokaci yayi haka zai bayyana kan shi.

**

Masarautan Gombe.

Tun kafin a daura auren, aka turo kiran Innayoh wacce ta farka tun karfe biyu na asuba tana shirya kayan Fulani Aminatu, da sauri ta fita bayan ta rufe kofar sosai ta

nufi shashin Mai Martaba Sarkin Gombe. A bakin kofar shi ta same shi yana tsaye shi da Babayo.

"Allah ya kara maka lafiya da nisan kwana, barka da dare"

"Innayoh ba zan gaji da baki amanar Aminatu ba, idan wani abun farin ciki ya faru kece zan yi alfahari dake, kuma kamar muradin mahaifiyar ta ce, idan akasin haka ya faru kamar faduwar ki ce, ga Aminatu nan tarbiyyar ki ce nan da wasu sa'o'in za a daura auren ta da Sarkin Gobir, kuma an shirya kome na tafiyar ku, kayan ta ma sun yi gaba. Kar naji kar na gani, idan ƙaddara ta fado bata da inda ya wuce masarautar da yafi wannan."

Wani irin kwalla ne ya cikawa Innayoh idanun ta, iya soyayyar da zai nunawa yar shi ita ce koda wani abu zai biyo baya bata da inda ya wuce nan lallai Fulani Aminatu tayi dacen Uba na gari.

"Insha Allah babu abinda zai faru da zai kawo ta ma sai alkhairi"

"Maza ki shirya ta akan lokaci ana daura auren zaku dauki hanya" ya fada tare da barin wurin, sai da ta daina hango hasken fitilar shi, sannan ta mike ta koma shashin Fulani Aminatu. Suka ci-gaba da shirin su.

Kamar yadda ka tsara haka ce ta faru, ana daura auren da manyan manyan akwatin gwala-gwalai da suturanta masu yawan gaske daga masarautan elkaname aka kawo mata, sannan aka akwai wanda aka Kawo mata daya masarautan gobir na auren tare da manyan akwatin nan zinarai. Na auren ta wanda lokacin da aka shigar da shi cikin gida abinda matan mai Martaba suka fada shine.

"Amma dai sayar da Fulani Aminatu mai Martaba yayi ko? Wannan in ba sayar da ita yayi ba ina za a kai wannan kayan me mugun yawan gaske sai kace ita ce tafi kowa."

Sun manta akan ta aka ya fara aurar da Y'a, kuma ya fara bikin shi na farko a cikin masarautan, dan haka ya saka aka daura duk kayan a kai mata kayan ta tayi ta sakawa tana ado dashi. Sannan kafin su bar masarautan yayiwa Innayoh Alkhairi me tarin yawa, aka bata bayi kowa daki sai da suka bata bayi, lokacin da aka kawo na dakin Kilishi kiri kiri Innayoh taki amsar su, da sauri Jakadiya Jebu ta koma tana me gayawa Kilishi abinda Innayoh ta ce.

"Ki mai da su bama bukatar su, muna da wadatattun bayin da zasu mana kome." Lumshe jajjayen idanunta Kilishi tayi ta mike tare da gyara mayafin ta, ta fito harabar masarautan. Tana fitowa bata tsaya ba ta tsinke Innayoh da mari wacce take rike da Fulani Aminatu zata shiga leken dokin da aka kawo mata daga masarautan Yola.

"Tasss" sautin marin ya karade harabar masarautan. Rike hannun Innayoh Aminatu tayi cikin tsananin tsoro tare da kifa kanta a kadadar Innayoh.

"Fulani kilishi a iya yanzun baki da iko dani ko Aminatu, sabida muna ƙarƙashin mulkin masarautan Gobir ce, yin haka kamar lakatar rigima ce, dan haka ki mai da bayin ki bama bukata. Idan wani abu ya faru ba iya su zai tab'a ba, hatta ke da kike da mafarkin goben ki. Idan kuma aka samu akasin haka matar sarki ce fa" ta fada maganar cikin wani irin dakiya. Sauke hannu Kilishi tayi tana kallon ta.

Tabbas tsoro ya danne kashin bayanta, ba zata iya aikata wani abu ba, dan haka ta juya ta bar harabar da bayin ta. Juyawa tai tana kallon Innayoh da itama ta juya tana kallon ta. Juyawa Innayoh tayi ta shiga cikin keken sabida yadda Aminatu take kara riko hannun ta. Suna shiga aka fara busa algaitu tare da barin masarautar.

Riko hannun Aminatu tai tana faɗin.

"Daga yau babu tsoro babu shakkar kowa Insha Allah kina inda za a baki kariya da kulawa. Ba zaki kuma kuka ba sai dai ki ga wasu nayi amma ke, Ya kare a wurin ki"

Yadda Innayoh take mata magana da yadda take kara nuna mata wasu abubuwan har barci ya dauke.

...

Kasa zama Kilishi tayi tana kallon bayinta, kafin ta juya tana me fita daga cikin zauren ta, ta nufi katangar da yayi iyaka ga masarautar. Zuwa waje tana hango yadda ake tafiya da Fulani Aminatu. Wani irin bakin cikin ne ya cika mata rai tana tuna abinda hare ta gaya mata.

"Matukar ta shiga masarautar Gobir ba zaki iya mata kome ba, karshe sai dai ki rasa duk wani damarki. Tauraron ta yana haduwa da na Sarkin Gobir babu wanda ya isa

ya iya samun gallaba akan su sai ƙaddara ita kuma wannan ƙaddaran zata zo ne kamar yadda guguwar yashi take tawowa daga tsakiyar sahara. Karki sake amon ki ya cigaba da kewaye ga Fulani Aminatu. Idan kuma haka ya faru tabbas da walakin goro... Domin Ubanta zai iya shirin yaki domin d'igar kwayar hawayen ta d'aya tal"

Dunkule hannun tayi tana jin wasu irin kwalla na zuba mata, tabbas ta so daukar fansa akan Yarinyar sannan abin da ya kuma d'aga mata hankali yadda hare ya ce.

"Yarinyar zata rayu cikin aminci da salama, zata yi farin ciki a farko a tsakiyar zata fuskanci rayuwarta na tsawon lokacin da ban san adadin shi ba. Kuka da kukan wasu zubda jini zai yawaita bayan shekarun rayuwar ta. Amma zata dawwama cikin farin ciki, kin ga yanayin da yake cikin ƙwaryan jinin! Kinga bakin duhun da ya ratsa hasken nan guguwar ƙaddara kenan, wannan hasken ita ce zata biyo bayan kome a wannan gefen matukar ka tunkaro ta domin cutarwa ba mamaki kanka ya sauka daga gangan jikin ka domin"

"Hare nayi farin cikin fuskar ta shekarun rayuwar ta, kuma zan yi farin ciki mara misaltawa domin wannan abin farin ciki ne ya same ni bana fatar Aminatu ta rayu cikin salama." Ta fada tana dariya.

"Tana da uwa a gefenta, ba zata yi kunci a fili ba, amma a cikin ta zata yi bakin ciki kowani mutum yana tafiya ne bisa jagorancin ƙaddaran sa, amma ba makawa zata isa inda baki zata ba akwai tafiya me nisa da zai cimma kafin wannan lokacin karki sake a samar da fitilar da zata isar da ita ga ƙaddaran ta. Yawan adawar ki yawwan nasarar ta."

Hi my beautiful mommy's and sister's Barka da Juma'a! Please a ta'ayani sharing mana i can't wait to see Sarki Bello da Fulani Aminatu ga Azumi Yazo fa ya muke ciki zan gudu nan da jibi wato Sunday idan nayi posting Insha Allah sai Bayan sallah

#Mai_Dambu

[3/28, 11:48 AM] UmmuHabibah❤: KALLABI...!

A tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

https://www.wattpad.com/1205468431?utm_source=android&utm_medium=link&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=Mai_Dambu&wp_originator=jBs9Dv1EFyPUnLBE9l6ckoD6pAsV9A8few5U6c%2F%2F9NmiM0LtJVNAr%2BHtZYxDeN5g1snT5Dl6VUKqJ54qxgM%2B8KZ75nwrIveEGvLj7JCUZz0XPfayJSn65EUggB9zTXfc

<Babi Na Takwas>

Tabbas Hare ba zai mata karya ba, zata so ganin bayan Aminatu domin da taimakon shi aka rufe bakin kowa na masarautar akan mutuwar Kwarkwarah Amrah Mahaifiyar Aminatu ba dan haka ba da yau bata raye.

Kurawa tutar Masarautar Gobir idanu tayi.

"Ina ma da Sakinatu ne a wancan matsayin ba zan yi nadama ba, haka ma sai dai ya saka mai Martaba dawo da ni matsayina. Kai ina ko ana hamaza hamata sai na ga bayanki Aminatu." Ta fada tana kara dukar jikin katangar.

A hankali ta juya haduwa Jakadiya Jebu ce a tsaye kanta a sunkuye.

"Ya?" Ta tambaye ta.

Gyada mata kai Jakadiya Jebu tayi.

"Inda ba kasa lallai nan ake gardamar kokuwa"

Gyara zaman mayafin ta tayi, sannan tayi gaba tana murmushi, Jakadiya Jebu tana take mata baya..

A hanya kuwa kamar wacce aka mintsina ta bude idanunta. Tare da tashi zubur tana raba idanun ta.

"Innayoh dan dalago na" itama Innayoh raba idanu tayi tana kallon ta.

"Mun bar shi a gida"

Sake ware idanun tayi kamar zata yi kuka ta ce.

"Haba Innayoh, me yasa zaki bar min shi bani da aboki kamar shi fa" murmushi Innayoh tayi sannan taja mayafin da yake can gefen keken sai ga kejin dan dalago har da abincin shi.

"Ahhhh dan dalago na" ta wani sauka a hankali tana zare ido. Sai wani murmushi take.

"Innayoh iya zamu ne? Har yanzu bamu isa ba?"

"Eh tafiyar ce da tazara" Innayoh ta bata amsa.

Sunyi tafiyar wuni guda suka yada zango. Kallon ta Innayoh tayi sannan ta ce mata.

"Ba kowani abinci ake saka mishi rai ba, wani ana hakura da shi ne domin kare kanka da rayuwar ka" dake an kafa musu tanti ne, fitar da dambun nama Innayoh tayi ta madara. Ta ajiye mata. A hankali ta dauka ta sha, sosai sannan ta ci namar ma. Wani goran duma Innayoh ta mika mata da ruwa a cikin sha, sannan ta ce mata.

"Kiyi hakuri, matsayin ki ya wuce shan ruwa a haka." A hankali ta kwanta a jikin Innayoh tana sauke ajiyar zuciya.

Koda aka kawo abincin da aka dafa, sun samu Fulani Aminatu tayi barci, dan haka suka tafi da shi, dan Innayoh ma tace ta koshi..

Washi gari.

Kafin a kawo abin karyawa, Innayoh ta dama mata fura da sauran madaran ta zuba zuma wadataccen ta bata tasha, koda aka kawo shima mai dawa aka yi.

Wurin Galadima aka tafi da maganar abinda Innayoh tayi jiya da kuma Yau.

"Ku kira min ita"

Tana cikin kintsa Fulani Aminatu aka sake mata sallama.

"Innayoh Galadima yana son ganinki"

"Toh gani nan tafe" kallon Fulani Aminatu tai ya rufa mata kanta da babban jam mayafi me ratsin zaren ruwan zinari.

"Yanzu zan zo, ƙarki sake wani ya kawo miki abu ki amsa kin ji nan babu wanda ya dace ki yarda da shi sama dani kin ji uwar ɗakina"

"Toh"

Sannan Innayoh ta fita, fadawa biyu da suke gadin kofar tantin ta kalle su ta ce musu.

"Karku sake wani ya wuce ku ya shiga cikin tantin"

"An gama Jakadiyar alkhairi"

Wuce su tayi ta tafi yar tantin Galadima, tana isa tayi sallama.

"Shigo Innayoh" aka mata iso a cikin tantin Galadima. Cikin girmamawa da kaskantar da kai ta shiga tantin yana kishingida ya gama karyawa. Shiru tantin ya dauka kafin Innayoh ta d'ago kai ta ce.

"Allah ya baka nasara, an ce kana nima na?"

Jinjina kai yayi kafin ya ce mata.

"Eh na samu labarin an kai abincin Fulani Aminatu amma baki amsa ba har sau biyu? Ko Meye dalilin haka?"

Gyara zama tayi tare da sunkuyar da kan ta.

"Tuba nake ranka ya dade idan nayi kuskure a wannan bigirin a hukunta ni!"

Shiru yayi kafin ya kuma cewa.

"Ina son sanin hujjar haka"

"A yayinda Duniya ta cika ta tumbatsa gamu mutane masu son kaiwa kololuwar damar da Fulani Aminatu ta samu, ai kasan zuciya bata da kashi kowa zai yi fada ne domin samun damar da ta samu" murmushi yayi sannan ya ce mata.

"Haka yana nufin baki yarda da kowa ba kenan?"

"Ko daya ba haka bane, nauyin Fulani Aminatu ya rataya a bisa kafaduna dole na kiyaye abinda zai wargaza min amanar da yake kaina" ta fada tana matse hannun ta.

"Me Innayoh take bukata a bata domin ciyar da Fulani Aminatu da hannun ta?" Ya tambaye ta.

Murmushi tayi tare da cewa.

"Allah ya baka Yawan rai duk abinda aka bawa Innayoh zata iya sarrafa shi domin Fulani Aminatu"

"Toh shi kenan, an bawa Innayoh damar dafa duk abinda Fulani Aminatu ta ke so"

"Godiya muke, Allah ya kara maka lafiya da nisan kwana" ta fada tare da barin tantin.

Tun daga wannan ranar Innayoh ke sarrafa abinda Fulani Aminatu take bukata, har suka dauki tsawon kwana ki goma sha uku, saura kwana ɗaya su shiga cikin masarautar Gobir. Daga inda suke suna hango katangar masarautar da tutar ta..

**

Masarautar Gobir

A cikin masarautar biki ake sosai, kamar yau aka daura auren shi kan shi sarki Bello ba karamin al'amari bane a wurin shi domin ya yantar da bayi babu iyaka, an fitar da abinci daga Baitul Malin masarautar an rabawa talakawa sadaka. Kowa sai albarka yake saka mishi.

Tun safe sako ya isa ga amarya da tawagar yan daurin auren nan sun dawo, amma ba zasu shigo da hasken rana ba. Sai gobe da yamma, hard'e hannun shi yayi a kirjin shi. Idanun shi akan sansanin da yake hangowa. Baki daya bai tab'a shirywa kan shi wani abu ba, balle ya ce ya ware shi a matsayin ranar auren shi. Shi kan sa auren yana jin wani irin dauki da son zaman shi magidanci ne ta fuskar sarautar shi, amma ta fuskar soyayyar da zai yi bai shirya mata kome ba.

Sai dai a lokacin da Sarkin Gombe ya bashi auren Yar shi yayi mamakin da bai ki amsar auren ba, sai ma karba da yayi da hannu bibbiyu duk da kuwa masarautu da dama sun daina basu auren Yaran su mata gudun kar su zama zawarawa. Sai dai abinda Sarkin Gombe yayi akan shi ya matukar saka shi amsar auren Fulani Aminatu. Koda kuwa bai ganta ba yana ji a ran shi zai amshi auren da dukkan zuciyar shi. Domin masu iya magana sun ce zoka ci tuwo yafi tuwon dadi. Duk da yasan itama Yarinyar da za a bashi tana da wanda take so. Amma haka bai wani dame shi ba.

Kawai abinda ya sani zata amshi aauren ne domin biyayya ga mahaifinta. Bayan nan kuma zata zo domin zama matar shi. Sai dai yasan ba mamaki itama taji tsoron zamanta bazawara. Wani irin kunci ne ya cika mishi zuciya. A hankali ya juya ga kallon sansanin su. Domin yana jin wani irin nauyi a ran shi. Idan ta shigo masarautar bata son auren shi fa? Zata iya daukar kiyayyar shi tayi ado da shi. Anya bai yi kuskuren auren ta ba? Domin yasan matukar bai mata ba, ba zai tab'a jin dadin zama da ita ba, duk da zaman shi marubuci ya sha rubuta hikayoyin kiyayya akan sarakunar da suka shude wasu sabida soyayyar da sukewa matan suke mutuwa akan matan ko matan su shayar da su guba. Hankalin shi ne yayi mugun tashi.

Kusan raba dare yayi a saman katangar, yana jin wani irin yanayi da damuwa. Har sanyin asuba ya mai da shi can shashinsa domin ba dan sanyin ba, Toh zai gwammace ya dawamma a wurin da ganin abinda zai rusa mishi farin cikin shi.

Washi gari Juma'a. Masarautar ta tashi da wani irin biki na auren shi, duk abinda ake yana can tukarar shi a kwance, bai ji a ran shi ya fito ba.

A can cikin gidan.

Ajuji mahaifiyar Yarima Yakubu ce gaban Gambo cikin tsannanin b'acin rai ta ce.

"Ban ji kina magana akan Bello ba, kina nufin ki bar kishi mulkin da ya dace a ce Yaran mu ne akai?"

Kallon Ajuji Gambo cikin sannan ta ce mata.

"Bani da hurumi akan masarautan nan ina zaune ne Sabida Zakaria, idan ta b'aci masai idan tayi kyau rijiya"

Jikin ajuji a sake ta bar shashin Gambo, domin tasan tunda ta gaya mata haka ba zata tab'a karya maganar ta ba.

...

Wuraren yammacin ranar aka shigo da amarya da tawagarta, yana kallon su, har aka wuce da ita a keken doki har shashinta. Baki daya bayin gidan da sauran bararorin gidan jira suke a fito da Amaryan sarki. Bude kofar keken wani badakare yayi, Innayoh ta fara fitowa, tana rike da hannun Fulani Aminatu wacce ta sha jan mayafi har kasa, tana tafe a hankali tana kara rike hannun Innayoh. shiru wurin ya dauka kafin Jakadiya Rama ta sake gud'a me mugun karfi da amo, haka ya tabbatarwa kowa Fulani Aminatu ta iso cikin masarautan.

"Ke Amaryan ma yarinya ce." Inji wata baiwa.

"Eh lallai wannan reno aka kawo mishi kenan?" Kafin kace kwabo maganar kankantar shekarun Fulani Aminatu ya zaga masarautan har ya fada kunnen sarkin gida, shi kuma ya samu Sarki Bello da maganar.

Yana zaune, a wurin shan iskar sarkin gida ya zube a gaban shi.

"Allah yabawa takawa lafiya, nazo ne da wani batu" ajiyar zuciya ya sauke sannan ya ce mishi.

"Ina jin ka"

Ya fada yana lumshe idanun shi.

"Yanzu naji labarin wai Fulani Aminatu yarinya ce karama" ya fada yana sunkuyar da kan shi.

Ware idanu yayi akan Sarkin gida, kafin ya ce mishi.

"Ka nimo min Galadima yanzu"

"Allah ya baka nasara an gama"

...

A can cikin gidan kuwa Jakadiya Rama ta wuce shashin Ajuji, cikin dakon gulma ta guntsa mata labarin, Fulani Aminatu.

Murmushin gefen baki tayi sannan ta ce mata.

"Me kika fahimta akan Yarinyar?"

"Uwar ɗakina. Akwai sulke a tare da ita. Duk harin da za a kai matukar ba a fara fatattaka sulken ba babu wanda ya isa ua cimma ta."

"Lallai kuwa Sarkin Gombe ya san kan duniya. Muje zuwa" injin Ajuji.

Baki daya labarin ya shiga lungu da sakon masarautan, labarin da ya raba kan mutane dayawa har wajen masarautan kawunan jama'a ya rabu, sannan ana ta samun sukar masarautan Gombe.

Bayan wani lokaci, manyan fada sun tura sakon niman zama da mai martaba. Kallon Sarkin Fada yayi sannan ya ce mishi.

"Bayan sallah magariba akwai liyafa sai a tattauna a can."

"Toh Allah ya baka nasara, takawarka lafiya a huta lafiya" Zubawa Galadima idanu yayi yana jiran karin bayani.

"Wato lokacin da muka isa masarautan Gombe, Sarki Shehu Usmanu ya min bayanin da ya gamsar da ni, da gaske yarinyar karama ce ainun, domin shekarun ta goma sha biyu. Asalima yanzun take wasan kasar ta. Sai dai mahaifi irin shi ba zai jure abinda yake shirin faruwa da ita ba. Ta rasa Mahaifiyar ta daga isowar ta duniya, shima bai samu ya bata kulawar da ya da ce ba, sabida katangar da aka mishi tsakani da ita, Innayoh da Fulani Shatu suka yi dawainiyar renon ta. Babban tashin hankalin ba kome bane sai jifarta da ake ta ko ina na masarautan, haka ya

saka masana suka saka shi a gaba da lallai ya dauke ta daga masarautan. Sau biyu yana zuwa wurin marigayi sarki Ibrahim amma yana jin amsar tayin shi na dan kome ba sai dan wasu dalilai gudu biyu"

Ciki da mamaki yake kallon Galadima, kafin ya gyara zaman shi yana mishi kallon karin bayani.

"Dalili na farko shine idan sarki ya amshi auren ta, zata girma a matsayin bazawara har karshen rayuwarta bata san dadin rayuwa ba, sannan zata sha wahala a hannun kishiyoyin ta. Dalili na biyu kuma tunda Sarkin Gombe yazo ake kawowa Sarki Ibrahim saran shi, wannan dalilin ya hana shi karban auren amma daga baya da ya fahimci akwai kamshin gaskiya a maganar yarinyar shine ya gaya min ya kuma roke ni da na tsaya maka a baka auren Yarinyar. Sukar Sarkin Gombe ya bar shi akan adawa irinta manyan sarakuna kaji yadda aka yi kome."

"Toh amma me yasa bai nimawa Zakaria ba sai Ni?" Sarki Bello ya tambayi Galadima.

"Ba mamaki idan da shine akan kijeran da an fadadda yakin sa kai, karshe ya mutu, kowa yasan tun zamanin mahaifin ka ya fada kai baka son yaki, wannan nahiyar tana bukatar zaman lafiya ne" Galadima ya bashi amsar.

Shiru yayi baki daya ya rasa me zai ce.

"Toh yanzun ya zan yi da ita? Kasan dai yarinya ce." Dariya Galadima ya kyalkyale da dariya. Sosai kafin ya tsagaita da dariyar shi.

"Kai kake karanta mana, labarin soyayya da kauna yau kuma kai zan tunawa baiwar da Allah yayi maka, Jarumin sarki dan soyayya ka fara akanta mana, idan bai yi aiki ba sai mu sauya salo amma maganar gaskiya zaka ajiye mulki ne ka fitar da soyayyar gaskiya daga zuciyar ka."

"Taya Galadima?" Ya tambayi Galadima yana zare idanu.

"Ka manta labarin Sarki da aljana da ka tab'a bamu? Da labarin Sarkin dodonin da Yar fulani!, Yau kuma sai ka bamu naka labarin Sarkin gobir da Fulani Aminatu" ya fashe da dariya, irin na abokan da suka san junan su, duk da galadima ya girme Bello amma kusan akwai amintaka a tsakanin su. Kishingida sarki Bello yayi cikin nutsuwa ya ce mishi.

"Dukkan su, sun fada soyayyar gaskiya ne bayan ganin yan matan ni kuma ban ganta ba zan fada?"

"Mai Martaba yana da ikon ganin ta, amma kafin nan ka fara ganin Innayoh ko zaka fahimci kome akan Fulani Aminatu."

"Yaushe galadima ya zama ɗan kanzagi ne ban ban sani ba?" Mikewa Galadima yayi yana faɗin.

"Na dibi wata guda ban ga iyalina ba, dan rashin Imani irin na Jarumin soyayya ya tsare ni jin kalar matar da aka bashi ko tausayin yan tsofin mata na bai yi ba". Lumshe idanu sarki Bello yayi dan yasan yana takalar shi da magana ne.

Tafiya yayi yana mishi dariya, bude fararren idanun shi yayi wanda suke dauke da wasu irin maiko. Tashi yayi ya nufi shashinsa ya shiga yayi wanka sannan ya fito ya saka Sarkin gida ya kira mishi Innayoh. Yana zaune a babban zauren shi suka shigo. Zubewa tayi tana mika mishi gaisuwa.

Shiru yayi yana nazarin ta, kafin ya ce mata.

"Da fatan kun iso lafiya?"

"Lafiya lau" ta fada. Daga haka bai ce mata kome ba, sai da ya gama abinda yake rubutawa sannan ya ce mata.

"Kar a bar Aminatu tasan ni ne Sarkin . Umarni na ne"

"An gama ranka shi dade"

"Zaki iya tafiya"

"A huta lafiya" ta fita, sai da ta samu damar fita ta sauke ƙatuwar ajiyar zuciya, tana kallon kofar.

"Toh me yasa baya son Aminatu tasan shi sarki ne?" Ta tambayi kanta. Sannan ta bar wurin. Tana zuwa ta samu an Fulani Aminatu ta idar da sallah, abincin da aka kawo daga gidan Galadima, suka ci har da sauran bayin daga nan suka kwanta domin sun gaji.

Haka aka yi ta shagali, har dare inda shima sarki Bello ya je nashi taron liyafar, nan suka yi ta surutu kamar zasu cire bakin su. Mikewa yayi tare da cewa.

"Ina son Aminatu haka. Akwai wanda yake da wata magana ne?" Ya tambaye su. Girgiza kai suka yi, sannan ya ficce abin shi, da wannan ya kashe bakin su baki daya.

Haka al'amuran suka Cigaba da tafiya a bangaren shi bai kuma bin ta kan Fulani Aminatu ba, sai da aka kwashe mako biyu me kyau. Sannan yayi shigar kamala ya rage kasumabr shi, ya fito sosai matashin sa, ya nufi shashin ta, kofar ya nufa aka bude mishi. Sautin tsagiyar ta yaji tare da karan awarwaron ta, suna fitar da wasu irin sauti me shiga kunne.

"Dan dalago tsaya kaji" ta fada tana d'aga mayafin da aka jera a zauren tana niman zomonta, lafiyayyen gashin kanta da ya zube a gadon bayan ta. Kasa motsi yayi yana ikon Allah.

"Kiyi a hankali Fulani Aminatu, karki fadi" Ya jiyo muryan Innayoh,

Wani irin iska ne ya d'aga labulen, daidai zuwan zomon gaban shi, garin biyo shi kawai tayi karo da shi dan bata gan shi ba sabida labulen.

"Wayyo Allah na" ta koma ta zauna dabas. Kamar wani Yaro haka shima ya bita ya zauna. Dafe goshinta tayi tana cewa.

"Wayyo ni! Waye kai?" Ta tambaye shi kamar zata yi kuka, domin ta gwaru da Kirjin shi.

"Ni?" Ya nuna kan shi. Rudewa yayi yana kallon ta.

"Ai ho toh baka da suna ne?"

"Fulani dawa kike magana?" Innayoh ta karaso wurin tana tambayar ta.

"Barka da zuwa, ranka shi." Shiru tayi tana kallon Fulani Aminatu.

"Innayoh waye shi" kallon sarki Bello tayi, girgiza mata kai yayi.

"Baffan ki ne?"

"Baffa'm!" Ta furta a hankali. Kallon bakin ta yayi da ya furta baffa'm.

Barka □ ya kuke ga pagen nayi shi ban sani ba ko ya hadu for me kome zam-zam □□ ba mamaki ranar talata da Alhamis mu kuma haduwa sai dai ban sani ba ko Allah zai kai mu ranarku ina muku fatan Alkhairi

#Mai_Dambu

[3/28, 11:49 AM] UmmuHabibah□□❤: KALLABI...!

A tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

https://www.wattpad.com/1205922691?utm_source=android&utm_medium=link&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=Mai_Dambu&wp_originator=jEIgEgxQnZJ5LDIlhjtY7iqHX7Ay8MxiyvCu7Tr%2BNpFDvcTEdIFEupX6i6ZW8mYIOF2zHM3Yd3iwbF69Wzb%2FxjVRshRLctjr4IhnWv9yq0YNV6Ycy5hS1ehPf6kl0vF1

<Babi Na Tara>

GAISUWAR WANNAN SHAFIN NAKU NE YAN KALLABI LOVER FANS AKWAI KAUNA ME KARFI A TSAKANIN MU DA KU A CIGABA DA TAFIYA A HANKALI □😍□😜

"Baffa'm!!" Shima ya fada tare da kallon Innayoh a rude, dauke kai tayi dan kallon tuhumar da yake mata, tashi yayi a hankali ya kalli Fulani Aminatu da take kallon shi da Idanunta masu shirin kawo ruwa.

"Toh me yasa...?" Sai kuma yayi shiru, yana kallon ta, kafin yayi wani yake, ya juya ya bar zauren har zai rufe kofar ta ce mishi.

"Baffa'm!" Juyawa yayi yana kallon ta.

"Ka bar min dan dalago ya fita" tsintar kan shi yayi da yake, sannan ya ce mata.

"Za'a kawo miki shi" da sauri ya fita yana dafe kirjin shi.

Haba Bello kai fa sarki, ita kuma yarinya ce

Shashi na zuciyar shi ya bashi amsa, jinjina kai yayi yana kara yarda da abinda zuciyar shi ta gaya mishi.

**

"Auren shi ne karshen burin ku, ba zaku tab'a cimma shi ba." Dan k'ank'anin mutum kamar yaro dan shekara uku ya gaya musu haka.

"Jarmai ya zamu yi?" Suka kuma tambayar shi a karo na biyu, zana kasa yayi tare da kallon su, sannan ya ce musu.

"Ku fita ku bar ni da wancan da wannan" ya nuna mutane biyu da kan su yake rufe da mayafi dariya yayi da yar muryar shi kamar na gyare ya ce musu.

"Kuna tsammanin zaku iya ne? Ko a tunanin ku Bello zai fadi ne kai tsaye? Hmm" ya faɗa yana watsa wasu kananan duwatsu saman kan yashi.

"Zaka yi mulki amma sai ka samo irin Aminatu, ko ka amshe ta da karfi ko kuma ka yi ta zaman jiran bayyanar ta" ya fada a karo na uku.

A matukar firgice suka kalli junan su, kafin suka kalle shi dan ya fato su yayi da kananun yatsun hannun shi ya ce musu.

"Kuna da zabi dama uku amma biyu zaku dauka." Kasa yayi da murya sosai me kama da ta gyare yana magana baki daya jikin su rawa yake, kafin ya bude muryan shi.

"Wane kuka zab'a? Zaku jira amma kafin nan zaman taurari guda biyu wuri guda zai iya cika ya tumbatsa har ya fitar da wani irin haske, shi hasken zai kuma dakatar da ku dan haka a yanzu baku da hurumin dakatar da su, amma akwai shekaru masu zuwa"

"Kiru me yasa sai mun jira?" Matar ta fada ƙasa ƙasa.

"Idan kuka fito da burin ku zai iya kararr da ku, kuje bayan shekara biyar ku dawo ina nan ina jiran ku! Kuma kafin nan gyara muku kome sai dai damar haka, amma ku sani ku nisanta kan ku ga amayar da adawa ku musamma'n ma kai da baka da hakuri" gyada kai yayi har zasu mike, sai namijin ya ce mishi.

"Kace idan ba Fulani Aminatu sai dai na jira?" Murmushi yayi sannan ya ce mishi.

"Idan ka kuskura ka tun kare ta, mutuwa yayi domin dalilin da ya saka aka had'a ta da Bello? Hmm ka kiyaye" ya fada yana dariya, a rude matar ta kalle shi.

"Kamar ya hmm?"

"Sabida akan ta zai fara? Akan ta zai fidda kan shi, idan har kuka fito da shi ba zai yi muku dadi ba, amma idan har kuka mishi kisar mun muke fa? Bana ce kuyi hakuri a jira lokaci ba"

Gyada mishi kai suka yi, sannan suka fita daga kokon ramin. Suna fita ya zubawa kasar gaban shi idanu yadda ya rine da jini, rintsa idanu yayi yana wasu yan surutai, jini ne ya cigaba da lullebe tiren, sautin karan takoba hadi da kukan mutane yasa shi buɗe idanun shi. Zanen hoton fuskar mace ce nan ya shiga zanawa sai da ya jima kafin sunan Fulani Aminatu ya bayyana a kan kasar.

"Tabbas ita ce! Ita ce!! Ita ce!" Ya fada yana zare idanun shi. Buga kasar ya kuma da sandar hannun shi, wani irin duhu ya mamaye yashin, rintsa idanun shi yayi na wani lokaci kafin ya bude sakamakon dumin da yaji a hancin shi na alamar ruwa, shafawa yayi ya ga jini ne, sake buga kasa yayi da yar ƙaramar jaririyar muryan shi ya ce.

"Idan ba ita ba ce waye?" Ya fada da ƙarfi. Sannan ya bude wani tunkuyar da yake gaban shi. Ya zuba idanun shi cikin tunkuyar kafin ya ya rufe, tashi yayi a hankali ya nufi wata ƙatuwar randa ya hau kai, sannan ya leka a hankali yana kallon cikin tukunyar. Wani irin farin hayaki yake, kafin ya kurawa hayakin idanu. Wani irin sauti yake fita a cikin tukunyar, can kuwa da ya matsa da kallon sai ga wani irin hayaki me sufar zaki ya wani irin yunkurowa kamar zai cafke shi, mugun razana yayi sai da ya tintsira da sauri ya tashi yana me kartawa a guje. Jikin shi yana rawa zunzurutun tsoro. Komawa yayi wurin kasar ya sake ganin kasar shi tana fitar da wannan sufar Zakin a jikin zanen hoton Fuskar Fulani Aminatu. Dafe wuyar shi yayi tare da zaro idanun shi. Kafin kace me jini ya fara zuba ta hanci shi da bakin shi, haka yayi ta shure-shure har ya mutu.

Jinin da ya fita ta hancin shi da bakin shi suka yi ta gaggarawa cikin yashin, ya shige ya b'ata tass a cikin shi.

**

Kaiwa da komowa yake, Galadima da waziri sun yi cirko cirko. Tsayawa yayi yana kallon su. Duk da yana dame amma bai hana shi tsayawa ya kalle su ba.

"Baffa'm!"

Ya furta, cikin jimamin sunan Waziri Zakaria ya kalle shi kafin ya ce mishi.

"Yanzun don Allah Fulani Aminatun ce ta kiraka da Baffa'm?" Zama yayi a kujeran shi, sannan ya kalli Zakaria ya ce mishi.

"Jeka"

"Toh Baffa'm!" Bude Idanu yayi, kafin ya mai da ya lumshe, yana jin kamar yadda ta kira shi. Sam sunan bai mishi ba Waziri yana fita ya tashi ya zauna yana kallon Galadima yadda ya tsare shi da idanun ya shi zubewa a gaban Sarki Bello.

"Takawar ka lafiya! Matashin Sarkin da babu irin shi, akwai wani abu da na gano jiya zuwa yau" a hankali yayi kasa da murya. D'ago kai yayi yana kallon sarki Bello. Mikewa suka yi, suka shiga takawa har saman wurin shan iskar shi. Anan Galadima ya shiga mishi bayanin abinda aka gaya mishi akan Fulani Aminatu. Baki daya sai da ya firgita sosai.

"Wannan shine dalilin aurar da ita kenan?"

Girgiza kai Galadima yayi tare da kallon shi, idanun shi ya cika da kwalla. Ya ce mishi,

"Wallahi ban sani ba, amma tabbas akwai hatsari masu yawan gaske a rayuwar ta, ba iya ita ɗaya ba hatta masarautan nan yana fuskar ta hatsarin matsalar bamu san ta inda zata fara fuskar ta rayuwar ta ba. Sai dai abinda nake hasashen indai zata kasance haka toh dole."

"A'a! A'a!! a'a! Ba zan iya ba, ba kuma xan iya ba, ba zan bada ita ba. Idan na fahimta itace ƙaddara ta zab'a?" Ya fada yana jin wani irin yanayi kamar zai yi kukan tausayin ta.

"Galadima na yarda da kai, duk da ina tsoron cin amana. Galadima ka boye tauraron Aminatu. Idan ya kasance nawa tauraron zai mutu ka rufe nata, ina jin kaifin jinin ta a kaina." Ya fada yana me juyar da bayan shi, dan baya son Galadima ya ga saukar kwallar da yake zuba daga idanun shi.

"Mai Martaba!"

"Jika kawai" ya fada bai juya ba, shi kan shi, yana jin wani irin abu a ran shi, domin jiya baki daya bai yi barci ba sakamakon mafarkin da yayi na yakin da ake. Dake shima kan shi Hatsabibin kan shi ne yana farkawa ya shiga bincike da dube dube, anan ya gano asalin abinda yake bibiyar Aminatu.

Sai dai har asuba bai iya barci ba, kuma bai rintsa ba, sai asuba bayan ya tafi masallaci ya dawo ya samu barci. Shi yasa ya kudiri Aniyar sanar da mai martaba gaskiyar abinda yake shirin faruwa.

Haka yanayin ya cigaba da tafiya, har tsawon kwanaki. Kafin Galadima ya kuma samun shi da maganar.

"Allah ya baka nasara an rufe tauraron ta, sannan" shiru yayi ya rasa yadda zai iya gaya mishi.

"Ina jin ka Kawu, kome ka gaya min zan dauka"

"Na mai da kome nata na rufe, sai dai ban sani ba zaren ku zata yi tsawo da ita amma ba makawa cikin gidan nan za a iya samu wani labari domin ina da yakinin akwai wanda yasan wacece Ita"

Kurawa Galadima ido yayi, kafin ta ce mishi.

"Sai na datse makoshin kowaye! Tunda ka rufe shi kenan" daga haka ya juya ya cigaba da rubutun shi.

"Toh Baffa'm" d'ago kai yayi, wani irin yake yayi sannan ya cigaba aikin shi bai kuma magana ba.

**

Bayan kwana biyu.

Yau ya kasance laraba, fitowa tayi tana kallon gidan tun zuwan su bata tab'a fitowa ba, dake lokacin rana yayi zafi tsakanin sha biyu zuwa daya ne, baka ka ganin motsin kowa. Gyara zaman mayafin ta tayi tana rike da zomon ta, tsalle yayi garin sauka ya ja mata tsagiyarta.(beads ne ko nace jigida, amma a can an fi kiran shi da tsagiya sabida suna kara kamar duwatsun ruwa suke) aikuwa sai ga zaren ya tsinke ita kanta bata sani ba, shi kuwa dan dalago shashin Sarki Bello ya nufa, dake ta bayan gidan suke ba ta gaban gidan ba, dan haka babu wanda ya sani, wurin shan iskar karamar lambun ce, me kyan gaske wurin ya nufa ita kuma bata lura ba ta wuce ta wata yar karamar kofa ta shige shashin Sarki Bello.

Tafiya take har ta fito da kofar da masu tsaro suke.

"Baku ga dan dalago ba?" Da sauri suka juya suna kallon ta, cikin girmamawa suka gaishe ta.

"Yana ciki amma yana barci baya son hayaniya" gyada musu kai tayi, suka nuna mata kofar Mai Martaba, su a tunanin su shi take nima. Tattara mayafinta tayi ta shiga tana kiran shi a hankali.

Yana kwance akan wani farin buzu, yayi matashi da wani matashi me ɗauke fatar zaki. A hankali ta kara tana kallon shi, hango tawada tayi ta zauna a dauki alkalami, kallon shi tayi kuma sai ta fasa kawai ta dangwala da yatsar ta, ta nufi goshinsa domin ta dangwala mishi, ya rike hannun ta. Wani zaro idanu tayi tare da toshe bakin ta.

"Tashi ki koma can ki zauna!" Girgiza kai tayi ta rarrafe, tsagiyarta yana sauka yana wani irin kara, bude idanun shi yayi ya zuba mata idanu ganin yadda take rarrafen sai da murmushin ya so subuce mishi. Can kamar an ce ta juyo, lumshe idanun yayi kamar me barcin gaske.

Juyawa tayi ya bude idanu, jinjina Yaranta ta kawai, kuma da bai ji shigowar ta ba, haka zata zana mishi fuska da tawada. Gyara kwanciyar shi yayi, ya cigaba da barcin shi duk da barci rabi da rabi ne, domin yana jin yadda take barna, sai ya bude Idanu ya ganta zaune. Kamar ba ita ba tsabar rashin jin magana.

Tana zaune a wurin har itama barci ya dauke ta, tashi yayi yana kallon ta, kwashe tsagiyr yayi ya saka a cikin wata yar akwati ya ajiye, sannan ya karasa inda yake ya dauke ta cak, ya wuce da ita turakar shi (😒fassaru ba wani abu zai mata ba kawai ya kai ta ne domin tai barci yawwan dan nasan halin ku da ririta al'amari)

Sannan ya fita ya shirya, ya nufi masallaci, bai dawo ba sai yamma ya manta da ita ma baki daya sai da ya shigo ya samu taci Uban turakar domin hatta shimfidar turakar a kasa yake, litattafan da yake rubutawa ya samu an yi ɗai-ɗai da su, kamar ya kurma Uban ihu yake ji sabida barna kuwa tawadar shi ta rubutu, anyi wasa da da ita. Bata ci kome ba a dakin amma kuma tayi mishi barnar da ko a tarihi bai tab'a jin wanda yayi irin shi ba, kallon Sarkin gida yayi yana kallon gidan.

"Ka kirawo min Innayoh"

"Allah ya baka nasara, wannan ne karo na farko ayi hakuri idan tayi karo na biyu sai a kira ta." Kwafa yayi, domin a cikin litattafan shi akwai wani labarin da yake masifar kauna me sunan Soyayyar kusurwa daya, labarin Sarkin dodonin da

Zainatu. Wannan labarin kaf labarun sarki Bello babu kamar shi domin ita ce bakandamiyar shi. Amma yarinyar nan ta zo ta wargaza mishi kome, dam haka shi da Sarkin Gida suka gyara ko ina tsaf, sannan ya zauna yana mai da numfashi.

... Ita kuwa Fulani Aminatu da ta ga irin barnar da tayi da sauri ta fita daga shashin ta nufi shashin ta, tana zare ido, bata ga dan dalago ba haka ta d'aga musu hankali. Aka fita niman dan dalago,can aka samu shi a cikin lambu yana fidda jini ta hanci ta baki. Wani irin ihu tayi tana faduwa a kasa ta dauke shi.

"Wayyo Allah na,Wayyo Allah na,Wayyo dan dalago Wayyo Allah na". Ta fada da wani irin kuka tana rungume shi, sosai ji take kamar wani dan uwanta ne.

"Me ya same shi?" Inji Innayoh da ta ji kukan ta fito a razane, tana zaune ta saka shi akan cinyarta tana kuka kamar me.

"Lafiya?" Sarkin gida ya iso wurin su.

"Zomon Fulani ne wani abu ya same shi" d'aga zomon yayi ya kalla da kyau.

"Ku matsa akwai mugun dabba a wurin shi ya tab'a shi" ya fada ja bada kowa yayi, kamar sarkin gida ya san me zai faru ya sa kowa ya matsa, aikuwa sai ga wani irin bakin maciji yana tuttukowa kamar ana turo shi, ihun bayi mata ne ya saka Fulani Aminatu d'ago kai tana kallon bakin macijiin nan da ya fasa kan shi kamar faranti babba. Yana zaro harshen shi jajjur da shi.

"Fu...la...ni!!!" Inji Innayoh, da tsabar kidima da tsoro, ya saka bata iya magana ba, sai kiran sunan Fulani da tayi a rarrabe.

Kasa motsi ita kanta Fulani Aminatu tayi domin baki daya ta suma. Ihun da ake ya saka shi fara kokarin kai fashen yawu, yadda ya fesa yawun babu wanda ya ga zuwan shi sai dai sun gan shi durkushe da rigar saki a gaban Fulani Aminatu, yana kallon yadda ta kafe a wurin. Ciro wukar da yake kugun shi yayi a fusace ya saka wuyar macijin, sannan ta juya ga Fulani da take kamar an dasata zaune.

Ya saka hannu ya dauke ta, sannan ya mike.

"Ka kai gidan Galadima kace ina niman shi" sannan ya shiga ta shashin Fulani Aminatu ya kwantar da ita akan Kilishin da yake zauren ta.

"Ki saka idanu akan ta."

"TOH ranka shi dade!" Shiru yayi yana kallon hawayen da ya bushe a saman fuskar ta. Tashi yayi ya nufi wurin shan iskar shi, nan ya samu Galadima. Zama yayi tare da kallon kasa.

"Allah ya huci zuciyar ka. Insha Allah babu abinda zai faru ga Fulani Aminatu!"

"Sakon daga ina ne?" Ya kalli Galadima bayan ya tambaye shi.

"Daga wajen masarautan ne, amma a cikin masarautan aka idda aikin." Ya bashi amsa.

"Ita yarinayar meye na farmakarta?" Ya tambaya da ƙarfi.

"Sabida yanayin da aka tabbatar akan ta."

Wani irin dariyar takaici ya kama yi kafin ya ce.

" Kafin gobe a fidda min me aikin ko na dauki salon da bana son dauka....

_____

Wash.....Anya ba wahalar banza nake ba? Wallahi sai ji nake kamar ina aikin banza

#Mai_Dambu

[3/28, 11:49 AM] UmmuHabibah□□❤: KALLABI....!

A tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

https://www.wattpad.com/1206238744?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=share_published

<Babi Na Goma>

Gaisuwar wannan shafin naki ne Mrs Sadauki Mom Nasmah sakon ki ya iso Nagode sosai

"An gama Allah ya baka nasara" Galadima ya fada a sanyayye, domin ya jima bai ga fushi ko fusata a idanun shi ba, balle ya ji maganar b'acin rai.

"Kayi hakuri." Cire rigar shi yayi tare da juya bayan shi.

"Subhanallahi! Kana bukatar kulawa fa"

"Kar bashi ka nimo masu laifin" ya fada bayan ya mai da rigar, fita Galadima yayi ya turo masu maganin masarautan amma fir Mai Martaba ya ki bada ciwon a duba mishi, kuma guba ce domin sake rura fatar shi take. Haka ya fito ya nufi shashin Fulani Aminatu da zazzaɓi ya rufe ta.

Tana barci ne amma sai firgita take, tana matse hannun ta. Yana zuwa ya zauna a inda take ya riko hannun ta, sannan ya kalli Innayoh.

"An zo an duba ta?"

"Eh an zo" ta fada cikin girmamawa, fita suka yi aka bar su a wurin, abu ya ciro a cikin rigar shi ya saka mata a kasar matashinta, sannan ya fita. Dakyar ya isa kofar shi kafin ya zube akan gwiwar shi yana dafe kirjin shi. Ai kuwa amai ya fara wani irin bakin jini. Kakarin aman shi masu tsaron shi suka jiyo sai gasu da gudu, kafin kace me har sun kinkime shi sai turakar shi. Suka kwantar da shi a kife sabida nuna musu bayan shi da yayi.

Sarkin gida ya tafi har gidan galadima ya kuma kiran shi.

"Amma dai Bello akwai dan banzan taurin kai kamar arnan farko sai da na hana shi fita ya tsaya a kawo mishi magani" har suka isa turakar fada yake, sannan ya saka aka yaga rigar aka zuba mishi magani.

"Sarkin gida ina zan samu danyen madara"

"Ba za a rasa a wurin Innayoh ba, domin daga gidan gonar masarauta ana kai mata." Sarkin gida ya fada yana kallon Galadima.

"Maza amso min"

Fita yayi da sauri ya amso madaran, yadda ya gayawa Innayoh halin da mai Martaba yake ciki ya d'aga mata hankali, domin gani take kamar laifin ta ne da ta bar Fulani Aminatu ta fita.

Har wurin magariba Mai Martaba bai dawo hayacin shi ba. Shigowar Waziri Zakaria ya saka suka zuba masa ido.

"Ya jikin Baffana yake?"

"Sai godiya amma ba a magana domin bai san wanda yake kan shi ba" inji Sarkin gida. Galadima kan bai d'ago kai ba, sai da ya samu Mai Martaba ya shanye madara da maganin nan, ko dakika dari da ashirin ba a dauka ba, ya fara kokarin amai, saka mishi wani tasa aka yi bayan ya mike zaune, ya shiga amai sosai sai da ya fitar da gubar. Sannan ya kalli galadima ya ce mishi.

"Ya Fulani Aminatu?" Sannan ya koma ya kwanta. Sai barci me nauyi yayi gaba da shi.

Ajiyar zuciya suka yi sannan galadima ya umarci Sarkin gida da ya kula da shi. Sannan suka fita baki daya suna jajjanta abinda ya faru, dake a shashinsa aka yi sallah la'asar magariba kuma Galadima ya wuce masallaci a can ake sake jajjanta mishi abinda ya faru.

Bayan ya idar da sallah Yarima Yakubu ya ce.

"Dake ragon maza ne shi yasa ta kare mishi"

"Ce maka aka yi jarumta kamar niman bayi mata ne da wasu suke amfani da matsayin su?" Waziri Zakaria ya tambaye shi.

"Eh na yarda da haka duk ranar da na samu dama sai na fille kan kowa" Yarima Yakubu ya faɗa yana kad'e rigar shi.

Kallon juna suka yi Galadima da waziri, cike da mamaki domin da alamu Zakaria ya Haukace.

**

Sanyin asuba ya rab'e shi kasancewar an bar tagogin a bude, yasa shi buɗe idanun shi yana sauke ajiyar zuciya.

Tashi yayi zaune yaji garau. Murmushi yayi yana kallon tagar. Sannan ya hango Sarkin gida yana ta sharan barci. Ban daki ya shiga ya zauna yana me kallon tagar. Tunanin jikin Fulani Aminatu yake, ya jima a wurin kafin yayi wanka. Ya fito a hankali ya shirya. Ya saka kayan sakin shi sannan ya gabatar da sallah da ya rasa,

kafin ya nufi filin bayan gidan Fulani Aminatu, ya shiga wasa jinin shi. Kiran sallah ya tsayar da shi ya tafi sallah, bayan ya dawo ya cigaba.

"Fulani tashi asuba tayi." Innayoh ta tashe ta,

"Innayohhh!" Ta fada a sangarce,

"Tashi lokaci ya kure, zaki kaiwa Baffa'm ɗinki madara" da sauri ta tashi zaune tana raba idanun.

"Innayoh! Gaskiya ba zan je ba zai min fada"

"Me kika mishi?"

"Babu" ta fada tana wani tura baki. Kallon ta Innayoh tayi, ta dauke kai tana me sauka a gadon.

"Fulani kin shiga kin mishi bar..."

"A'a fa, ban shiga wurin shi ba" ta fada da ƙarfi tana shiga ban daki.

"Allah ya kintsa ki" inji Innayoh,

Bayan yayi alola tazo innayoh na kallonta, har ta idar da sallah sannan ta fita can sai gata dauke da magani da kuma madara.

"Innayoh kullum sai na sha magani nan ne? Ba dadi" ta fada kamar zata yi kuka, yadda Innayoh ta b'ata rai yasa ta amshi maganin ta sha, sannan ta dauke madaran ta shanye tass. Wannan shine al'adar Innayoh kenan.

Kwanciya tayi bayan Innayoh ta saka ta tayi wanka, ta shirya ta cikin wasu kaya masu kyau, an jera mata kayan kwalliya irin na matan sarakuna. Sannan ta kwanta. Baki daya ta manta da batun dan dalago barcin ta kawai take, bayan kusan awa guda. Taji karar takuba. A hankali ta tashi fita tayi babu wanda ya sani ta nufi inda take jin sautin. Daga nesa ta hango shi dan dalago yana cin ya'yan itaccen da aka yanka mishi a wani tire. Da wani irin farin ciki ta karta a guje ta dauke shi tana faɗin.

"Dan dalago na" ta wani rungume shi, yana jinta bai juya ba ya cigaba da abinda yake, wurin shi ta nufa tana kallon shi.

"Baffa'm!" Sauke takobin yayi, ya kalle ta da wutsiyar ido.

"Nagode da ka kula min da Babban abokina, da ya mutu da nima na..." Kura mata ido yayi yana jiran yaji me zata ce.

"Da ban san ya zan yi ba nima, Hamma Buba ne ya bani tun yana dan karami. Ina kewar shi sosai" ta fada idanun ta,yana zubda kwalla. Haka kawai ya tsinci kan shi da tambayar ta.

"Me ya kawo ki masarautan nan tunda kina kewar hammanki?" Kallon shi tayi sannan ta tab'e baki ta ce mishi.

"Ban san dalilin da yasa aka kawo ni ba, Innayoh ta ce idan na girma nayi hankali zan fahimta, amma karka gayawa kowa dan tace babu kyau na fadawa wani" ta fada cikin shahshanci da shirme.

"Ai daga ni sai dan dalago muka ji idan ma kin ji labarin a wani wurin toh ga wanda ya faɗa!" Ya nuna mata dan dalago.

"A'a yana magana ne?" Ta tambaye shi, tana zare ido alamar a tsorace take.

"Kwarai tunda ai ba ni na baki ba? Kuma zai gayawa Hammanki duk abinda ya faru, dan haka ki yar da shi domin munafuki ne" k'amk'ame dan dalago tai tana kuma kallon shi.

"A'a ba zan yarda shi ba, Hamma na ne ya bani shi tun yana jariri"

Share ta yayi domin ya lura ba zata tab'a yarda ta rabu, da dan dalago ba, shima kuma bai san ya akayi yake son ta rabu da zomon ba. Ajiye dan dalago tayi ta zauna tana kallon yadda ya dauki baka yaja. Sannan ya sake a jikin mutum mutumin ciyawa da aka ayi. Kallon shi tayi ta ce mishi.

"Baffa'm!"

"Hmm!"

"Ka koya min nima" ta fada tana mishi kwal-kwal da idanu.

"Aikin maza ne ba na mata ba" ya fada yana cigaba da harbawa.

"Don Allah" ta fada cikin wata irin murya, sake kwarin yayi ya juya yana kallon ta.

"Kin ci abinci kuwa?"

"Na ci"

Zuwan su Innayoh wurin ya sata juyawa.

"Innayoh kice ya koya min" sumkuyar a kai Innayoh tayi da sauran bayi matan.

"A kula da ita ta daina fitowa da rana ko da sassafe"

"Baffa'm" ta fada hawaye na zuba mata, bai kula da ita ba. Ya cigaba da abinda yake yi har aka wuce da ita. Sakata suka yi a tsakiyar su, a hankali ta juya tana kallon shi yana abin shi. Juyawa tayi ta cigaba da tafiya, sai lokacin ya juya yana bin su da idanu. Bayan ya gama horon ya koma sashensa yayi wanka sabida zufar da yake karyo mishi.

.....

Wajen hantsi aka fito da wasu bayi mata biyu, sun ki magana kawai sun amince da sune suka turo macijin. Shiru fada yayi kafin ya bude baki kamar ba zai magana ba ya ce.

"A kashe su."

"Mai Martaba! Babu kuskure a hukuncin ka?" Inji Chiroma,

"Me zan musu? A cikin gidana a da'irar sansanina suka farmaki matata?" Ya fada,

"Haka ba zai kara kome ko ya rage kome ba, sai dai tarin bakin jini da ita Fulani Aminatu" Yarima Yakubu ya faɗa bayan ya mike zai bar fadar.

"Wannan shine mafi munin yanayi a tarayyar ka da Yarinyar da aka alakanta rayuwar ka da ita" ya sakai yafita.

**

Zauren Fulani Aminatu.

Jakadiya Rama ce a bayan Ajuji, bata zauna ba tana tsaye tana kallon kyawun zauren Fulani Aminatu.

"Lalle maraba da zuwa, yau muke shirin kai Fulani taga Yayunta"

"Ba zuwan tattaunawa nayi ba, an san Fulbe da kunya da kawaici sai ga labari yana yawo a cikin gidan Fulani Aminatu ta yarda da al'adar su tana bin Mai Martaba har turakar shi? Koda yake taya yar kwarkwara zata yi kunya! Kamar yadda kika saba turata ki turata ta hana shi idda nufin shi na kashe bayin da basu ba basu gani ba. Idan tayi hakuri zata isa inda yake, karki manta a nan macen da ta isa mace take rike kambunta ba kwaila ba"

Har ta juya zata tafi, Innayoh ta ce mata.

"Mace da ta isa mace ita Jarumin sarki ke bada rayuwar shi domin kare nata, idan har kwarkwarah tana da bakin magana toh tabbas matar sarki idan ta tashi magana ba za a ji muryan kowa ba! Ba zan raba had'in da Allah yayi ba, sai dai maki gani zai iya mutuwa"

"Ke baiwa!" Ajuji ta daka mata tsawa, murmushi Innayoh tayi sannan ta ce mata.

"Fusatar na me? Kin ji haushi ne? Idan rana tafito tafin hannun bai kare shi. Iya yau gare mu gobe ta Allah ce kiyi shiru ki ja bakin ki koma gefe kiyi kallon abin da zai faru ga sarki da Kwailar matar shi, barin da ba zai tab'a goguwa ba a tarihin masarautar nan labarin da zai zauna daram a zukatan al'ummar wannan yankin. Mun iya magana amma mun fiso ayi maganar mu haka zai karawa shukar mu yabbanya"

Kasa magana Ajuji tayi ta saka kai ta fita, sannan ta juya ta kalli Fulani Aminatu, da tayi tsuru-tsuru tana kallon su. Baki daya ba zata ce ga inda Maganar ya dosa ba.

Dan dukawa kaɗan Innayoh tayi tana kallon Fulani Aminatu.

"Daga yau ba zaki kuma fita ba, ki zauna anan, amma zan tura ayi magana da Baffa'm ki roke shi da ayi musu afuwa"

Hannun ta Innayoh ta rike, tana kallon ta kamar zata yi kuka.

"Innayoh yaushe zamu bar nan bana son nan mu koma gida" murmushi Innayoh tayi sannan ta ce.

"Zan kika fara zaman nan"

Mikewa tayi ta saka aka kira mata sarkin gida, can sai gashi ya zo.

"Fulani tana son ganawa da Mai Martaba ka gaya mishi"

"An gama" sannan ya fita, har fada anan kan tattauna batun abinda ya faru jiya, sarkin gida ya gaya mishi sakon Fulani Aminatu. Babu musu ya mike. Gyara murya Waziri Zakaria yayi ya ce.

"Baffa'm" cak ya tsaya kunya ta kama shi sam ya manta ko zai tashi sai an sanar yau sai gashi ya mike. Komawa yayi ya zauna, yana muzurai. Take sarkin fada ya fara kokarin mikewa yana faɗin.

"Gyara kintsi! Mai martaba zai tashi aikin gaggawa" watsawa Waziri harara yayi, yana tashi ya nufi shashinsa, Waziri da Galadima suna biye da shi. Yana shiga ya cire kayan baki daya ya sauya. A zauren shi ne farko ya gansu zaune dauke kai yayi kamar bai gan su ba.

"Baffa'm" inji Zakaria,

"Ban san yaushe na zama kakanka ba, amma zan hukuntaka zan baka aikin kula da bakin da zasu shigo da fita na masarautar nan baki daya daga yau aikin ya fara"

"Baffa sabida kawai nayi abu karami za a mai dani duba gari" Galadima bai ce uffan ba, sai da ya fita ya mike shima yana faɗin.

"Yawwan duba gari idan ka fita"

"Kawu har da kai?"

"Toh na daina"

Shi kuwa yana fita ya nufi shashinta ta, tun daga babban zauren ya fahimci yar sakalcin tana daki, yana shiga ya same ta, da dan dalago.

"Yawwa dan dalago, yaushe samu tafi gida na gaji da nan" gyaran murya yayi U shiga cikin dakin. Gyara zama tayi tana kara daura zomon kan cinyarta.

Shiru yayi yana jin tana zuba shirme da dan dalago.

"Tashi" ya fada mata, mikewa tayi ya kalle ta da kyau sannan ya ce mata.

"Baki iya kawo ruwa bane ga bako?" Ajiye zomon tayi, ta fita tana faɗin.

"Ai Innayoh ta gaya min" ta fada bayan ta nufi wani daki na musamman da aka ajiye kayan Abincin da aka tanada, wani tire ta dauko ta kawo dakin, an saka dan gamon da ake sakawa a kasan kwarya ya rike yar kamar ƙwaryar da yake rufe da damammen fura da nono. Sai kamshi kanumfarin da masoro da citta yake.

Dauka tayi ta mika mishi, tana faɗin.

"Baffa'm amsa ka sha?" Ba musu ya amsa, ya dama a hankali sannan ya fara sha, yana kallon ta komawa gefe tayi can ta zauna tana wasa da dan dalago.

"Zo kisha"

"A'a na koshi"

"Toh zaki dauki kayan ki" a hankali ta taso, tana kallon shi kafin ta ce mishi.

"Me yasa ba zaka sha ba?"

"Ban iya cin abinci ni daya ba"

Zama tayi sannan ta ce mishi.

"Innayoh ta hana ni cin abinci da wani"

"Ni ne wani?"

Sunkuyar da kai tayi tana matse hannun ta.

"Waye ni?"

"Baffa'm"

"Toh daga yau ni ba baffa'm bane, Nima ina son zama abokin ki kamar yadda kike daukar dan dalago"

Sake baki tayi tare da cewa.

"Toh ai kai ba zan iya daukar ka ba, kayi kato" ta fada kamar zata yi kuka.

"Toh lallai dole kiyi abokata dani"

"Ayya taya zan dauke ka kamar dan dalago?"

Da alamu idan aka kwana biyu kallon dan dalago zata maka ka yanke dan banza ka huta, domin shi ya hana ka samun kanta

"Toh shi kenan, me yasa kika tura a kira ni." Shiru tayi tana kallon kasa ta rasa me yake mata dad'i domin ta manta yadda suka yi da Innayoh.

"Baki ji bane?" Da sauri ta d'ago kai tana kallon shi kafin abin ta dawo mata rai, d'ago kai tayi tare da amsar ludayin hannun shi. Tana sha tana magana baki daya jikinta rawa yake ta ce mishi.

"Baffa'm! Ka gayawa Mai Martaba ayiwa su Hakama da Arewa afuwa ba zasu kuma ba. Idan aka kashe su ba zai kawo karshen kiyayyar ba. Haifar da shi zaka yi a madadin a haifi da me idanu ba. Baffa'm rayuwa da mutuwa duk na Allah ne muke sayan kiyayya muke sayan soyayya. Idan har mae martaba ya musu afuwa zai iya wucewa. Amma kiyayya tana iya rayuwa na tsawon karninnika a dakatar da kiyayyar tun Yanzun!" Murmushi yayi tare da kallon ta sannan ya ce mata.....

_____

Kai ma mai martaba da rigima kake taya Fulani zata dauke ka kamar dan dalago. Ka mata bayani yadda zata fahimta kasan yadda aka saka mana idanu yanzu tace kayi kato Allah kadai yasan abinda su Ooo zasu fada kaico☹

#Mai_Dambu

[3/28, 11:49 AM] UmmuHabibah❤: KALLABI...!

A tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

<Babi Na sha ɗaya>

Fatan Alkhairi gare ku Yan uwa da abokan arziki Nagode sosai 😍

"Me kike so?" Ya tambaye ta cikin tattausar harshe. Goge kwallar da yake zubo mata tayi har lokacin jikinta rawa yake.

"Baffa'm a yafe musu" ta furta bakinta yana rawa, saka hannu tayi ta rufe bakin, domin wannan ne karo na farko da ta samu kanta da rokon wani , kuma baffa'm ba wani ba ko mahaifinta bata tab'a samun damar zama da shi haka ba. Kallon ta yake a hankali shekarunta basu kai rike abinda ya fada ba, girman ta bai kai shi ba.

Dan bata da wannan girman,

Innayoh zuciyar shi ta furta, kenan .

"Toh zan gayawa mai Martaba, amma zaki yi abu daya?" Da sauri ta d'ago kai tana kallon shi. Hararan dan zomon ta yayi da yazo kusa da ita.

"Zaki mai dani abokin ki?" Ya fada yana kallon cikin idanunta, itama shi take kallo, lashe bakin ta tayi tana me ƙoƙarin janye idanun ta daga kallon shi da ya mata kwarjini. Da sauri ta dauke kai tana kallon dan dalago.

"Kai fa Baffa'm" hannun shi ya kai saman labbenta, a hankali ya d'ago fuskarta da daya hannun shi, yana shafa kyawawan labbanta. Sosai ya janyo ta jikin shi yana kallon kwayar idanun ta. Kafin ya kai kai shi zuwa kunnen ta.

"Abotar mu babu karya, babu cikin amana gaskiya zamu kulla. Sannan zamu tafi ko ina tare kin yarda domin har wajen masarautan nan zan kai ki" kamar wata gunki haka ta tsaya yana magana da ita, a hankali ya mike ya barta durkushe da gwiwowin ta, sai da ya isa bakin kofar ya juya yana kallon ta. Murmushin gefen baki yayi sannan ya fita a dakin.

Zubewa tayi tana ajiyar zuciya, domin baki daya ya saka ta wani irin yanayi.

Tunda ya fita ya nufi shashinsa, ya rubuta sako zuwa ga mutanen fadar sannan ya badda umarnin a dakatar da kashe su hakama da arewa, sun samu afuwa daga Fulani Aminatu, dan haka wannan ba aikin shi bane, ita tayi musu afuwa kuma shima yayi musu, dan haka ayi kokarin kiyayye abinda da zai kuma had'a su.

**

Wurgi yayi da kofin hannun shi tare da fasa ihu yana faɗin.

"Ba haka nake son mulkin ba, ba haka nake so, so nake ayi mulkin da ko kasa taji takun mu sai ta girgiza. So nake talakawa su ji tsoron mu, kamata yayi mu addabi kowa da yaki wancan mutumin ya hana. Dole mulki ya dawo hannuna domin mune muka cancanta."

"Karka manta jarmai yayi mutu, yanzun saura tsinbura, idan har muka yi hakuri lokacin da ya fada na zuwa mana"

Kallon madubin gaban shi yayi, bai san lokacin da ya dauki kofin da yake shan ruwa ya wurgi madubin da shi. Yana ƙara faɗin.

"Lokaci-lokaci lokaci lokaci! Yaushe lokacin zai yi ne?" Ya fada da karfi, dafe goshinsa yayi sannan ya kwanta.

**

Shekaru goma sha tara.

1789

Masarautar Sahil.

Masarauta ce ta suke tsakiyar sahara, masarauta ce da take da karfin mulki da ta tsafi. Musamman camfe sunyi imani da camfe.

Masarautar an wani gari ne aka ganta a wannan wurin da Alummomin ta, sun shafe sama da karninnika a wurin, basu tab'a fita yaki ba, amma kuma babu tsuntsun da ya isa ya gifta ta masarautar. Suna da wata gunki da suka sassaka shi da itacce me suna hil ita wannan gunki siffatar kamar mace ce da goyon daya, gefen wuyar ta kuwa kamar an sare ta, a duk bayan shekara biyar ana sadaukar da jinin wasu kabilu masu suna Na.

Wadannan kabilun sun kasance wasu shashi na larabawa makiyaya da suka yo hijira daga wata Alkarya da take tsakanin kogin Nile da kasar Habasha, kasancewar ana samun rashin zaman lafiya da kabilun yankin wurin. Cikin dare suka fada masarautar Sahil. Koda gari ya waye aka ga baki nan aka tafi masarautan inda aka samu sarki Arkhan aka gaya mishi. A lokacin sarki yana cikin matsanancin damuwan rashin da namiji.

Ana gaya mishi ya tura a kira bokan shi me suna zeela, kafin dan aiken ya iso bokan ya bayyana.

"Ka sani Ya mai Martaba, kukan ka ma shekaru arba'in zai kare ne da zaran ka samu daya daga cikin yan matan da suka yo gudun hijira, ka yi tarayya da ita kafin kusfewar rana da wata. D'igon ruwan da zai shiga jikin ta shi zai haifar maka da namijin duniya. Zaki kuma gamzaki wanda zai zama fasa taro. Idan aka samar da shi dole jinin uwar ya zama sadaukarwa ga Hil uwa mabada mana. Kafin nan bari

na gaya maka sawaye mutane nan nan. Su din mabiya wata addini ne masu dabi'ar dukawa. Sannan suna da wata baiwa na musamman na iya sarrafa maganin kowacce ciwo, sannan suna da wata irin karfin da ya fi na sihiri. Sadaukar da jinin uwar zai karawa masarautar mu karko da nisan kwana. Dan kuma zai kasance gaggarabadau. Sai dai tasirin su yana faruwa ne daga daren da rana da wata suka yi kusufe. Idan kuma namiji ya aure su, suna iya kara Mishi karfin mulki karshe mulkin yana iya dawowa hannun su, ba zan yarda da wannan yanayin ba shi yasa nake kallon Gara ka ajiye dayan su domin samun wannan babban rabo"

Kallon boka zeela yayi kafin ya bude baki yayi magana bokanya Tursi ta bayyana.

"Zeela me yasa kake aiki da jahilci? Ina gaisuwa Mai Martaba. Babu macen da zata haifa maka da namiji a cikin su, dan ko an haifa zai koma. Ita wannan macen da zaka sadaukar ba a haife ta ba, sai dai taurari sun tabbatar tana cikin su. Kafin nan a cikin matan a duba mace da take da alamar wata a jikin ta idan aka samu sai a fara kawo maka ita sauran mutanen ayi sadaukarwa da su. Domin idan ba haka ba zasu yi tawaye kuma zasu iya daukar kasada domin baiwar su bata kanannun mutane be."

**

"Shugaba akwai matsala anan" wani matashi ya faɗa.

Jinjina kai tsohon yayi tare da cewa.

"Amjad ka ɗauki ke su, ƙaddaran tana tare da su, ku bar wannan nahiyar ku tafi." Ya kalli wata karamar yarinya da take tsotsar hannu.

"Karka had'a su wuri guda, domin zasu iya bayyana baiwar su ka raba kan su. Idan ta kama bauta ce ma su. Ban shirya ganin tashin hankali"

Zana inda suke yayi sannan ya d'aga hannu yana addu'a, tare da yiwa Ubangiji kirari, wani irin duhu ne ya mamaye inda suke kafin ya shiga washewa. Babu mutumin da Yan matan.

Suna barin wurin dakarun sarki na zuwa aka kwashe su da karfin tsiya aka kai su fada, anan aka shiga duba su babu yan matan.

"Kai me farin gashi ina sauran Yaranka"

"Babu su iya mune"

"Ku sake dubawa, ko ku kashe su baki daya."

"Da haka kuka yi tabbas da yafi sauki akan mu bayyana muku inda sauran suke"

"Kenan kun san inda suke?"

"Bamu sani ba, amma mun san kana niman Kallabi."

"Tursi babu wani mafita?" Zeela ya tambaye shi.

"A sadaukar da jinin su amma ba dukkan ba, domin ba mamaki yan matan su kuma haifar masu irin wancan baiwar"

Haka suka wuce da mutanen a take aka yanka tsohon sannan aka watsa jinin shi ga abin bautar su hil. Kafin nan kuwa garin ya dauki wata irin hadari da ruwa lokacin guda..

Bayan shekaru sha tara.

Bincike suke baki dayan su bokanya Tursi take kafin ta d'ago kai tana kallon Sarki Arkhan.

"Akwai yiwuwar akwai dayan su a raye sai dai sun yi wata irin nisa na ban mamaki." Sake mai da kanta tayi tana cigaba da bincike jini ya shiga suka daga hancinta. D'ago kai tayi tare da cewa.

"Tafiyar shekara hudu zuwa biyar zai kai mutum inda suke, sai dai tauraro daya ne yake bayyana, daya yana boye. A cikin wannan yanayin cikar shekara biyar din nan wata da rana zasu samu kusfewa a cikin wannan yanayin Imma a kawo maka dayansu ta samu digon ruwan ka Imma ayi ra zubda jini domin nan da wani lokaci shekarun fuskarta rayuwa ce"

"A ina? Yaushe?" Sarki Arkhan ya tambaya a gaji burin shi magaji. Burin shi a haifa mishi da namiji,

"Idan har kayi hakuri hakan zai faru ne ta sanadin shekarun rayuwar macen da zata iya daukar haka"

Shiru yayi yana kallon su amma baya jin yana da rabon samun da namiji, kuma Sadauki wanda zai dauki mulkin kasar baki daya. Baya son ya rasa wanda zai gaje shi da karfin sihirin shi yana da y'aya mata babu adadin amma namijin yake nima.

"Kince daga nan zuwa Nahiyar shekaru huɗu zuwa biyar. A shirya yaki domin dauko ta" ya fada cikin izza.

"An gama"

**

Masarautar Gobir.

Yau kwana huɗu kenan ana niman dan dalago, sama da kasa babu labarin shi. Abin duniya ya taru ya dame Aminatu, tana zaune ta Zubawa kofar shigowa zauren ta ido, ga bayi mata sun yi jungum-jungum.

"Ayya Fulani ki saka wani abu a bakin ki mana"

"Taya zan yi hakuri bayan an nime shi an rasa" ta fada tana kuka.

Shigowar Mai Martaba da kwana uku kenan baya nan, ya shiga cikin zauren da Sallama. Mika mishi gaisuwa suka yi kafin kace me sun cika mishi gaban shi da abincin, sannan suka bar wurin. Mika mata hannu yayi ta taso, fashewa tayi da kuka. A hankali ya janyo ta jikin shi, yana me kallon ta, turaren da Innayoh ta saka mata yana ratsa hancin shi. Saka kan shi yayi a dokin wuyarta, ya shiga goga hancin shi, yana tambayar ta.

"Ke da waye?"

"Dan dalago ya b'ata" ta fada tana zubda kwalla, dumin kwallar yana ratsa jikin shi sabida saukar da yake a hannun shi. Juyar da ita tayi yana kallon yadda fuskar nan tai jajjur. Lashe bakin shi yayi a hankali ya kai bakin shi kan nata. Ya sauke mata karamin sumbata, lumshe idanun ta tayi kwalla na zuba mata.

"Baffa'm!" Ta kira sunan shi, tana me janye fuskar ta, a hankali ya mai da ita ya kwantar, yana kallon yadda take shirin bare mishi baki, juyawa yayi sannan ya mike. A shekarun shi yana bukatar abokiyar rayuwa, shi kuma matar da yake kallo tayi kankanta.

Fita yayi baki daya, sannan ya koma shashinsa.

"Ka kira min Galadima" ya fada a sanyayye,

"An gama"

Bayan wani lokaci sai gasu tare sun shigo.

"Allah ya baka nasara, gani nan"

Shiru yayi, kafin ya ce mishi.

"Ina bukatar wacce zata dauke min nauyin Aminatu."

"Allah ya baka nasara, kayi hakuri mana. Akwai alkhari a tarayyar ka da ita idan ka sako wata cikin al'amarin ku zai lalace. Kayi hakuri"

"Toh ya zanyi?"

Mikewa Galadima yayi, sannan ya kalle shi.

"Kai namiji ne, janta jikinka sakata a jikin ka zai saka kaji sauƙin wasu abubuwan, ka koya mata zama a jikin ka yadda kome nata zai tsayar da kai amma matukar ka sake taraba shimfida da wata haka zai kasance mata tashin hankali. Zai haifar da kishi idan har wacce zata zo ka mai da ita abar biyan bukata Aminatu zata wahala. Don Allah kayi hakuri"

Shiru yayi bai ce kome ba, kafin Galadima ya cigaba da cewa.

"Kai ka gaya min baka son ayi kishi me zafi a gidan ka kuma kana niman baiwa dan nasan ba aure zaka yi ba sai dai Kwarkwarah" haka Galadima ya gama maganar shi bai ce uffan ba. Har ya tafi.

Wa shi gari

Tura sako yayi a kawo mishi Aminatu kasancewar ranar Laraba ne. Tunda aka fadawa Innayoh, ta sakata a gaba tayi mata wanka, a wurin wankar take kallon kirjinta da kan dukiyar fulanin ta yake dan turo kai. Kasancewar ta daura mata mayafi, a saman jikinta. Goge mata jikin tayi sannan ta ce mata.

"Fulani idan Baffa'm ya tab'a jikin ki karki gayawa kowa kin ji, mutuwa ake idan kika fada, karki ji tsoro kin ji amma kiyi shiru da bakin ki" gyada kai tayi tana kallon Innayoh, haka ta gama shirya ta, sannan aka raka ta har babban zauren shi suka dawo, yana zaune yana rubutu. D'ago kai yayi ya mata murmushi. Ganin haka yasa

ta nufe shi ta zauna. Haka ya cigaba da rubutun shi, sannan ya tura mata wani katon tire dauke da kayan ciye-ciye.

A hankali take ci tana mishi magana, sannan ta tura tiren komawa gefe tayi ta dangwali tawada ta manna mishi a gefen kumatun shi inda ya lubb'a. Lashe baki yayi yana ci-gaba da aikin shi dauke fatar raƙumin tayi da yake rubutu a cikin shi ya nade can ta ce mishi.

"Baffa'm har yau babu dan dalago"

Ina zaki ga dan banza bayan ni da su waziri mun cinye dan banza

Abinda ya faru, duk yadda yabi sai ya lura dan Zomo dai ya hana shi samun hankalin ta, shine yasa Innayoh ta kama dan banza aka bawa Sarkin gida ya yanke aka gasa musu, ya haɗa da guzirin shi.

Tunawa da yayi shima cikin jimamin ya rungume ta, yana bata hakuri. Gudun kar amishi kallon zallamamme amma babu abinda ya isa hana shi samun matar shi, yanayin da yake samun kan shi yasa baki daya. Cikin wani irin shiririta ta fara kokarin zamewa a jikin shi tana wani irin yauki da kiriniya, tana wani irin zamewa kamar karkashi. Baki daya kamshin ta da wani yanayi me dadin Bala'i yana ziyarta yanayin shi na lafiyayyen namiji cikakken jarumi. Wanda ya san me yake yi kuma yasan waye shi.

A hankali ta d'ago kai tana kallon yadda ya lumshe idanun shi, hannunta, ta kai kan tawadar ta shiga zana mishi akan fuskar shi. Bude Idanu yayi akan ta..

"Ah" had'a goshinsa yayi da nata,

"Zan miki bulala"

"Kayi hakuri" lallubar hannun ta yayi tare da jifa yatsarta a bakin shi yana tsotsa yana me lumshe idanun shi.

"Baffa'm!"

"Hmm"

"Karka cinye min hannu"

"Hmm" ya fada bayan ya bude idanun shi kanta, zare yatsar yayi yana me sumbatar tafin hannun ta.

"Baffa'm! Wata rana zaka yi fushi da ni?"

Sosai ya ware idanu shi akan ta, yana kallon cikin idanunta, itama shi take kallon.

Fulani Aminatu ita zanen ƙaddara ba bawa keda ikon zata ba, ilahi yake zanata idan har akwai tafiyar Ƙaddara toh ba makawa sai na mai da ita sadaukarwar ƙaddara

A zahiri kuma murmushi yayi mata,yana jan kumatunta ya ce mata.

"A'a"

Mai da kanta tayi ta kifa a kirjin shi, tana jan shashekar kuka.

"Baffa'm!"

"Hmm! Fulani"

"Karka zama kamar Baffana kaji. Karka manta dani kaji"

Waye ya gaya miki marubuci yana rubuta labarin shi! Idan babu toh tabbas ba zan taba bada labarin mu ba

"Ina tare dake" ya fada mata,

"Baffa'm! Karka zama sarki domin akwai dodanin da zasu shiga cikin mu"

Ba halicci wani dabbar da zai shiga cikin mu ba

Kukan da bata san dalilin shi ba, bata kuma san hujjar yin shi ba, take yi tana karawa, har da shiga jikin shi, ajiyar zuciya ya sauke. Sakamakon jin tayi shiru, yana leka fuskar ta yaga tana barci, gyara mata kwanciya yayi sannan ya dauki kayan rubutun shi ya ci-gaba yana yi yana kallonta.

A hankali lokaci ya cigaba da tafiya, ya kasance duk sati Fulani Aminatu tana kai ziyara shashin sa, idan ta shiga tun ranar Laraba baza a kuma jin duri'ar ta ba, sai ranar asabar da yamma zata dawo shashinta, a lokacin idan ka gan yadda ta koma zaka yi tsammanin wani abu ake bata, sai kara kiriniya take, amma sabida sabo da tayi da zama a wurin shi dakyar Innayoh take lallabata, idan kuma taso sai ta tadda musu rigimar banza zata wurin shi.

A cikin wannan yanayin aka samu shekara daya da auren su, cika shekara daya yayi daidai da fara wani irin rashin lafiyar da ta fara, inda ta fara da wani irin abu a gefen wuyar ta, ya fito kamar bakin tabo.... Ba a lura da wuri ba sai da ciwon ya kwantar da ita, ana cikin haka wata Jumma'a aka wayi gari da mutuwar dabbobi cikin masarautar. ba a taba samun irin wannan annoban ba. Galadima ne ya nufi wurin shan iskar Mai Martaba.

"Allah ya baka nasara, ina ganin a fitar da Fulani Aminatu zuwa Sokoto ko za'a dace"

"Toh amma ina ganin kamar haka bai da alaka da mutuwar dabbobi nan?"

"Bana fatar haka"

"Allah ya baka nasara kazo" inji Sarkin gida.

"Lafiya?" Galadima ya tambaye shi,

"Fulani Aminatu ce"

Bai rufe baki ba, Mai Martaba har ya isa matakalar wurin shan iskar, kafin su zo tuni ya isa shashin ta. Tana kwance wuyar ta yayi jajjur, tabon bakin ya washe yayi ja.

"Baffa'm! Zan sha ruwa" ta fada a sanyayye, karban ruwan yayi ya bata tasha.

"Baffa'm akwai ciwo, cikina yana ciwo wuyana kamar wuta" ta fada hawaye na zuba a idanunta, d'ago yayi ya rungume ta, yana jin yadda jikinta yake firfitar da wani irin zafi. Janye kayan jikinta yayi bayan yayiwa Innayoh alamar ta fita, ya kwantar da ita ta shiga mata fifita. Dawowa wurin tafin kafarta yayi ya saka mata hannun shi yaji sanyi.

Tashi yayi ya lullube ta sannan ya bar shashin ta.

Fita yayi wurin Galadima, sun jima kafin zuwa dare suka fita daji, suka nimo saiwowi na bishiyoyi babu iyaka, aka kai cikin gida aka dake shi akan idanun Sarkin gida, aka dawo da shi nan aka hada mata magani kafin gari ya waye an yi mata wanka da shi. Sannan an bata wani tasha. Zuwa la'asar jini ya fara zuba bata, domin tana barci taji kamar tayi fitsari.

"Innayoh" ta kira ta.

"Na'am ranki shi dade,"

"Innayoh nayi fitsari"

Dubawa Innayoh tayi, taga kamar jinin haila ce, rangad'a gud'a tayi tana me fadin.

"Fulanina ta girma" kafin kace me labari ya karade cikin gidan, ana bada labarin girman Fulani, gyara ta Innayoh tayi sannan aka kwashe kayan aka kai wurin wanki. Innayoh da kanta ta wanke kayan.

Innayoh na fita ta kwanta, ko jimawa bata yi ba.

**

"Ban gane ba! Tsawon wani lokaci ka dauka da sanin haka?" Mai Martaba ya tambaye shi a fusace....

_____

Ina ga zan mai da posting din sau biyu a sati ko kuma kawai dan voting din ku gaskiya sai a hankali ku kara comments da Voting mana ko kuma mu hadu bayan sallah Insha Allah

#Mai_Dambu

[3/28, 11:49 AM] UmmuHabibah❤: KALLABI...!

A tsakanin Rawuna.

Na

Mai_Dambu

EWF

https://www.wattpad.com/1206974103?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=share_published

<Babi Na Sha Biyu>

"Kayi hakuri amma ba yadda kake zata bane, kuma ba mayya bace" shiru yayi dunkule hannun shi yayi ya daki bango.

"Kenan duk kokarina sai da kome ya faru?"

"Ina ga da zamu iya dakatar da wasu abubuwan ba mamaki kome zai iya tafiya daidai" inji Galadima.

"Yanzu meye makasudin bayyanar abin wuyarta?"

"Baiwa ce da ita, da a ce zaka iya kusantar ta ne, haka zai ragu ko idan ta samu ciki zata samu lafiya, domin kaifin abu." Wani Zubawa galadima idanu yayi kafin ya dauke daga kallon shi ya cigaba da abinda yake.

Tun lokacin ya saka idanu akan sannan shima da kan shi yake nima mata magani, duk da bata dauki kwanaki me tsawo tana hutun ta ba, amma kuma tayi kewar baffa'm. Har Innayoh ta mata magana.

"Ki rage yawan daukin da kike kar ya fahimci haka"

Shiru tayi sannan ta ce mata.

"Toh" a lokacin Innayoh ta shiga koya mata abubuwa da akanta, tana nuna mata yadda zata rike miji.

Ana cikin wannan yanayin watan azumi ya maka, har zuwa lokacin babu abinda ya nima daga Fulani Aminatu, a cikin gida kuwa kiri kiri Ajuji take jin daci akan Aminatu. Tun tana boyewa har ta fitar da kiyayyar ta.

Innayoh da wasu bayi da ita Fulani Aminatu, duk shirya abubuwan kyaututtuka suka shiga cikin gida da shi, dakin Gambo suka fara zuwa. Jakadiya na gaya mata ga Fulani Aminatu, ta mike da sauri ta faɗin.

"Lalle maraba da fara me farar Aniya" ajiye mata tiren bayi suka yi, sannan Fulani Aminatu ta zauna tana murmushi.

"Ayi hakuri ban samu zuwa da wuri ba, ga wannan na tarban azumi ne" ta fada tana Murmushi akan fuskar ta.

Murmushi Gambo tayi sannan ta ce mata.

"Idan akwai wata toh ba makawa taurarin da suke zagaye da shi masu haske ne." Ta fada tana kallon Innayoh.

Bude baki Innayoh tayi zata yi magana suka ji muryan Fulani Aminatu.

"Hmm! Daidaiton hasken shi karfin kusancin shi, mun barki lafiya"

"Haka ne, sai dai kar kusancin hasken ya rage karfin wani shaashi. Koda yake kwanaki naji labarin Fulani Aminatu ta girma har yanzu bata yi daidai da tsarin mulkin Sarki Bello bane? Idan yau ban cire ba a gobe akwai masu cirewa!" Kallon Innayoh Fulani Aminatu tayi tana kuma kallon Gambo.

"Laa karki damu, da alamu baki tab'a haduwa da shi bane? Tambaya da kyau. Waye Sarki? Baffa'm da kike gani shine Sarkin" kallon Innayoh ta kuma sannan ta kalli Gambo, da take dariya.

"Ta Yaro kyau take bata karko, da alamu abinda nake ji ma da gaske haka ne, Fulani Aminatu bata san me ya kawo ta masarautar Gobir ba, auren sarki kike Innayoh wannan ba kauna bace boye abinda yake daidai,Kanwata Nagode ayi azumi lafiya sai dai ki sani baki dayan mu, mun auri sarakuna ne a shekaru irin naki, idan kika sake lokaci ya karu baki same shi ba, kwarkwarah itace zata hanaki rawan gaban hatsin kamar yadda Kwarkwarah Ajuji ta min."

Idanun Fulani Aminatu ya cika da kwalla, amma sai ta mai da kwallar ta kwantar da hankalinta sannan ta kalli Gambo tace mata.

"Fulani Gambo, Nagode da tunatarwan ki. Ai na jima da sanin me nake a cikin masarautan, ni Mace ce kuma soyayyar sarki nake nima, ba baiwa bace ni, sannan ba karfin mulki nake nima ba, balle nayi tunanin bin shimfidar shi. Na barki lafiya"

An tashi da wani sabon al'amari ne na farin ciki, wanda tun asubar farko ake buga tamburan masarautar wanda dama dabi'a ce ko ace al'adun masarauta ce, ana bugawa duk lokacin da Sarkin Gida ya samu labarin wani cigaba ya faru a masarautan, ko za'a tarbi mai Martaba daga dawowa a yaki,.ko an samu karuwa a cikin masarautan, ko sarki ya kwana da Amaryan shi da yake girmama al'amarin ta, toh tun asuban fari ya sanar da Sarkin gida a kira Innayoh, tana shiga turakar Mai Martaba, aka ji ta rangad'a gud'a tare da fitowa da sauri tayi ta rangad'a gud'a, wanda ya farka da wasu bayin sashin Fulani Aminatu, kafin kace me an shiga had'a gagarumin biki, kamar yau ake bikin Sarki Bello da Fulani Aminatu, biki me sunan buki, wanda Innayoh ita ta wanke Fulani Aminatu da madarar saniya da aka amso daga can gidan gonar masarautar

Tun Fulani Aminatu tana kuka da noke mata, har ta sake jiki tana me kallon abinda ake mata, an gasa ta kuwa babu iyaka, sannan ta wanke ta tass ta rikota suka dawo dakin Mai Martaba, haka aka kuma nad'e shimfidar su, aka fita da shi, aka fara

terere da shi ana gayawa sauran Jama'a wannan shine dare mafi girma ga Mai Martaba Sarki Bello, daren da ya raya shi da Fulani Aminatu, wannan Al'adar ba karamin tasiri take da shi ba, a cikin masarautan kasar Hausa, domin da mace ta kasance ba budurwa ba, gara ta mutu tun kafin ta janyowa Zuri'ar ta kiyayya da tsanar masarautar domin zai fi sauki a tsinci gawar ta a yashe da ake ta shigo da wani abin kunya cikin masarautan.

Wunin ranar an yi shi ne cikin farin ciki da jin dadin domin shi kan sa sarki Bello a tarihi ba a tab'a samun Sarkin da ya yanta bayi babu adadi ba,.kamar shi duk da abin yayiwa wasu manyan fada ciwo, kuma da kan shi ya tafi har gidan kaso yayiwa wasu rifsinoni afuwa aka yafe musu laifin su, tare da musu gargadin kar su kuma.

Sannan an karawa wasu manyan bayin da suke tare da Innayoh matsayi wanda yasa kowa fahimtar cewa Fulani Aminatu mace ce ta musamman a rayuwar Sarki Bello. Kuma ta zama macen da babu biyun ta a cikin masarautan, wannan ya haifar da wani irin kishi da yawa me mugun ci rai, wanda har sauran uwaren gidan suka kasa boye damuwar su, kiri-kiri Ajuji ta fadi abinda yake ranta akan Fulani Aminatu, wanda haka yasa aka fara kananan magana, abin ka da gidan sarauta sai al'amarin ya zafaffa kamar dama jiran ake Sarki Bello yayi tarayya da Fulani Aminatu.

Zaune suke a babban turakar ta, Innayo ta saka mata abinci a gaba tana tsakura, kamar ba zata ci ba. Kamar zatayi kuka, idanun ta sun cika da kwalla tab. Jira kawai take su zubo,

"Kina nufin ba zaki ci abinci bane? Wai ma kina dauka al'amarin aure wasa ne? Maza ci ya kama miki jiki yadda zaki ji dadin daukar al'amarin mijinki da daraja."

Sharr sai ga hawaye dama jiran hanyar sauka suke, kuma dama an ce me shirin kuka aka wurge shi da kashin awaki. Shine ya faru akan Fulani Aminatu.

Cikin mugu mugun shagwab'a Fulani Aminatu ta kalle ta.

"Innayoh na fasa auren!"

Daga waje suka ji sallama yana faɗin.

"Takawar ka lafiya, giwa me tafiyar kasaita, an gaishe ka alfadari me kashin kudi, Barde namijin zaki, gamji me tuhon alkhairi, Angon Fulani Aminatu, Namijin gaske namijin duniya"

Bayan shi kuwa fadawa ne ke take mishi baya, fuskar shi tana fitar da wata irin murmushi me daukar hankali, duk inda ya gifta murmushi kawai yake, yana kara jin wani irin shauki da mulki yana kwasar shi.

Kalaman Galadima ce ta dawo mishi rai dazun da suka kebe ya zuba mishi ido kafin ya ce mishi.

"Ka dan bita a hankali, yarinya ce matuƙar ka kuma Binta da zafi zata razana kuma ba xata iya sake jiki da kai ba, a yanzu kake da damar kafa soyayyar ka me gardi"

Shafa wuyar shi yayi ta cikin alkyabar shi yana kallon sama, kafin ya shiga yar karamar harabar sashin Fulani Aminatu, sannana aka bude mishi kofar. Manyan mayafan da aka saka a tsakar zauren yayi ta d'agewa har ya isa bakin kofar da take, ya fahimci tana wurin ne, Sabida bayin ta da ya gani a kofar dakin dan haka ya shiga cikin da sallama.

A wani irin sukwane ta d'ago kai tana kallon shi, kafin ta sauke da sauri. Hannun ta yana rawa. Kwalla ne ya cika mata Idanu,

"Barka da zuwa Mai Martaba." Innayoh ta gaishe shi,.tana kowa gefen can.

D'aga mata hannu yayi, sannan ya zauna yana fuskar ta Fulani Aminatu, da take kallon Innayoh idanun ta yana cika da kwalla. Ko nace yana zuba, da sauri Innayoh ta fita, shi kuma ya zauna yana kallon ta, dan wauta sai ta fashe da kuka tana kiran Innayoh.

"Innayoh!!"

Kallon fuskar ta yayi, wanda suka bayyana tsoron ta ƙarara.

"Mmmm" ya sake murmushi me sauti yana kallon yadda take kara diriricewa hadi da shashekar kuka.

"Toh meye na kuka? Ni ne baki son gani na fita?"

Ya tambaye ta yana kallon yadda hannun ta yake rawa. Girgiza kai tayi.

"Toh me kike so?"

"Zan tafi wurin Innayoh, tsoro kake bani" a hankali ya cire alkyabbar shi, sannan ya zare rawanin ya kura mata ido, yana me ajiye kayan dukka a gefen shi, riko hannun ta yayi yana kallon yadda jikin ta ya dauki rawa, ba wai zai mata wani abu bane, amma baki daya yanzun ya rigada ya ji dadin ta, ba zai iya awa daya bai ji ta a jikin shi ba, dan haka ya dauke ta cak ya daura ya a saman cinyar shi, yana me sake wata irin ajiyar zuciya. Kuka ta saka tana me ƙoƙarin sauka a kan cinyar shi.

Kifa kan shi yayi a bayan ta, yayin da ya zura hannun shi cikin rigar ta, cikin kulawa da tattalin irin ta mazan da suka yarda da kan su, ya shiga latsa albarkan jikinta,

yana hura mata iskar bakin shi a dokin wuyarta. Bata tayi shiru tana sauke ajiyar zuciya, namijin gaske, sai gashi lokaci guda ta b'ata shiru, da wannan damar ya shiga wasu shafuka na musamman a rayuwar su, ya shiga nuna mata shi din fa ba na yau bane yana son ta daga nan har karshen rayuwarsa. Bata tai shiru, malamin su kamar zai yi Hauka domin baki daya ta samu gyaran jiki na kwana biyu, dan haka da wayo da dabara, ya sake angwancewa a dakin ta, sai da yayi da gaske domin yadda take kuka da niman gayawa duniya yana tare da ita yasa shi toshe mata baki da na shi, haka yasa lokaci guda, ya shidar da ita sai da ya samu nutsuwa sosai kamar ba shi ba, sannan ya kyale ta, yana me daurata a saman kirjinn shi, kawai hakuri yayi dan wallahi da turakar shi ce take yau ba zai kyale ta ba, sai ya shan ye duk wani ruwan da yake jikin ta, amma ba damuwa zai reni soyayyar shi a hankali yadda duk duniya babu me ikon shiga birnin su.

A hankali mai Martaba yake samun kafa gwamnatin shi, ta yadda sai da ya budewa Fulani Aminatu idanun ta, ta zama cikakkiyar mace me hankali da nutsuwa, wanda baki daya masarautan ana mamakin sauyin ta, domin a da can an santa da wasu abubuwan kamar shjga cikin bayi ayi ta hira, toh yanzun babu sai dai su shigo shashinsa su mata hira, a da can an san ta da yawan fara'a toh yanzu babu fara'ar kamar da, sai wani irin kamewa wanda ya haɗa da girman aure da ya shige ta, wannan yana cikin dalilan da yasa Innayoh take kara samun daraja a wurin Mai Martaba Sarki Bello, domin duk wani girma da daraja yana samuwa ne ta sanadin Innayoh, hatta sauran matan gidan sun san da haka kuma ba karamin faduwa bane a gare su, da farko basu zata Innayoh zata iya zamewa Fulani kariya haka yasa duk sharrin su, da fitinar su baya isa gare ta, sai dai ya tsaya a kansu, hatta manyan mata bayi suna matukar shakkar innayoh, kuma ba kome bane dabi'ar mutanen kirki ne matukar zasu rike gaskiya kowa tsoron su yaƙe, ana shakkar su.

A hankali kwanaki yana tafiya, Mai Martaba Sarki Bello ya makalewa Yar Kwailar shi, wato Sarki Bello irin mazan nan ne da ake kira a turance (lover boy) domin a cikin lokaci ƙalilan ya nuna ko a fada Fulani Aminatu ce rabin rayuwar shi.

Ta kai ta kawo ko zaman fada sai da ya wargaza tsarin zaman shi, a madadin ya fito tun safe sai gashi ya dawo da zaman maraici, wannan abun ba karamin dadi yayiwa Galadima ba, sannan yana tashi ba zai kuma sauraron kowa ba sai gobe, daga cikin manyan fadar da haka ya basu haushi, akwai Chiroma, akwai Wanbai, akwai Yarimar Gobir, amma daga Waziri har Galadima garin su gabar domin babu abinda yake basu haushi sai farin ciki.

**

Masarautar Gombe

Fulani Kilishi.

"Jakadiya me yake shirin faruwa ne? Jiya na kai ziyara wurin boko ya nuna min Aminatu tana cikin da nutsuwa abinda bana fatan haka ya faru!" Ta fada cikin matsanancin b'acin rai.

Cikin kaskantar da kai Jakadiya Jebu ta ce mata.

"Aikin da aka yi sarki Bello ya karya, abinda nake jin kar muyi wani abu" Jakadiya Jebu ta faɗa.

Shiru Fulani kilishi tayi kafin ta ce mata.

"Ya bani wannan aikin bana son yarinyar ta rayu cikin aminci da salama"

Murmushin mugunta da kaguwa domin jin wani irin tuggu aka shiryawa Fulani Aminatu.

"Uwargijiya ta bani umarni zan cika miki"

"Ki nimo min, budurwa sa'ar Aminatu ki kawo min ita, amma dole ya zama a siritacce."

"An gama uwargijiya ta, duk abinda kike bukata haka za ayi," Jakadiya Jebu ta faɗa cikin farin cikin da jin dadi, sannan ta mike ta fita da sauri, bin bayan ta Fulani kilishi tayi da muguwar murmushi, wanda ya kara munana fuskar ta, kasance duhun zuciyar ta ya kara tsammari.

**

Masarautar Gobir

Zaune take a takure, kunyar yadda yake shiryawa a gaban ta, yasa ta sunkuyar da kai, takowa yayi cikin wani irin salo, ya dan zauna a saman gadon, sai tattare mayafin da suka rufa da shi yake, taki yarda ta kalle shi.

Zama yayi a gaban ta, ya riko hannunta yana murmushi ya saka a tarin kwanjin da yake kirjin shi, yana murmushi.

"Idan baki kalle ni ba wacece zata kalle ni da soyayya....

End of page 15

T

akabbalahu Minna waminkum _Truly, Allah is full of kindness. The most merciful towards mankind (Q2: 143). May you and your family enjoy His mercies forever. May He give you a key to every closed door, light for every darkness, joy for every sadness and answer all your supplications now & forever Amin.

Edi Mubarak

Mai_Dambu...

[5/14, 2:22 PM] Pearl crystal: KALLABI....!

A Tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

BABI NA SHA SHIDA

D'ago fararen idanun ta, tayi tana kallon shi cikin sanyin jiki, a hankali ta zare idanun ta cikin na shi, tana me wasa da mayafin da yake kare mata jikin ta.

A hankali ya zare mayafin albarkatun kirjinta suka bayyana, d'ago kai tayi tana son kallon shi amma yadda yake mata wasu abubuwan yasa kunyar shi kara turnike ta, cikin kulawa ya d'ago habb'atar ta ya ce mata.

"Ko baki son na fita fada ne?" Da sauri ta d'ago kanta tana kallon shi.

"Toh gaya min me kike so?" Ya fada yana sumbatar hannun ta, zuwa yatsun hannunta da suka sha lalle.

"Hmm" ta ce tana girgiza kai, a hankali ya kai kan shi wuyar ta ya sumbata, yarrr tsigar jikin ta ya mike, bata san lokacin da ta kai hannun ta wuyar shi ba.

"Kina son na cigaba ne?"

Da sauri ta dauke hannun ta, tana zare ido.

"Toh me kike so?" Ya kuma tambayar ta, bayan yayi mata rumfa da fadadden kirjin shi, yana me janye mayafin da take rike da shi, sumbatar goshinta ya fara har zuwa kirjinta, jan mayafin yayi ya rufa mata, sannan ya mike yana yar dariya, saka kayan shi yana kallon yadda ta rufe idanunta.

"Baffa'm!"

Bai kalle ta ba, amma hankalin shi yana kanta kacokan.

"Ina jin ki"

"Hmm dama yaushe zan je gombe?" Juyawa yayi ya kura mata ido, shekara kusan hudu bata tab'a tambyar shi ba, yau ta bude baki ta tambaye shi. Yayiwa kan shi adalci kuwa. Samun kan shi yayi da zama yana me kallon ta.

"Kunyi magana da Innayoh ce?" Ya tambaye ta,

Girgiza mishi kai tayi sannan ta ce mishi.

"Allah bamu yi magana da ita ba, nice dai na tambaya da kaina" ta fada mishi haka tana wasa da zanin ta.

"Toh zan duba" d'ago kai tayi tana kallon shi,

"Allah ya baka iko" yadda tai maganar shi kan shi sai da burge shi.

Haka ya gama shiri tsaf sannan ya kalle.

"Zan je na dawo nasame ki ne? Ko zaki koma wurin ki"

"Duk yadda kace haka xan yi"

Murmushin farin ciki yayi sannan ya shafa gefen fuskarta, yace mata.

"Toh ki jirani kin ji"

"Toh, Allah ya dawo da kai lafiya"

Ta fada tana me ƙoƙarin sauka a shimfidar su, cak yayi sama da ita sai da ta ja wani irin numfashi.

"Matsoraciyar yarinya" tura baki tayi tare da cewa.

"Baffa'm kullum daga kace min matsoraciya sai ka ce min raguwa kawai, ko sarauniyar raki me yasa kake gaya min haka?"

Murmushi yayi mata me sauti.

"Ina magana kana min dariya?" Ta fada cikin jin haushi.

Yana shigar da ita ban dakin ya ajiye ta akan wani dutse da ake zama a ban dakin, ya ce.

"Duk ranar da kika daina kuka a shimfidar mu ba zan kuma kiran ki raguwa matsoraciyar yarinya me raki ba" ya fada yana barin ta a ban dakin. Murmushi kwance akan kamilar fuskar shi.

Yana fita ta shiga tura baki gaba tana faɗin.

"Ba dole mutum yayi kuka ba. Abin kullum kamar abinci aka mai da mutum"

**

Rugar bayan gidan gona

Kallon Dabbobin Bingel tayi tana jin a ranta matukar ta cigaba da zama a nan rabon ta zai wuce ta, dan haka ta juya tana kallon rugar su, tasan abu me wuya ne wani ya ce zai je masarautar Gobir niman ta,amma a wurinta damar da yafi kowanne girma ta samu na tserewa izuwa ƙaddaran ta.

Tafi Fulani Aminatu kyau, tafi Fulani Aminatu sura me kyau, ta fita cikar halitta, sannan zata iya kome domin bawa Sarki Bello farin ciki, sai dai a lokacin da take wannan nazarin Allah ya gama na shi ikon, bayan ta gama zagaye da kiwon ta, ta koma gida anan ta samu labarin ai Jauro ya bada auren ta ga Dan kanin shi, Jabbu, da mugun gudu ta shiga ɗakinta ta rufe kofar, tana kuka baki daya ta rasa ina zata saka rayuwarta, dan haka sai da ta zauna a wurin har dare ya raba, sannan ta fito daga cikin dakin ta, ko tsoron daren bata yi, ta bar gidan tare da gudun ƙaddara.

A tunanin ta farin cikin da Aminatu take ciki, ita ya dace da samun su ba Aminatu ba. Taya kamar Aminatu zata zama matar Sarki ita kuma da danginta suna bautawa masarautar Gobir. Zata tafi kodan ta samuwa ƙabilar ta abin dogaro ba zasu kare a bayi ba. Wannan shine dalilin da yasa ta ganin itace da damar da Fulani Aminatu ta ke ciki.

**

Da gayya taki motsi dan kar ya ce idanun ta biyu, shi kuwa babban abinda ya shigo da shi dakin daban, amma ganin yadda ta kwanta, kamar wata mage, sannan mayafin da ta rufe jikinta ya fitar mata da asalin kugunta zuwa mazaunin ta, dan ma baya barin ta. Ta huta amma Fulani Aminatu mace ce da ake kira mace, irin mata kalagun nan ne daga sama a cike yake sakamakon murzan da yake samu, haka ma K'ugunta shima yana bayyane da nashi kiran, doguwa ce me wata irin karuwar jiki, irin jikin nan nan da kome kankantar ado yana iya tafiyar da rayuwar wasu. Dan haka ya zauna tare da ɗaukar alkalamin shi da yake rubutun shi na ajami ya fara rubutun labarin su da yadda yake jin kome a kanta, bai tab'a ka manta yin zane ba sai gashi haka kawai yana kallon ta yana zana ta a jikin wani farin fata, ta

shi yayi ya fita zuwa waje, yana goye da hannun shi a baya. Da sauri sarkin gida ya iso yana kallon shi ya ce.

"Allah ya baka nasara, dare ya fara rabawa!"

Shiru yayi na wani lokaci, kafin ya ce mishi.

"Ina jin wani abu a raina ne, ina son a niman min allin da ake zane da su daidai wanda zan iya zane a fatar bauna da fatar rakumi. Maza ina jiran ka"

"Allah ya baka nasara an gama" ya fada tare da juyawa da sauri ya bar wurin, har zai shiga sai ya hango wucewar wasu mata, bai wani damu ba. Ya ci-gaba da tsayuwa can sai yake jin babu dad'i kawai ya gwada haurawa saman wurin shan iskar shi, yana zagaye wurin, hango mutanen yayi suna hakka rami, ganin haka yasa shi, sauka da sauri tare da kiran masu tsaron kofar shi, suka nufi wurin. Jakadiya Rama ce da wasu bayi maza.

"Me kuke yi?"

"Shi kenan mun shiga uku" Jakadiya Rama ta fada da sauri tana kallon kasa.

"Me kuke yi a wurin nan?" Shugaban dakarun da suke tsaron kofar mai Martaba ya kuma daka musu tsawa.

"Me kuke yi anan? Ko baku ji ne?"

"Allah ya baka nasara, a yafe mu tsautsayi da asara ya kawo mu binne..." Sai kuma tayi shiru.

"Ku tafi da su" haka suka tisa keyar su, suna tafiya yasa aka tone ramin, aka ciro abinda aka binne, sannan ya koma shashinsa, da abinda aka tono yana mamakin yadda Jakadiya Rama ta zama haka ? Duk akan raba da matsayin da take ne ko kawai amfani aka yi da ita? Wannan ce tambayar da ya kasa amsawa, kuma yaji ran shi ya kuma b'aci dan haka ya wuce sashin Fulani Aminatu, yana isa aka bude mishi kofar, ya shiga da sallama Innayoh ta amsa kishi cikin girmamawa, tana me risina mishi, a sanin ta dai Fulani tana wurin shi, toh ko wani abu ya zo dauka? Ta tambayi kanta.

"Ko akwai wani abu ne a tsakanin ku da Jakadiya Rama ce?"

Ya tambaye ta, yana me kura mata ido, maganar ya zo mata bazata dan haka a dan rude ta ce mishi.

"Mu kuma? Toh me zai hada mu? Sai dai ko akan.."

"Akan me?"

Shiru tayi domin basu tab'a magana irin haka ba, dan haka tayi shiru, sai da ya kuma tambayar ta?

"Akan me?"

"Jakadanci ba!" Ta fada a matukar firgice,

"Toh" ya fada sannan ya juya ya bar sashin.

Koda ya koma, ya samu Sarkin gida da Galadima.

"Lafiya?"

Suka tambaye shi,

"Hmm! Ga shi can ban san me ke damun mutanen gidan nan ba, Rama tana tadda min husuma kuma ina kokarin dauke kai daga gare ta, amma bata lura da haka, shekarun ta da kuma Surikin ta sarkin Yaki nake dubawa, ba wai ban san me nake yi ba, matukar aka samu sunan Fulani Aminatu a cikin wannan abin da suka binne tabbas sai na hukuntatta mafi girma da daukaka a cikin masarautan nan" yana gama fadar haka ya shige abin shi, bai kuma magana ba. Koda ya shiga cikin tsayawa yayi yana kallon Fulani Aminatu da take kwance mayafin rufuwar da yake yana da tsantsi, ya salube daga jikinta ya sauko har kan cikin ta, dukiyar Fulaninta suna tsaye cur-cur, lumshe idanun shi yayi kafin ya kauda kan shi, ya nufi ban daki yayi wanka, ya jima zaune kamar bai da abinda yi, a hankali ya fito ya haura gadon ya kwanta.

Yana sauke ajiyar zuciya, bayan ya janyo ta jikin shi. A hankali ruwan da yake jikin shi ya shiga gangara jikin ta, a matukar sanyayye ya juya yana fuskar ta shi.

"Baffa'm! Meke damun ka naji kirjin ka yana bugawa da sauri da sauri." Tana maganar ne amma idanun ta a lumshe kamar me magagi. Shafa fuskar ta yayi zuwa wuyar ta, sannan ya saka bakin shi a habb'atar yana tsotsa, shigewa jikin shi tayi sosai tana sauke ajiyar zuciya a kan fuskar shi.

"Baffa'm!"

"Aminatu! Ina jin kamar zan rasa ki ne shi yasa yake bugawa da sauri da sauri" ya fada yana me sumbatar goshinta.

Gyara kwanciyarta tai a jikin shi.

"Babu abinda zai faru" ta fada tana sauke ajiyar zuciya a karo na biyu.

Gyara mata kwanciya yayi a jikin shi, sannan ya lullube ta.

*

Tunda ya shiga ya bar su, suka yi shiru sannan suka nufi wurin Dakarun suka tambaye su, keken faruwa, nan suka gaya musu sannan suka nufi wurin da aka ajiye shirgin, basu yi gangamin tabawa ba, sai dai kuma suna barin cikin gidan sarautar aka samu wani bakin labari. Na mutuwa Jakadiya Rama da bayin nan, kiran sallah farko ya d'aga shi, kan shi na sarawa a hankali ya janye ta a jikin shi ya shiga ban daki yayi wanka da alola. Sannan ya nufi hanyar masallaci. Kus-kus din da dogarai suke yi ne ya ja hankalin shi bayan an idar da sallah ne yake jin labarin mutuwar Jakadiya, idan ran shi yayi dubu sai da ya b'aci. A fusace ya nufi fada cikin abinda bai wuce rabin sa'a ba sai ga dattawan fadar sun Bayyana baki dayan su, basu tab'a ganin b'acin ran shi ba.

"A kira min sankira" shine me tsaron kofar gidan yari.

"Allah ya huci zuciyar zaki, Allah ya baka hakuri da afuwa" ya mike bayan ya gama fada, sannan ya nufi can gidan yarin da yake cikin masarautan.

Bayan kamar minti goma sai gasu, irin manyan mutane nan ne jibgege kamar kututturen bushiyar loko (wato bishiyar kuka) zuwa yayi ya zube.

"Taya aka yi Jakadiya Rama da mutanen da aka kama suka mutu?" Waziri Zakaria ya wurga mishi tambaya?

"Allah ya baka nasara, wallahi jiya bana kofa. Sakamakon mai dakina tana bisa gwiwa" a zafaffe sarki Bello ya kura mishi Idanu,

Sankira waye a kofar jiy" Galadima ya wurga mishi tambaya.

"Allah ya taimaki Galadima, Sanda ne a bakin kofar jiya"

"Toh maza a tawo da shi" inji Waziri,

"Allah ya huci zuciyar ka"

"Hmm! Maraba gasashe kura taga bakin jaki!" Inji Yarima Yakubu.

A yadda Sarki Bello yake ji zai iya sakawa A bawa Yarima Yakubu kashi dan haka ya nuna shi da yatsa, sannan ya mishi alama da ya bar fadan.

Cikin rashin mutunci da ya saba ya bude baki zai magana.

"Kai!!!" Ya daka mishi tsawa, take dogaran fadar masu fushi da fushin wani suka harxuka, kuma daman haka suke jira suke kawai sarki ya d'aga murya su kaddamar maka, an hore su ne da hakan koda dadi ko ba dadi kullum cikin fushi da fushin wani suke....

Ga bikin zuwa babu zanin daurawa. Eh TOH ina goron sallah na□□😆😉 idan babu tabbas Karku saka rai da posting gobe sai kun bani happy sallah na

More page more comments da vote □

@Mai_Dambu

[5/14, 2:22 PM] Pearl crystal: KALLABI..!

A Tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

https://www.wattpad.com/1222513643?utm_source=android&utm_medium=link&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=Mai_Dambu&wp_originator=7gnb3MI4WrBFYo4f8bqXOdMGqUuyCCYOsQ3xzd6ZxRZnZQ9AhBeGnIaAs4ln%2BVjddA%2BcfxIRyRqhNy2iy%2FNjaq6sJpfG%2FrdMUtx%2FOpTdvw66ELKl7FBy94kcUdszKKf2

BABI NA SHA BAKWAI

GAISUWARKU CE A WANNAN SHAFIN MASOYAN KALLABI NAGODE SOSAI

"Fita aka ce maka, me yasa baka da mutunci ne? Maza fita mara hankali daga yau an dakatar da kai shiga harkokin fada!" Inji Waziri Zakaria, shigowar sanda da dogarai, yasa Sarki Bello kura mishi Idanu.

Masu iya magana sun ce mara gaskiya ko a cikin ruwa yake gumi yaƙe, abinda ya faru kenan ga Sanda domin yana ganin shi a gaban sarki Bello ya fashe da kuka.

"Kai yi min rai ja gafarce ni, na tuba wallahi ni na kashe su" lumshe idanu sarki Bello yayi sam bai gamsu da Hujjar Sanda ba, dan haka ya kura mishi Idanu, kafin ya janye daga kallon shi, lashe bakin shi yayi yana kallon yadda yake gumi.

"Kana da iyali?" Ya tambaye shi, kafin ya cigaba da cewa.

"Ku mai da shi, bakin aikin shi a tabbatar da an yi suturar Jakadiya Rama"

Daga haka ya mike tare da barin fadar.

"Ban gane abinda Bello yake nufi ba, shin ya bar Sanda ne?"

Mikawa Galadima yayi sannan ya ce.

"Duk diya nai da ya hana uwatai kwance ai shima ba zai kwana ba" yq kad'e alkyabar shi yayi gaba.

"Shawara ta rage ga me shiga rijiya Imma ya hwada da kai Imma ya dira bisa sawaye nai"

Shiru fadar ya dauka domin maganar gaskiya magana suka gaya musu, amma toh duk wanda zai ji haushin wannan abin toh tabbas yana da hannun cikin abinda ya faru, dan haka sai gashi sun sani shiru babu wanda ya kuma tankawa.

Haka aka tafi Jana'izar Jakadiya Rama. Bayan an gama aka dawo fada, inda aka yi ta kanannun magana aka. Sarki Bello ne yasa a kashe Jakadiya, wanda ba haka bane tsabar sharri ne irin ta mutane.

*

Shiru wurin ya dauka, kafin Galadima ya ce.

"Ina ga an rufe daki da barawo fa, domin duk wanda ya kashe Jakadiya Rama akwai wani abinda ya boye ne, haka kawai ba zai kashe ta ba, dan haka ina da yakinin anyi haka ne dan rufe."

Murmushin gefen baki Mai Martaba yayi yana kallon littafin hannun shi.

"Eh toh kana da hujja?" Ya tambaye shi.

"Bani da ita, amma yadda aka kashe Jakadiya ya isa ya tabbatar da hujjar da nake da ita, sannan idan ka dubi yadda ake gararanba da zancen dole ya tab'a kowa naka" inji Galadima,

"Bana jin haka kuwa kawai ina nazarin rayuwar al'umma ta ce"

Daga haka ya mike tare da nufar inda tukwanen shuka suke yana me tsayuwa wurin.

"Bana jin akwai wani kwanciyar hankali a cikin gidan nan. Ina son na dauki Aminatu zuwa Gombe tafiyar makwanin ne"

"Allah ya nuna mana" galadima ya fada yana me mikewa yana cewa.

"Amma ba zaka bar masarautar nan yanzun ba sai ka gyara wasu al'amarin, domin"

Juyawa yayi yana kallon shi, hango Fulani Aminatu yayi tana tsaye a bakin kofar shigowa ganin Galadima ya sata mai da takalmin ta zata juya.

"Shigo" ya ce mata, yana kallon ta.

Girgiza kai tayi zata juya tana kara jan mayafinta, dokin rufe fuskar ta.

Juyawa Galadima yayi wanda yayi dai-dai da juyawa ya itama, bisa tsautsayi kawai ta tafi baki daya.

"Aminatuuuuuuu" ya kira sunan ta da karfi wanda idan ba wani ikon Allah ba, kaf masarautan babu wanda bai ji kiran ba.

Da mugun gudu, ya nufi kofar ya samu ta gungura can sai kokarin tashi take amma ta kasa, da sauri ya isa tare da d'aga ta yana kallon yadda goshinta da hancin ta da suke zubda jini.

"Baffa'm! Ba wani ciwo bane fa" ta fada a wahale, saka farar alkyabbar shi yayi yana goge mata hanci, kafin ya dauke ta, dan har dakaru sun fara zuwa, ya nufi tarakar shi da ita. Wannan dalilin ya sa kowa ya kama gaban shi.

Ajiye ta yayi a bakin gado yana kallon yadda take lumshe idanun ta, tabbas yasan tana da hakuri da juriya, bai zata na yau zai zarce na kullum ba, dan haka ya shafa gefen fuskar ta yana kallon yadda take ajiyar zuciya.

"Sannun kin ji"

"Naji tsoro sosai" mikewa yayi ya nufi ban daki ya dauko ruwa a wani tassa, sannan ya zo ya wanke mata fuska da hanci, kafin ya zuba mata ido.

"Me kika zo yi a wurin?" Hawayen da take dannewa ne, ya shiga saukowa bakinta yana rawa ta ce mishi.

"Me yasa aka kashe Jakadiya?" D'ago kai yayi ya kura mata ido, kafin ya mike tare da nufar ban daki ya zubda ruwan sannan ya fito ya nime wuri ya zauna. Kallonta yayi na wani lokaci kafin ya ce Mata.

"Waye ya turo ki?"

Yadda yayi maganar babu wasa ko sassauci, yasa ta d'ago kai ta ce mishi.

"Babu"

"Toh daga yau kar na kuma jin kin shiga harkokin masarautar nan kin ji?" Hawaye sharrr yake sauka ta ce mishi.

"Naji" kallon kofar dakin yayi tare da cewa.

"Nasan Innayoh tana jiran ki je ki" mikewa tayi, zata fara tafiya amma ina ta koma ta zauna, tare da rike kafarta. Kuka ne ya kwace mata tana yarfe hannu.

Kai hannun shi yayi samar kafarta, yaga yadda wuyar kafar tayi fushi.

A hankali ya tashi ya fara dauko kayan aiki da kan shi ya dauko wani abu ya saka mata a bakin ta, sannan ya koma wurin kafar ya ja, wani irin ihu ta sake amma sabida abin bakinta ya hana a ji ihun, tana kuka tana kome ya ja kafar sai da ya cire gocewar, sannan ya mike yana me daukar ta cak ya nufi sashin ta da ita, akan idanun Ajuji da ta zo wucewa ta hango su, kura musu ido tayi babu laifi sai dai cutar Hassada ta hanata hango iyakar su, gani take kamar shigowar Fulani Aminatu gidan zata iya yaɗuwa tayi yabanyya.

Kwafa tayi tare da barin wurin da bayin ta.

**

Bayan wasu makwanin kamar biyar Sarki Bello ya shirya tafiya zuwa garin gombe, tare da Innayoh.

Yadda Fulani Aminatu take murna ba zaka taba tsammanin zata yi shi ba,ko ya aka yi dai dole tayi daukin zuwa ganin gida, dan haka aka shirya dakarun na musamman tun daga masarautan har zuwa wasu manyan masarautu kama daga na kano, Sokoto, Hadeja, Bauchi har zuwa gombe. An shirya tsaf ranar Laraba suka bar masarautan inda ya barwa Galadima ajiyar garin shi baki daya, suna barin masarautan Bingel tana shiga masarautan. Dan haka aka samu saba'ni a tsakanin su basu ga juna ba ma,

**

Tun daga lokacin da ta shiga masarautan ta fahimci ashe kuskuren ƙaddara ce ta barota da gida, domin masarautan cike yake da mugunta da zalince, musamman da aka fahimci sarki Bello baya kasar, sannan shi kan shi Galadima bai san meke tafiya ba, wani abinda yasa aka kasa cimma Galadima sabida shima takadarirran mutum ne, Hatsabibi ne na gayawa mutanen gari, jan wuya ne da ya kware a rashin mutunci, kuma abinda ya sa yake biye halayyar shi amincin da ke tsakanin shi da sarki Bello, shi yasa bai cika shiga damuwan kowa ba, da kuma Allah ya sa aka wurge shi da rikon kwarya, sai ya fidda hakikanin gaskiyar shi, d'aga musu kafa da Sarki Bello yake yi shi ya ce bai iya ji ba, koda Yarima Yakubu yaso mishi iskanci

rufe idanu yayi yasa aka bashi kashi, ya kuma tabbatar mishi an haramta mishi shiga harkokin masarautar Gobir har abada, idan kuma ya sake ya shiga toh ya kwana da sanin sai ya sheka lahira.

A inda Bingel take, shashin Ajuji aka kaita a nan kuwa ganima Yakubu yake diban mata da yan mata babu ruwan shi, koda Galadima yaji labarin haka ran shi ya b'aci dan haka ya saka aka kamo mishi ya kubu yasa Sarkin bulala ya zane shi, kuma ya saka aka raba bayin a cikin wadanda aka raba har da Bingel inda aka kai ta gidan Chiroma.

**

A cikin kwanaki biyar da suka bar masarautan yana cikin kwanakin da Aminatu ba zata tab'a mantawa ba, domin ya ajiye sarauta bawan Allah nan ya shiga bayyana kaunar shi, kamar zai cinye ta, haka kawai ma a ranar na shida da barin su masarautan ya ce a yada zango, bawan Allah nan tunda ya fito yayi Sallah ya koma dakin ya shiga turmushe yar mutane, Dakyar ya fito sallah magariba da isha, ai kuwa yana komawa ya shiga dasa bama-baman kaunar shi, itama mara kunya ta saba da halin shi, haka take amsar shi a duk lokacin da ya bukaci haka, wani irin mahaukaciyar kauna sukewa juna kamar zasu cinye kan su, har suka isa masarautan kano, a nan ma sai da Sarkin Kano yayi ta Mishi hannun ka me sanda, kafin ya kyale yar mutane.

Haka suka yi ta sauka a masarautu daban-daban har Suka iso masarautan Bauchi. Kwanan su biyar a Bauchi, sannan suka nufi masarautan gombe, sun bar bauchi sosai har sun isa dumduma, suka yi karo da gawarwakin mutane, kuma da alamu fatake ne, dan haka basu yi yunkurin wani abu ba, sai da suka gaya mishi, da kan shi ya fito yana kallon su, daya bayan daya. Kafin ya shiga juya da sauri dake tsakanin keken dokin su da inda suke akwai tazara, hango wani gawurtaccen zaki yayi ya nufi keken dokin su....

End of page 17

Barka dai □□ lemme park my wahala go domin gaskiya zan ajiye labarin nan na fuskanci gaskiya....ba kome ba vote sai kace gantalaliyya ♀

Mai_Dambu

[5/14, 2:22 PM] Pearl crystal: KALLABI...!

A Tsakanin Rawuna

EWF

BABI NA SHA TAKWAS

"Kai!!!" Ya fada da ƙarfi amma ina har zakin nan ya samu damar bangaje keken dawakan da suka gan shi a fusace suka tsinke domin tsira da rayuwar su.

Kamar wani aikakke domin burin shi bai wuce yayi ta wasan tamola da keken ba, har ya kai ga ya fasa cikin ya zakulo bil adam din da yake cikin keken ba, sai dai kash! Ihun sarki Bello ya tsayar mishi da kome, a fusace ya juya ga sarki Bello da ya ke tunkarar shi gadan-gadan, ohoho faduwar gaba asarar ragon maza, cikin tsananin fushi da fusata, sarki Bello ya amshi wani ya tare da ambaton Allah ya wurgawa wannan zakin, amma ya kauce. Tabbas abin ba karamin al'amari bane dan haka kamar waɗanda aka tinxira su, suka fuskanci juna da mugun gudu, sarki Bello ya rungume zakin suka fada can kusan rafin dumduma, burin Zakin ya fasa kan sarki Bello. Shi kuma sarki Bello burin shi su fada cikin ruwan, gashi zakin ya jima shi ciwo da faratun shi, (wato kumbar shi) jini yake zuba Sosai, a can kuwa dakarun sun yi nasarar ciro Fulani Aminatu, amma ta jigata sosai, domin ta bugu ta ko ina gyara mayafinta tayi sannan ta ce musu.

"Ina Baffa'm?"

Gurnanin zakin da suka ji yasata, mikewa ta nufi wurin suna tare ta ina ta karta a guje, har bakin ruwan suma dakarun suka iso, lokacin baka ganin kome sai jini da ya bata saman ruwan, wani irin dafe kirjin ta,ta fasa wani irin kuka tare sa kiran shi.

"Baffa'm!!!" Zata shiga cikin ruwan.

Innayoh da suka samu damar isowa ta kamota,

"Don Allah ki sake ni, Wayyo Allah na Baffa'm Wayyo kar ka tafi ka bar ni, don Allah ka fito mu tafi" ta kuma fada da ƙarfi zata shiga cikin ruwan. Wani juyi suka yi a cikin ruwan. Zakin yana wani irin kuka na niman agaji. Suka kuma nutsewa, ba a kuma jin karar su ba, da gudu Fulani ta kwace, ta fada cikin ruwan tana niman shi, ihu take tana shawagi a cikin ruwan, kamar an ce ta juya ta hango gawan zakin, a saman ruwa.

"Baffa'm!!" Ta fada da ƙarfi tana kuka, a hankali ya sako a hannun shi ta cikin ruwan ya ja kafarta ta fada cikin ruwan ji kake tsudummmmm.

"Fulani Aminatu!!!" Suka fada da karfi, d'ago hannun yayi daga cikin ruwan yana musu alamar su tafi kawai.

Juyawa kowa yayi simi-simi. Koda ta nutse cikin ruwan kokarin tashi take ya sakalo hannun shi zuwa kugun ta, yana murmushi a hankali ya janyo ta har wurin da

kafarta ba zai iya kaiwa ba, ya d'ago ta yana kallon yadda take shaƙar iska, sabida ya d'ago kanta saman ruwan.

"Kin zata na mutu ne?" Ai kuwa ta fashe da kuka tare da rungume shi.

"Baffa'm naji tsoro"

Sumbatar bakinta yayi yana cewa.

"Ni ma naji tsoro amma ban zata idan na gan shi zai miki wani abu xan daina jin tsoron shi ba, sai kawai naga Sabida yar kwailata nayi fada da zaki" tura baki tayi tana faɗin.

"Ni ba kwaila bace" ta fada tana kokarin kwace kanta.

"Toh Fulani karki manta nan ba zaki iya tafiya ba sai dai ki nutse dan haka a jira na fito dake ko?" Kwalla ne ya cika mata Idanu. Baki daya ya gama rena mata hankali, zata tambayi Innayoh taji me yasa yake kiranta da kwaila? Komawa tayi ta kifa kanta kirjin shi, sai yanzu ma take jin tsoron biyo shi cikin ruwan da tayi.

"Kayi hakuri ka fidda ni waje!" Ta fada kamar zata fasa kuka.

"Hmmmm" ya fada cikin jin radadi sannan ya ware idanu shi akan ta.

"Sai kin yarda ke kwaila ce" ai kuwa sai gashi ta harxuka, halin Fulani ya motsa kawai ta kwace daga jikin shi ta fara kokarin fitowa waje, ai kuwa yana sane ya kyale ta, ganin zata nutsu yayi maza ya biyo ta, tare da ɗaukar ta a kadadar shi har waje, ya shimfida ta a yashi, sannan ya zauna yana saukd ajiyar zuciya.

Kallon rigar ta yayi yadda ya kwanta a jikin ta, sakamakon jikewar da tayi.

"Lallai kwaila ta fara girma naga kirjin ba laifi" da sauri ta juya mishi baya tana tura baki, dan haushi ma tashi tayi tana kokarin barin wurin ya kamo hannunta, ta koma kan shi. Rungume ta yayi sannan ya sumbaci hancin ta, zuwa bakin ta yana kallon yadda take matsar kwalla.

Mikewa yayi ya ce mata " karki yarda ki fito a bayana har mu isa wurin keken mu"

"Toh" ta fada, a hankali suke tafiya tana bayan shi yana gabanta, har suka isa wurin keken su, tantin da aka kafa ya nufa tana bin bayan shi, suna shiga ta zube a saman Kilishin da aka shimfida.

"Na gaji"

"Sannun yar kwaila" tura baki tayi taki amsa mishi, yana sane ya fadi haka domin ya kara bata haushi, har ya sauya kayan shi, ya duba kayan ta da yake ajiye a wurin ya fita, sannan yasa aka tura mata Innayoh.

Ai kuwa Innayoh na shiga ta rushe da kuka, zaka rantse ya mata wani abu ne kafin ya fita nan kuwa kalmar kwaila ce take yakushinta.

"Kiyi hakuri tunda babu abinda ya faru da shi" cewar Innayoh sabida a tunanin ta ai sabida abinda ya faru ne, ai kuwa tura baki tayi ta fara jan dan hancin ta.

"Innayoh wai me yasa yake kirana kwaila? Don Allah gaya min kullum daga ya ce min kwaila sai ya ce min matsoraciyar yarinya ko ya ce min raguwa" aikuwa take Innayoh ta d'ago bakin zaren, dan haka ta toushe kanta tana murmushi.

"Idan ya kuma ce miki kwaila, toh da gaske ke Kwailar ce, karki kuma mishi kuka idan ya bukace ki kin ji ko?"

"Toh naji, amma Innayoh dole ne sai an yi wani abu, wallahi ni baya na ne ma yake min ciwo." Ta fada tana juya mata baya, fita Innayoh tayi ta sa aka nimo hararabi, a take aka tafasa mata shi, sannan aka shiga da shi ta sakata dole ta sha, ita kuma ta shiga rarrashinta, tana gaya mata wasu manyan manyan sirrin mowar mace, tunda ya ce mata kwaila ta yarda a tafi a haka sai ta mishi irin aikin kwailayen. Aikuwa haka ce ta faru, bayan Innayoh ta fita tayi Sallah, ta ci abinci kaɗan. Sannan ta kwanta barci ya kwashe ta.

....

A waje kuwa kwashe gawarwakin mutane aka yi aka binne su, sannan aka shiga gyara keken dokin su.

"Allah ya baka nasara dole sai mun kwana asuban fari mu bar nan"

Mikewa yayi yana kallon su, sannan ya ce.

"Kuyi duk abinda ya dace" sannan ya juya zuwa tantin su, yana shiga ya same ta akwance tana barci.

Shafa wuyar ta yayi zuwa fuskar ta, aikuwa tayi wani munafikin mika, duk rabin cinyoyin ta suka bayyana, kura mata ido yayi yana kallon ikon Allah, yarinyar nan ta ci uwar kwaila sai dai uwar Kwaila. Garin ya gyara mata kwanciyar ta, ta wani juyi ta koma saman shi. Hàdiye yawu yayi cikin nutsuwa yana kallon ta, a hankali ya sauke ta, tare da kamo kafarta zai gyara mata zaman mayafin, ta wani bararraje kamar wacce ake gaya mata. Wani dauke wuta yayi kunamar shi da zuciyar shi suna wani irin bugawa lokaci guda. Gashi kamar dole an ce mishi ya gyara mata, sai kokarin ganin ya gyara mata kwanciya yake, aikuwa ya ɗan mike tare da mata rumfa zai ja mata bargo, kawai takai kyakyawar kafarta ta zungure mishi. Ya liman din shi, innalillahi wa'inna alaihil raji'un, kai idan bai yi karya ba har da yakuso mishi fatar limamiyar shi tayi, kura mata ido yayi yarinyar nan ta gama da shi saura lokaci kaɗan ayi sallah magariba, zata saka shi yayi wanka da almurin fari. Kasa hakuri yayi ya shiga lugwaigwaita yar mutane, tun yana kokarin yayi kaɗan bayan isha a sunkuya na gasken sai gashi, ya zurme baki daya ya shiga gurzanta kamar Allah ya

aiko shi. Babu abinda ya bashi mamaki yadda ta lumshe idanun ta, tare da k'amk'ame shi babu kuka ko ture shi, haka ya cigaba da haketa, Allah ya gani bai tab'a marmarin mace tun samartakar shi, wallahi idan ya haye saman Aminatu gani yake kamar alfarma yake mata idan ya kyale ta, amma tabbas bai da juriyan kyale ta domin wallahi ji yake kamar ya dauke ta yayi ta yawo da ita. Yasan darajar ta, kuma yasan muhimmancin ta, baya jin akwai abinda zai fita daraja a rayuwar shi. Dan haka har aka yi sallah magariba da Isha yana daki yana bulale yar Kwailar shi, yarinyar bata da wayo sam ta haye keken beran Innayoh ta zauna yana gurje ta.

Kallon fuskar ta yayi da yake dab da fara kuka wiwi. Kai bakin shi yayi saman nata domin yana son lallai ya rabu da ita amma yan kukan da take yi da ture ture yau bata yi ba, kuma shine mafi girman a rayuwar auren shi, yana son yaga tana kukan domin jin shi.yake kuzarin shi na karuwa. Kallon fuskar ta yayi kamar zai zubda kwalla ya sake bakin ta ya ce mata.

"Minani ba zaki min kukan bane ina son kukan ki" a hankali ta bude idanun ta, ta kura mishi ido kafin ta kuma lumshe idanun ta.

Cikin wani irin yanayi yake tafiyar da ita, bai san lokacin da ya shiga sumbatar wuyar ta, yadda ya rikita mata lissafi yasa ta sake wani marayan kuka dan har lokacin ba zata ce ga yadda take ji akan rayuwar auren ta ba, sai dai yasan duk yadda yayi da ita tana jin kamar karta rabu da rayuwar shi. Kuma shine namijin da ya koya mata abubuwa dayawa, dan haka ta fara wani irin shashekar kuka, me mugun tafiya da hankali. Cikin salon da bata san ya zame mata jiki ba, sai gashi tana mishi kukan tare da wasu irin fisge-fisge..

Shi kan shi bai san cewa ya kunce mata ba, sai da yaji muryanta na shirin tashi sama, kawai ya tushe ta baki daya.

Bayan wani lokaci ya koma gefe yana kallon ta, yadda take sauke numfashi. Tausayi ta bashi wallahi bai san yadda aka yi ya haukace akan ta ba, kome nata zam-zam. Janyo ta tayi ta kara rungume ta, hawaye ba zuba daga idanun shi, ya sani soyayyar Aminatu daga Allah ne, bai san wacce irin ƙaddara ce a tsakanin su ba, amma yasan Galadima ba zai cutar da su ba. Kuma tunda ya gaya mishi kome akan ta yake kaf-kaf da ita, a yanzun yana jin matukar ya rasa Minani a rayuwar shi tabbas zai kasance mutum me matuƙar asarar mata amfani ita din rabin rayuwar shi ne, juyawa tayi tana kallon yadda kwalla yake zuba daga idanun shi.

"Baffa'm kuka kake ne?...

_____"

End of page 18

Barka da warhaka ya hakuri da halina 😂♀free book kenan a amsa da hakuri □□

#Mai_Dambu

Yau na sha fama da network ne wallahi sai yanzu afwa

[5/14, 2:22 PM] Pearl crystal: KALLABI...!

NA

Mai_Dambu

EWF

BABI NA SHA TARA

WANNAN PAGEN NA KUNE MUTANEN BAFFA'M DA YAR KWAILAR SHI MUSAMMAN AUNTY SA'A WAI AN SAUYA MATA NI 😂 TOH A DAWO DA NI KAWAI

Janyo ta yayi jikin shi, yana shafa bayan ta, yana jin wani sabon kaunarta yana huda duk wani kusurwa na jikin shi, sumbatar goshinta yayi yana faɗin.

"Ba kuka nake ma, ciwo na nafama" kifa kanta tayi a kirjin shi ta fara sauke ajiyar zuciya, samun kan shi yayi da kallonta musamman yadda zufa da gashin kanta ya lullube mata fuska.

"Kin gaji ko?" Ya tambaye ta, bayan ya mike daga kwanciyar, ya dauki mayafi ya rufa mata, a hankali yayi ta wasa da gashin ta, da sauri ya nufi dan makewayin da yake cikin tantin. Ya zuba ruwa yayi wanka da alola sannan ya fito ya taimaka mata itama tayi wanka da alola, shi ya jasu sallah. Suna idarwa ya fita jim kadan sai ga Innayoh da kayan abinci har da y'ay'an itacce, gaushi da ya'yan Audiga. A take ta saka ta yin tsuguno akan gaushin da ya'yan Audiga, yana gyara mace sosai, dan haka tana gamawa ta sata a gaba sai da ta ci abinci sosai. Sannan ta bar tantin, shima ya shigo ya zauna ya fara cikin abincin. Yana kallon yadda take ta zuba gyagyadi, dan haka ya gyara mata kwanciya ya shiga harkan gaban shi. A cikin yanayin da yake, kamar ya koma gida jikin shi na bashi wani abu na daban, dan haka ya tattaro duk wani abinda ya iya domin kare lafiyarta sai da yayi, sannan ya cigaba da wasa da gashin ta, kafin ya kwanta.

....

A hankali take ganin kamar ana wani sha'ani ko biki ne, sai dai kuma bai yi kama da bikin ba, domin dai wata mata ta gani lullube da mayafi, a gefen Baffa'm. Takawa tayi zata tab'a matar aka ture ta ta fadi.

D'ago kai tayi, ta ga Baffa'm. Kafin ta mike ya riko hannunta.

Bude idanun tayi ta gan ta cikin jikin shi, tura kanta tayi cikin murmushi zuciyar ta yana bugawa.

Ganin shi a tare da ita yasa taji wani irin nutsuwa da barci me dadi ya dauke ta.

*

Washi gari

Da wuri suka isa gombe, kuma Alhamdulillahi sun samu karba na musamman, domin a shashin Fulani Shatu aka sauke ta, anan suka zauna ana yi ta hada musu abinci kamar me,

Kiran Innayoh yasa aka yi. Cikin girmamawa ta zube a gaban shi.

"Innayoh ki bata wannan ta tabbatar ta ci a cikin abincin."

"Toh Allah ya baka nasara" ta amshi kullin ta tafi da shi, ta bawa Fulani Aminatu ta gaya mata yadda zata yi amfani da shi.

Bata samu ganawa da mahaifin ta ba, sai washi gari. Tare da Baffanta, suka zauna a babban Zauren Mahaifinta.

"Alhamdulillahi Masha Allah, kin min abunda kowa ya kasa min, kin zauna da mijin ki lafiya. Haka ba ramin dadi yayi min ba, kiyi hakuri da halin da zaki shiga na rayuwa wata rana sai labari"

Gyada kai tayi. Haka suka yi ta mata nasiha. Har bayan wani lokaci sannan ta dawo shashin Fulani Shatu.

A wannan kwanakin, da kan shi Sarki Bello yayi ta bin wasu sha'ani na masarautan. Kafin ya gano asalin abinda yasa ake bibiyar matar shi. Da kan shi ya samu Surukin shi ya gaya mishi abinda ya ke hangowa. Ya kuma ce mishi.

"Idan Kilishi bata fita sabgar Aminatu ba, ba makawa zan dawo mata da kaidinta, kar ta kuma wannan yunkurin."

"Insha Allah babu abinda zai faru"

A bangaren Kilishi kuwa tayi tayi aikin ta yayi nasara amma ina babu abinda ya faru, dan haka ta saka a ran ta sai tayi amfani da karfin ta, dake bata da imani, tana cikin wannan yanayin ta aka aiko mata yarta da za ayi bikin shekara me zuwa ta fad'o daga sama ta mutu, shi ne abinda ta shiryawa Aminatu.

Kuma dama Sarki Bello ya fada ta kiyayye shi, Mahaifin Aminatu bai gaya mata ba, sai gashi ana cikin kokarin sururar Yarinyar daya yar ta ma aka same ta ta mike

kafin kace me sai gawa. Wannan tashin hankalin ba karamin haukatatta yayi ba domin bata tab'a tsammanin haka ba lokaci guda.

Sai da aka yi addu'ar Bakwai sannan Sarki Bello ya dauki matar shi suka bar masarautan zasu koma gida.

**

MAYAKAN SAHIL

"Shugaban rundunar saura wata biyu mu isa masarautar"

"Tabbas Lati nasara bata gare mu dan haka zamu tura budadiyar wasika ga Sarkin su, idan ya amshi abinda ake bukata toh idan bai amsa ba, zamu shiga cikin masarautan mu dauko ta"

"Ya shugabana kana ganin haka babu matsala?"

"Babu dan haka a cigaba da tafiya" haka suka yi ta ratsa tsakanin manyan duwatsu har suka yi tafiya me nisan gaske.

**

Bayan sati biyu

"Baffa'm! Amma mun kusan isa gida ko?"

Ta tambaye shi.

"Insha Allah nan da mako guda zamu isa lafiya" ya bata amsa, haka tafiyar ta kasance wannan karon yada zango kawai ake a huta, qashin gari a wuce. Amma bai hana mutumin nan turmushe yar kwailar shi ba, har addu'oi tayi tayi Allah ya kawo mata bakon ta, ta huta da jarabar shi.

Bakon shima kamar yasan nufin ta yaki zuwa.

Bayan wasu kwanaki suka isa gida lafiya, tun daga bakin masarautan ya fahimci galadima ya kintsa kowani dan Banza, a ran shi ya ji haka ma yayi mishi. Bai saurari kowa ba, sai da ya huta gajiya na tsawon kwanaki biyar sannan ya koma fada, aka cigaba da mulki inda shima yayi ƙoƙarin kamanta halin Galadima, kuma Alhamdulillahi sun tattauna sosai akan abinda ya shafe su har akan Aminatu.

Kuma ta bashi kwarin gwiwa sosai akanta. Shi yasa yake mugun kaunar galadima domin ya mishi abinda bai zata ba, kuma yana cikin mutanen da yakeke girmamawa.

*

A duk lokacin da ƙaddara ta Kwankwaso maka kofa babu yadda zaka yi da ita dole ka bude mata, haka ce ga Aminatu domin ana cikin wannan yanayin musamman ita da sarki Bello aka fara tsiro da wani irin Gulma akan rashin haihuwar ta, wannan shine matsalar da dukkan su biyu suka fara fuskanta, maganar rashin haihuwa har cikin fada, kuma dake an shirya kome a nutse sai gashi sarki Bello ya fara fuskarta matsin lamba daga Wanbai, Sa'i, da sauran manyan fadar musamman da suka kasance kusan iyayen shi ne da baffannin shi, a lokacin Galadima ya tafi lardin sokoto. Mai Martaba sai da ta kai ya kasa barci balle ya samu natsuwa da Aminatu,.itama ta rasa kuzarin ta, musamman da ta ga halin da yake ciki, a wannan lokacin Innayoh ta amsa uwa domin taki yarda ta bar Aminatu ita ɗaya, a duk lokacin d ta zauna tana nazarin halin da take ciki zama take ta dauke mata tunani.

Ana cikin wannan lamari sai ga sako daga shugaban Rundunar Sahil ya turo da sakon lallai sarki Bello ya turo mishi da Fulani Aminatu zai kai ta ga Sarkin su.

Dama an gama fusata shi, da maganar haihuwa yana jin haka ya ce.

"Ka je ka gaya mishi ko baiwar masarautar Gobir ba zata isa gare su ba, balle Matar da nake tsannanin Kauna idan bai tattara haukar shi sun bar min kasata ba, idan na fito sai na sare kan shi na ajiyewa Ungulu suyi watanda da shi"

Da sauri dan aiken ya juya.

"Amma ina ga tunda haihuwa ce bata yi me zai hana ka bas...."

"Nasiru Chiroma!!! Sai na yanke harshen ka idan ka kuma furta wani kalma ga Minani!" Ya fada da ƙarfi sai da fadar ta amsa, wannan yanayin ya tsorata su. Baki daya aka rasa me magana dan haka suka taru a wuri guda. Cikin fushi ya koma cikin gidan. Yana shiga cikin gidan, ta samu labarin yana wurin shan iskar shi. A hankali ta nufi wurin da kayan marmari. Yana tsaye ta shiga da sallama.

Bai amsa ba, sai ma huci da yake ta faman yi, wani irin iska ake lokacin guda ya haɗa da wani irin bakin haɗari, da sauri ya juya zai sauka yayi karo da ita.

"Ina ga kamar akwai abinda kuke boye min ko?" Ta fada mishi.

"Kin ga ki tafi zan zo"

Murmushi me ciwo tayi tare da cewa.

"Yau kwana huɗu kenan, ina son ganin ka babu halin ganin ka, na tafi turakar ka kaucewa Sarkin gida na koma zaka zo, wai akan haihuwa ce ake min haka? Ni fa ba dabba bace. Sannan Ni ba yarinya bace, kai ka girma da tunanina haka. Ba zan hana ka yadda kake so ba, amma idan nice bana Haihuwa me zai hana ka kara wata matar...."

"Keeee" ya daka mata tsawa, wanda ya firgita da ita, murmushin takaici tayi sannan ta ce mishi.

"Idan ba haihuwa kake so ba me yasa kake korata daga ganin ka?" Takaici yasa shi rab'a gefen ta ya nime wucewa. Rike hannun shi tayi.

"Yau ce rana ta farko da ka min haka, amma na maka uzuri domin nasan baka kome sai da dalili. Karka manta ka koyar min da kome ne da kanka ni dalibar ka ce, sannan wannan shine yanayi na farko da na fara fuskarta rayuwa ta a haka. Duk laifin da xan yi maka Karka juya min baya domin shine abu mafi raunin da zai kashe ni" wani irin juyawa yayi ya shiga sumbatar bakin ta. Ya Allah Ya zai yi da kaunar Yarinyar nan. Abinda ake shirin ya aikata shine katangar farko da xa a mishi da ita. Wani irin kaunarta yake ji me tattare da damuwa. Aikuwa iskar da ake ya sauko da ruwa me karfi. Yana zuba akan su. Domin iska ya yaye rumfar da yake wurin. A hankali ya janye bakin shi daga nata, sannan ya rungume ta.

"Kiyi hakuri da duk abinda zan miki" girgiza kai tayi tana Murmushi hawaye na zuba mata.

"Ba zan tab'a mantawa da haka ba" rungume ta yayi. Ita tana kuka shi kuma yana na zuci.

*

Lokacin da me sako ya dawo da labarin abinda sarki Bello ya ce ran shi ya B'aci dan haka ya tura sako kuma Masarautan ya basu wa'adin kwanaki uku su turo Fulani Aminatu ko kuma ya shigo ya sare kan sarki Bello ya tafi da ita.

Haka aka kuma kai sakon, sarki Bello bai ce uffan ba, domin yana bukatar Galadima. Abin sai ya hadu mishi kome yayi tsanani, dan haka ya tura Sarkin gida cikin sirri ya lardin sokoto, domin ya taso Galadima. Abu goma da ashirin shi a can bai da sukuni domin mutanen fadar sun Bayyana mishi bukatar su, ba zai cigaba da zama mace babu albarka ba, tunda ba zai yi aure ba dole ya nime kunyaga ko kwarkwarah, kuma yadda suka kawo hujjar su, sai ya kasa magana.

"Matukar aka baka auren mace ba zaka mata adalci ba, amma idan aka baka kunyaga ko kwarkwarah dole zaka sauke nauyin ta domin zata fi Fulani Aminatu baka lokacin ta, dan haka a matsayin mu na manyan fada mun yanke shawarar baka kwarkwarori daga kowacce gida, idan kuma kana ganin abinda muka yi ba daidai bane toh ka basu Aminatu domin kowa yasan kasar Sahil matsafiyar kasa ce da suka yi imani da tsafi yaki da su kamar yaki ne da rundunar bakaken ifiritai, dan haka ka basu ita ai shima Sarki Shehu Usmanu yasan cewa Yar shi tana da abinda Arkhan yake nima suka baka auren ta me yasa bai rike yar shi ba? Me yasa bai bata tsaro ba, matukar zaka shiga kasada saboda ita dole ka amshi batun mu ko ka janye daga shiga yakin ka bashi ita su tafi....

_____

End of page 19 idan kai ko ke ce a matsayin sarki Bello ya zaka yi wanne xaka dauka zaka bada Aminatu ne ko zaka shiga yakin ne domin ita sannan ka amshi kwarkwarah...

[5/14, 2:22 PM] Pearl crystal: https://www.wattpad.com/1223755152?utm_source=android&utm_medium=link&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=Mai_Dambu&wp_originator=5iXl3uke3sxzQOZVr%2BxMAKDP6eN42Ax4Ot6%2BxVKTareIlzg7OpeSh1RbIOS3Ug0rr8GGs3jYj5ArMbFIJM3y35oDHQehEsNhoUayOKN16aISPA5uCj65DE6pck%2BUtftx

KALLABI...!

A Tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

BABI NA ASHIRIN

Da wani irin tashin hankali yake kwana yake tashi, bawai dan bai da karfin kwatar kome bane, ko ba zai iya tsayawa Aminatu bane sai dai kuma yadda suke had'e kai da matukar tashin hankali. Domin kiri kiri suka juya mishi baya. Kawai abinda suke so zai yi dab haka baki daya ya kuma rudewa.

Ga shi babu Galadima, shima an can galadima addu'a yake Allah yasa kar ya amince da bukatar su, domin akwai son rai a cikin shi. Ba sarki Bello suke son yaka ba, Tarayyar shi da Aminatu ne, ya jima da sanin haka tun tafiyar su Gombe suka nuna basu son shi da Aminatu domin baya fahimtar kome idan aka ce Aminatu tana nan gani yake kamar dan bata kasance daya a cikin su ba, amma bai ga abin tashin hankali akan ta ba..

*

Yau kwana bakwai kenan da ta sanya shi a idanun ta. Ya zabge sai tarin kasumba, da sallama ta shiga cikin dakin shi. Yana kwance kasancewar yau Laraba. Kallon fuskar shi tayi tana tafiya a hankali dan bata son ya farka, kallon shi tayi na wani lokaci sannan ta shiga ban daki ta dauko tasa, da ruwa sai sabulu, tana fitowa ta ja wani karamin adaka ta dauki aska. Kallon shi tayi ta zauna a gefen gadon, sannan ta goga mishi sabulun da ruwa ta fara mishi askin kasumabr da ya tara. Cikin

kulawa da tattalin shi. Yana kallon yadda ta rame, wani karin kyau da ya ga ta mishi shine hancinta da ta saka aka huda mata, yayi mata mugun kyau, ya lura a yanzun take tashen yan matancin ta, a hankali take askin har ta kusan karewa, bata yi zato ba balle tsammanin kawai ta ji ya riko hannun ta. Wani irin ajiyar zuciya ta sauke tana kallon shi.

"Na saka ki ne?" A hankali ta ajiye askar.

"Barka da hutawa" ta fada fuskarta tattare da damuwa.

"Yawwa yan mata" murmushi tayi me ciwo, sannan ta shanye tana kallon shi.

"Akwai wani abu ne?" Ya tambaye ta yana me tashi zaune, bayan ya dauki madubi.

"A'a" kallon yadda take wasa da kafaffunta ya yi. Murmushi yayi yana jin wani kalar tausayi take ba shi, wato tayi sabon lalle shine bari ta zo ya gani.

Tashi yayi daga gadon ya nufi ban daki ya jima, sannan ya fito daure da wani katon mayafi kamar amawali a kugun shi. D'ago kai tayi ta Kalle shi tana masifar kaunar shi hadi da kewar shi. Wani irin mahaukaciyar kewar shi take, a hankali yake tafiya ta kurawa surar mijinta idanu, yadda yake tafiya irin ta cikakkun maza masu tsannanin kuzari da lafiya. Mikewa tayi ta nufi wurin da kayan shi suke ta kuma dauko wani amawalin, ta nufe shi cikin nutsuwa hadi da wani taku, kamar ba zata yi tafiyar ba, kafatar ilahirin jikinta wasu mahaukatar motsawa suke, kura mata ido yayi har ta iso gaban shi, ta fara goge mishi kirjin shi me ɗauke da wasu tarin kwanji da gargasa, janyo ta yayi ya mannata da jikin shi. Yana tuna yadda kome ya faru har ya wuce shekarun baya. Yarinyar nan da aka kawo babu kome a kirjin ta yau ita ce a gaban shi cikakkiyar mace me nutsuwa da tarin Darajojinta. Mikewar da kafarta tai alamar zata kara tsawo domin goge mishi kan shi, aikuwa ba zato kawai taji ya dauke ta cak. Wani ajiyar zuciya ta sauke, sannan ta cigaba da goge mishi, tana gamawa ta fara alamar zata sauka, bai dire ta ba sai saman lafiyayyen gadon shi. A hanya ya zauna da ita. Yana kallon yadda take kokarin boye damuwar ta.

"Nasan kin ji labarin abinda yake faruwa" damke amawalin tayi ta kura mishi Idanu kafin ta sake murmushi da ya boye kukan da take yi.

"Ba ga kamar sun fika gaskiya ne" bai zaci haka daga bakin ta ba, ya kura mata ido.

"Ta ko ina sun fika gaskiya, shi mahaifina yasan da haka ai ya haɗa ni da kai. Sannan me yasa bai rike ni ba? Me yasa ya baka aurena bayan yasan akwai wannan yanayin a tare da Ni" fuskar shi ya kai daidai fuskar ta, ya ce mata.

"Ƙaddaran So shi ya sa shi tunanin idan ya haɗa mu, Allah zai bani ikon kare rayuwar ki da darajar ki" hawaye ne ya zubu mata tana kallon shi.

"A'a son zuciya ce" yatsar hannun shi ya kai bakin ta, yana gogawa sannan ya mike, amawalin kugun shi ya fadi ƙasa, bata iya d'ago kai ba sabida kunya.

"Sun bukaci ka bashi ni, shine ka ki?" Ta kuma tambayar shi.

Murmushi yayi tare da cewa.

"Matar da nake so zan bawa wasu yan iska? Ke ki bawa ba zan basu daga masarautan nan ba, dan haka idan zaki kwanta ga amawali nan ki shiga ban daki kiyi wanka" ta fada yana cigaba da aikin shi.

"Amma kwarkwarah fa? Idan ka ajiye ta ba zan kuma samun damar kusantar inda kake ba." Juyawa yayi yana kallon ta kan ta a sunkuye, takawa yayi gaban ta, ya zauna a gefen ta, sannan ya shiga cire mata mayafin kanta da duk wani abinda yake tare da ita. Bai tsaya wata ba. Ya kwantar da ita sannan ya ja mayafi ya rufe su. Tana gaban shi shi kuma yana bayan ta.

"Ba maganar wasa nake ba, wannan maganar na gaske nake rayuwar mu zaka duba." Juyo da ita yayi da karfin tsiya yana kallon ta.

"Innayoh ce ta tsara miki abinda zaki gaya min?"

"Ina son ka fahimci." Bakin shi ya kai habb'atar, cikin kwarewa gami da kewar ta, ya shiga bin ta. Baki daya sun yi kewar juna, sai ka rasa ita ce ko shi? Domin yadda suke gurzan juna, kamar sun shekara basu hadu bane, dan haka sosai yake murzata yana kuma hake ta lungu da sako na jikin ta. Sosai ya gauraya mata lissafi, sai da ya hanata sake furta kome sannan hankalin shi ya kwanta, ya bata kan shi da rayuwar shi. Baya jin zata kuma bukaci ya bata wani damu. Sai da ya gama sannan ya koma gefe yana sauke ajiyar zuciya.

"Na gaya miki bana son kina shiga harkan mulkin ko?" Buɗe idanun tayi tana kallon shi.

Sannan ta ture idanun ta. Tana sauke ajiyar zuciya.

"Kwarkwarah zaka yi fa! Ba kishiya ba balle ka ce min na amince a zauna lafiya! Baffa'm kawai ka tura ni wurin su zai fiyye min kwanciyar hankali da ina kallon ka bani da iko da kai sai na tambayi kwarkwarar ka" tana gama fadar haka ta fara kokarin mikewa.

"Ke" ya daka mata tsawa. A Matukar raxane ta zuba mishi ido.

"Ki dawo nan ki zauna sai kin maimaita abinda kika faɗa"

"Akan me zan maimaita? Ai nasan dukkanin kunnen ka sun ji abinda na ce maka. Ka mika ni gare su idan bana nan zaka iya auren ka, da dai ina kallon yadda zaka dauko min kwarkwarah bani da iko da kai laifi ne dan nayi magana akan ka?" Kura mata ido yayi yana mamakin yaushe Aminatu ta fara kokarin mishi tsaurin ido.

"Yayi kyau!" Ya fada bayan ya dauki amawalin shi ya daura ya nufi ban daki yayi wanka sannan ya fito.

"Ba zan basu ke ba, kuma akan idanun ki xan kawo kwarkwarah har turakata" bata san lokacin da ta fashe da dariya ba, ta ce mishi.

"Eh me zan yi? Ka zata xan yi wani abu ne? Amma tabbas ba zan kuma had'a shimfida da kai ba, ka tafi ka tara bayin gidan nan ka kwana dasu."

Kura mata ido yayi yana mamakin yadda yarinyar ta Haukace mishi.

"Innayoh ce ta turo ki?" Yadda yayi maganar babu wasa a cikin shi yasa ta juyawa cikin fushi.

"Eh wani abu ne?" Ta fada bayan ta gama saka kayan ta.

"Babu shakka kin janyo mata masifa domin sai na saka a zane min ita" a tsorace ta juya tana yarfe hannu ta.

"Wallahi ba ita bane, kawai ni ce na kawo kai na, wallahi Innayoh bata san kome ba" tura ta ban daki yayi ya shiga shiryawa, yana mamakin kishi irin na Aminatu, domin babu abinda ya sakata wannan fadar sai zafin Kishi, yana gama shiryawa ya fita bai kuma, bin ta kanta ba ya nufi fada.

Suna kus-kus ne, amma ana ganin shi suka yi shiru.

"Sarkin yaki a shirya min tafiya yaki ni daya"

"Ya batun karin Mata"

"Bana bukata" kuma dama an gaya musu an ga Fulani Aminatu ta shiga shashin su.

"Akan me? " Suka tambaye shi baki a hade.

"Akan babu wanda yake da iko da ni sai Allah, dan haka kar a kuma min maganar wata mace Aminatu ta wadatar dani"

Takaici yasa suka shiga mikewa zasu bar Fadar.

"Karka manta babu Sarkin da aka tab'a kaiwa wannan lokacin bai da Zuri'ar shi sai kai, idan har ka shiga yaki domin ta, toh abu na gaba dole ka nime macen da zata haihu domin matukar ka dawo a raye dole ka nime wacce zata haihu da kai"

"Haihuwar nan dole ne?" Ya tambaye su a tsawace.

"Dole ne domin ba zamu zauna da bakirariya ba, mun ji ka shiga yakin amma dole ka nimo wacce zata haifa mana magajin gobe idan ba haka ba, zamu yaki masarautan Gombe kamar yadda suka ci amanar aminci basu gaya mana Meke dabaibaye ga rayuwar Yar su ba."

Shiru yayi yana fatar kafin ya sare Sarkin yakin Sahil Galadima ya iso, kusan haka aka rabu rai babu dad'i. Koda ya kome ya same ta kwance tana barci.

Itama tana cikin damuwa kenan? Ya tambaye ta, tana jin babu dad'i a ran shi. Har inda take ya tsaya sai kuma ya kyale ta, ya koma babban zaure, yana kallon abincin da aka shirya musu, na musamman.

Innayoh ce ta jagoranci kawo abincin,

Tana gama basu umarni ya ce mata.

"Innayoh meke damun Yar ki?" Shiru tayi sannan ta ce mishi.

"Ana tunzura ta ne da magana mara sa dadi."

"Waye?"

"Ajuji"

"Yayi kyau, amma ki gaya mata borin ta da rigimar ta ba zasu sauya kome ba, don Allah bana son tana haka." Ya fada yana daukar kofin da aka zuba mishi ruwa.

"Insha Allah zan mata fada ma" d'ago kai yayi.

"Karki mata fada domin ban shirya jin rigimar ta ba" ya fada yana cigaba da cin abincin.

"INSHA ALLAH"

Sannan ta fita daga Zauren.

*

Fada suke da wata mata, da ta shigo cikin gidan da tsohon cikin, a matukar tashin hankali, wasu mutane suka janyo ta waje, aka shiga rufe kofar Masarautan ga Baffa'm a tsaye kuka take da ihu tana kiran shi. Tun tana yin abin a cikin barci har Muryan ta ya fito ihu take, yana cikin cin abinci ya sake ya nufi cikin dakin da sauri ya same ta sai kuka take tana mika hannu,. Rike hannun yayi tare da sakawa a gefen fuskar shi. Sannan ya sumbaci hannun ta.

"Fulani na! Gani nan a gaban ki" bude ido tayi, tare da kallon shi bata san lokacin da ta rungume shi ba,.tana wani irin kuka me mugun ciwo.

"Baffa'm don Allah karka bari su raba ni da kai mutuwa xan yi" ta fada cikin matsanancin kuka. Rike hannun ta yayi yana kara jin wani irin kaunar ta, rungume shi tana kuka. Hannun shi ya kai bayan ta, yana bubugawa.

"Ki bar kuka idan Allah ya ƙaddara abu babu me iya kauce mishi kin ji Minani"

"Baffa'm tsoro nake ji, kullum tsoro nake ji kar ka rabu dani don Allah kar kar ka bari su raba ni da kai, don Allah Baffa'm." Yadda take kuka ba karamin al'amari bane a gare shi.

"Toh Insha Allah babu abinda zai faru" ya fada, yana wasa da sumar kanta. Tun ranar bata kuma samun nutsuwa ba, sai ranar Juma'a da ta bar dakin shi domin zuwan bakon ta, a ranar Allah ya nufa galadima shima ya dawo. Gwanin ban tausayi idan ka ga yadda suka damu, kallon Galadima yayi sannan ya ce.

"Na yarda haihuwa na Allah ne amma yadda suke kokarin ganin sun rabu da ita shine zuciyata ta gaza dauka. Galadima kayi wani abu."

Shiru yayi kafin ya ce mishi.

"Kayi hakuri tunda Sarkin gida ya kai min batun na shiga damuwa, wannan shine adadin lissafin kaddaran ta, Babu wani abinda xan iya yi domin kare ta, ko hanawa sannan kamar yadda kake son haihuwar ba zai zo cikin sauki ba, dan haka ka amshi bukatar su, tunda dole ka kare rayuwar ta."

"Kana nufin" ya tambayi Galadima tare da rike hannun shi idanun shi na cika da kwalla.

Gyada mishi kai yayi shima hawaye na zuba daga idanun su baki daya.

"Me yasa sai ita?" Ya tambaya cikin wani irin tashin hankali. Galadima shima zama yayi tare da sunkuyar da kan shi.

"Na tafi lardin sokoto ne domin dakatar da wani abun, Alhamdulillahi abu na gaba shine ba zan iya kome a tsakanin ku ba, kai ne kake da wuka da nama. Imma ayi nasara akan ka Imma kuma ayi akan ta."

"Ni kuma?"

"Eh kai! Kai ne na gaba"

"Galadima wai me yasa kake min magana a dunkule? Ka gaya min meye zai faru."

"Ba magana nake maka a dunkule ba, wallahi ban san dalilin ba amma ba makawa zasu iya bin ta kan ka"

Nuna kan shi yayi da dan yatsar shi.

"Kuma ni"

"Hmm! Kowani mutum yana bincike kafin ya aiwatar da kudirin shi, dan haka kayi kokarin ganin ka shirya." Mikewa Sarki Bello yayi tare da cewa.

"Wannan zancen banza ne, tunda ba zaka min bayani yadda zan fahimta ba, sai kayi." Baki daya dawowan Galadima bata mishi amfani ba, domin duk yadda yaso kare Aminatu sai ya samu Galadima yaki ba shi goyan bayan da ya dace karshe ma, sai ya kara fahimtar kamar ai da hannun Galadima a cikin abin da ake musu dan haka a zuciye ya shirya domin tunkarar makiyan Aminatu idan ya gama da su, zai dawo kan mutanen fadar.

Ana gobe zai tafi yakin bayan sallah isha.

Tana zaune a gaban shi.

"Baffa'm ka min alkawarin zaka dawo a raye!" Ta fada bayan ta kifa kanta a kirjin shi.

"Insha Allah zan dawo zan dawo miki da yardan Allah zan dawo kamar yadda na tafi"

"Baffa'm" ta kira sunan shi cikin shashekar kuka, hannun shi ya kai fuskar ta.

"Ba zan bari a ci mutuncin ki ba, kuma ba zan tab'a amince domin keta alfarmarki ba, ina son ki."

"Baffa'm Insha Allah zan haifa maka Yarinya Kyakyawa kamar ka, ayi mata irin wannan tsagon naka, ina son ta kasance mace Jaruma kamar kai."

"Ta zama me hakuri kamar ke" ya fada yana sumbatar goshinta, yau ne ranar farko da ta kalli cikin idanun shi tana son gaya mishi abinda take ji a kan shi. Amma kuka da shashekar da take ta kasa magana sai kallon cikin idanu juna suke, kamar ba zai dawo ba, hannun shi ya kai wuyar ta, ya janyo ta a hankali ya shiga sumbatar bakin ta, kamar ya had'a da ita ya cinye...

_____

End of page 20

Romeo and Juliet sun haɗe sai a hankali ♀♀♀

Kar wani ya ce min zai yi min kuka

Ina sanar muku da sabon labarina paid book da zan fara Insha Allah next month me suna Zayn Malik June update Insha Allah amma karshen june Insha Allah dan haka yan kasuwa da ma'aikatan gwamnati da uwaren gida masu sana'o'i gani nan zuwa gare ku da sabon labari... Dan haka idan kun ji dadin Kallabi na san da kanku zaku zo saya 300₦ ne kunsan yadda muke a kasar nan babu yawwa Allah yayi mishi albarka

#Mai_Dambu

[5/14, 2:22 PM] Pearl crystal: KALLABI...!

A Tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

https://www.wattpad.com/1224376096?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=share_published

BABI NA ASHIRIN DA DAYA

Lumshe idanun ta tayi tana kara rike rigar shi, tare da jin kamar su tafi tare, kallon yadda kwalla ke sauka akan kyakyawar fuskar ta yasa shi kai bakin shi saman siririn hancin ta ya sumbace shi a nutse. Sannan ya d'ago kanta yana kallon yadda zara zaran gashin idanunta suka mike bayan sun jike da kwalla, bakin shi ya kai kan idanun ta na dama, sannan ya mai da na hagun. A hankali ya janye daga jikin ta, yana me rike hannun ta.

"Kin yarda na zan dawo ba?" A hankali ta bude idanunta da suka yi jajjur sannan tayi murmushin da bai hana kwallar zuba ba, ta ce "nasan zaka dawo" ta fada bayan ta kai hannun ta saman Kirjin ta, yana jin yadda yake bugawa.

"Ki fadi abinda yake ranki"

"Idan ka dawo zan fada maka" ta fada tana Murmushi sannan ta mike daga inda take, ta nufi tagar shi, ta tsaya tana kallon waje.

Hannun shi ta ji a bayan ta, ya kuma k'amk'ame ta mai da kanta tayi Kirjin shi, tana fesar da kukan da yake cin ta, kan shi ya saka a kadadar ta. Yana sauke ajiyar zuciya samun kan ta tayi da daura hannun ta a saman na shi. Wani irin kuka yana kara rugurguz mata zuciya.

Da sauri ta juya tana fuskar tar shi, d'aga kai tayi tana kallon fuskar shi domin ya fita tsawo sosai, kanta a kirjin shi yake tsayawa.

"Idan na haihu ba zaka kara kwarkwarah ba?" Ta tambaye shi da wata irin raunanin murya wanda yake dab da falasa kukanta.

"Ko baki haihu ba, har abada ba zan bari kwarkwarah ta fiki yawa ba"

Cikin rashin gamsuwa ta ce mishi.

"Duk da ban san kome akan Mahaifiyata ba, amma nasan fifitatta da baffana yayi ne ya janyo mata mutuwar ta, ina tsoron kar na zama daya daga cikin mugaye mata ne, shi yasa amma dan ta nice ka kawo duk wacce kake so"

Tana gama fadar haka ta juya zata bar shi a dakin.

"Na zata kin zo muyi sallama ne, a tunani zaki kwana ne fa?" Juyawa tayi tana kallon shi kafin ta ce mishi.

"Ina ga lokaci ya kusa d zan koyawa kaina ni ɗaya a matsayin matar da tana ganin sarki da iyalin shi"

Lokaci guda yaji ran shi ya b'aci,

"Idan na isa dake ki tsaya muyi bankwana idan ban isa dake ba, ki tafi abin ki, kina nufin abinda kike min zai saka ni fasa abinda ya zama kamar dole ne a kaina ne? Ko kukan Ni da borin ki ne zaki saka ni fasa abinda na yi niyya ne? Ki gaya min meye nayi Miki da baki iya adana kishin ki ne?"

Cak ta tsaya tana mamakin yadda har ya fadi haka a gare ta, juyawa tayi tana kallon shi. Sannan ta koma bakin gadon shi ta zauna tare da sunkuyar da kanta.

"Kayi hakuri" daga haka ta fashe da kuka, ta jima tana kuka samun kan shi yayi da son rarrashinta, kuma bai yi kasa a gwiwa ba, ya shiga rarrashin ta har tayi shiru, kusan wannan daren sun yi shi ne babu wani dadi babu wani abinda suka karu da shi, har kusan asuba, sannan ya janyo ta ya rungume ta sosai a jikin shi yana shafa bayan ta, har tayi barci. Sai da aka kiran sallah farko ya raba ta a jikin shi, sannan ya nufi ban daki yayi alola ya nufi masallaci, sai wurin karfe shida ya samu tana barci , a hankali ya zauna yana ja mata yatsun kafa, bude ido tayi akan shi.

Ajiyar zuciya ta sauke tana kallon shi, kafin ta mike zaune tare da rike mayafin a kirjin ta, tana kallon yadda yake mata wani irin kallo tun daga sama har zuwa yatsunta.

Shafa kan ta yayi ya ce mata.

"Tashi kiyi sallah"

Tashi tayi a jikin ta a mace, jan mayafin yayi daga ita har mayafin suka zube a jikin shi.

Kyakyawar riko yayi mata tare da juyar da ita, lumshe idanu tayi tana jin bakin shi a wuyar ta, har zuwa kirjin ta, daga nan bata kuma fahimtar kome ba, sai da ya kai ta duniyar da bata zata ba, ya tara mata gajiya sosai, sannan ya dauke ta cak zuwa ban daki suka yi wanka, ta fito ta gabatar da sallah, sannan ta koma ta kwanta, tana son tayi kuka amma zuciyar ta tayi wani irin tauri, sai ajiyar zuciya take saukewa, lokaci zuwa lokaci.

Yana zuwa ya same ta a kwance, ya kwanta a bayan ta. Ya shiga rarrashinta tun tana daurewa har ta shiga kuka, baki daya ya lalace a wurin ta, ya manta da kowa sai ita, a hankali ta janye jikin ta jin ana ta buga tamburan masarautar, wanda yasa ta mike tana jin gyaran muryan Sarkin Gida, da kan shi ta fita ya amso mata wani irin kaya da aka masu iri daya, kome har da alkyabbar shi, da takalmin shi, an yin shi babba Alkyabbar har baya gashi an saka wasu irin kyalkyali kamar wata dawisu karamin kyau tayi ba, haka da taimakon shi ta shirya, suka fito har zuwa wurin cikin abincin, d'ago kai tayi taga Innayoh, kallon juna suka yi, a cikin kwayar idanun Innayoh ta ga kwarin gwiwa da juriya. Dan haka ta sunkuyar da kai ta fara cikin abincin. Tana ci tana share kwalla. Hannun shi na hagu ya daura akan nata, yana kallon yadda take goge kwallar ta, daura hannun shi yayi a saman nata, tare da matse hannun. Bata wani ci sosai ba, tabawa tayi yana kallon Innayoh, jin jina kai tayi tare da yada mishi kai.

Bayan sun gama ya mike, kasa tashi tayi sai da ya dauke ta, sannan Sarkin gida ya dauki kayan shi na yaki ya fitar da shi, haka yake tafiya da ita a hannun shi, tunda ake a tarihi ba a tab'a samun haka ba, asalima a ƙasar Hausa ba a tab'a haka ba, sai abin ya zama sabon alamari. Lokacin da suka fito baki daya mahakuntar masarautan ne a waje, komawa gefe galadima yayi dan yana hango karfin hali a wurin sarki Bello, yayin da Fulani Aminatu keta sharan kwalla, zama yayi yana share kwalla shima, a karon farko a rayuwar shi da ya kasa samawa abokin shi kwarin gwiwa, a karon farko da ya gaza fitowa ya gaya mishi makomar shi da Fulani Aminatu, a karon farko da ya ci amanar yarda da yayi mishi.

Yana kallon yadda Sarki Bello ya wuce da ita sashin sa, domin ya rarrasheta, sai da ya zaunar da ita, sannan ya rike hannun ta, yana murza yatsun ta.

"Ina jin zafin hawayen ki a zuciya ta, ina jin kamar ban Miki adalci ba, ki yi kokarin taimakona da hakuri man, ta ina zan samu kwarin gwiwar dakatar dasu, ta wurin ki ne idan ban samu ba ina fita gawata za a dawo Miki dashi."

Da wani irin sauri ta d'ago kai idanun ta na kara zubda kwalla hada hannayen su tayi wuri guda, tana matse su.

"Ba zan kuma kuka ba, kayi min alkawarin zaka dawo a raye, don Allah kar ka ce ba zaka iya ba" rungume ta yayi yana sauke ajiyar zuciya.

"Matukar bata Allah bace ta faru dani Insha Allah zan dawo da kafana." Rike hannun yayi sosai. Yau tafi bashi tausayi sama da kullum.

"Insha Allah zan dawo"

"Na yarda kuma nasan zaka dawo, tashi ka tafi Jarumin maza" ta fada haka tana me goge fuskar ta, babu musu ya mike, ita kuma ta rike hannun shi suka fito, akan fuskar ta kawai zaka iya karanto damuwar ta, bama sai kasha wahala ba. Dan haka suka nufi wurin da dawakai suke jiran shi. Tsayawa tayi sannan ta zare hannun ta acikin na shi. Kafin ta juya zata bar wurin.

"Ai zaki tsaya kiga tafiya ta" cak ta tsaya batq bukatar juyawa ta kalle shi matukar tayi haka zuciyar ta zata iya bugawa. Dan haka tana tsaye bata juya ba, tana jin ana Mishi addu'a. Har zai tafi wurin dokin shi, sai jin hannunta yayi a cikin nashi ta saka mishi wani abu. D'ago kai yayi yana kallon ta, ta juya a hankali. Kallon abin yayi sannan ya kalle ta, murmushi yayi domin ba kome bane sai gashi wutsiyar zomon ra dan dalago. Kallon shi yayi tare da juyawa ya kalli yadda ta kasa barin wurin. Takawa yayi har inda take, sannan ya kai hannun shi ya rungume ta, a hankali mutanen da suke harabar masarautan suka watse, sun jima a haka sannan ta juya tana ce mishi.

"Baffa'm ka tafi Allah ya tsare, ina nan ina jiran ka, sai ka gaya min waye ya baka damar cinye min dan dalago na" murmushi yayi yana me jan kumatunta.

"Da gaske me Fulani zata min idan na dawo?" Bakinta ta kai kunnen shi ta fada mishi wani abu, zare idanu yayi yana kallon ta, kafin ya sake dariya me sauti sannan ya ce mata.

"Kin ci bashi yar nan zan dawo da izinin Ubangiji" daga haka ya juya, kallon shi take tana murmushi, wani irin hadari ne da iska ya kamkama, tana tsaye a wurin har ya haura dokin shi, ya kad'a linzamin ya juya da sauri, suka bar masarautan daidai ana ruwan sama da karfi, zubewa tai a wurin tana me rike kirjin ta, sakamakon ciddar da aka buga, (wato tsawa) kuka take son yi amma ina ta kasa koda tari ne, hawaye ne ke zuba daga idanun ta, tana zaune a wurin sai da aka saka mata lema akan ta, Sannan ta d'ago kai, Innayoh ce tsaye idanun ta yayi jajjur.

"Tashi mu tafi"

"Innayoh zan jira shi ne" ta fada a sanyayye.

"Ba dawowar yau bane ko gobe, Addu'a zaki mishi"

"Toh Uwata" ta fada a sanyayye, d'ago ta tayi, sai kuma ta koma zata zube, Innayoh ta kuma rike ta da kyau, suka nufi cikin gidan.

A hanya suka hadu da Ladidi tare da Tabawa, sai matar Chiroma da yan mata bayi a bayan su.

"Ranki shi dade" suka gaishe ta,

"Ku taimakawa Innayoh kaita cikin gidan mana"

"A'a su bar shi" Inji Innayoh, kawai ganin su yasa ta jin wani irin yanayi a jikin ta.

Cikin mamaki matar Chiroma ta ce.

"Ita Fulani Aminatun ta fi kowa ne da ba a rike ba? Ku kama ta." Kawo hannun da Ladidi tayi, bata san lokacin da ta fasa ihu tana birgima kumfa na fita a bakin ta da hancin ba.

A tsorace suka ja da baya.

"Karku sake yunkurin kawo min farmaki. Bana son fitina" ta fara kanta a sunkuye, janyota Innayoh tayi suka wuce su.

Suna shiga shashinta, ta zube a zauren tana kuka kamar ranta zai fita, zuwan Sarkin gida da Galadima yasa Innayoh fita, can sai gata da sabon ƙwarya, shake da madaran saniya. Aka bata tasha, a hankali zanen da yake wuyarta ya shiga bajewa. Kwanciya tayi a wurin gwanin ban tausayi. Fita Innayoh tayi.

"Tayi barci"

"Aminatu zata iya Fuskar ta barazanar Kawo Mata hari, sai dai kuma me yiwa ta kare kanta, a duk lokacin da ta sunkuyar da kanta karki yi kokarin dakatar da ita, mugu ne yake tunkarar ta. Abinda yasa na ki bashi goyan baya kenan, domin idan ya ce sai nayi magana rayuka zasu ɓaci, Innayoh masarautan nan akwai munafukai ne, idan na ce zan hana ya amshi kwarkwarah abin da zasu ga Aminatun zai iya shafar rayuwar shi, ya kasa fahimtar haka, kai sarkin gida kasan kome kafin mu shigo masarautar nan daga Sokoto, karewa ma sai da muka yi yar dabara sannan muka shigo cikin gidan nan."

"Kashedi suka mana kar ya shiga cikin al'amarin Aminatu da Bello ya zamu yi? Ana son mulkin ne yanzu da karfin tsiya, shi yasa aka tinxira mutanen Sahil domin suyi yaki ba wai dan basu razana bane da gargadin shi. Idan aka kashe shi a yaki abu na gaba za a mika Aminatu ga mutanen Sahil idan kuma yayi nasara a yaki, TOH akwai yiwar a koma yakin cikin gidan.....

Ayi hakuri zaku ga labrin kamar ba yadda nace ba wato na zamanin da can, so nayi amfani da salon na musamman ne na saka mana loveromance yadda zai tafi da zamani. Kuma ina fatan xaku fahimci haka idan kuka dubi tsofin English novel na ancient zaku samu an yi mushi kwaskwarima yadda zai tafi da zamani soyayya kuwa ko a kissosin Manzon Allah ana gaya mana tsarin soyayyar gidan shi, S.A.W Nagode

Na fara jin barci idan na fara rubutun nan anya nima ba wadancan ne suka min nasu yar dabarun ba..

□□□😂

Barka da warhaka a cancare lafiya..

Please share comments and vote

#Mai_Dambu

[5/14, 2:25 PM] Pearl crystal: https://www.wattpad.com/1224701901?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=share_published

KALLABI...!

A Tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

BABI NA ASHIRIN DA BIYU

Zaro idanu Innayoh tayi, cikin tashin hankali tare da rufe bakin ta.

"Yakin cikin gida?" Ta kuma maimaita tambayar,

"Eh Innayoh, idan har muka basu goyan baya yanzun zasu iya ɓullo mana ta inda bamu zata ba, amma idan muka koma gefe dole shiri zamu yi na tsawon dawowar shi, dan haka kiyi kokarin ganin kin taushi Fulani Aminatu" inji Sarkin gida,

Wato al'amarin yana son kasancewa ne Sarkin Yawa ya fi Sarkin karfi, duk yadda zasu yi ba zasu iya ba, dole sai sun ninka karfin sarki Bello.

"Shi kenan, Insha Allah zan kiyayye kuma zan yi kokarin tausar zuciyar ta." Inji Innayoh, sannan suka bar shashin, cikin gidan kuwa babu wanda ya kuma d'ago zancen Fulani Aminatu kowa ta kasan shi yake, dake abin ya hadu ta ko ina sai gashi kowa yakin yake da son samun damar da yake ganin shine mafi alkhairi a gare shi.

*

Ana ruwan saman amma zuciyar shi tayi nauyi, kallon shi sarkin yaki yayi.

"Allah ya baka nasara idan suka yi nasara akan mu fa?" Juyawa yayi ya kalli sarkin yaki sannan ya dauke kai, abin ya bashi mamaki.

"Idan ka dawo daga yaki kazo ka samu wani yana tarayya da me dakin ka ya zaka ji?"

Shiru yayi bai kuma magana ba, shima Sarkin yaki maganar ta dake shi sai ya ce.

"Tuba nake, Allah ya huci zuciyar ka" murmushi sarki bello yayi tare da cewa.

"Ba fushi nayi ba, ai bana fushi akan abinda na san zan dawo maka da abinka"

Tsayawa suka yi a kasar wani dutse na dan lokaci, kallon rundunar yayi sannan ya ce musu.

"Ban umarce kowa da shiga yakin ba, ku bar ni nayi yaki domin kimar mata ta. Dan haka ku naku yan kallo ne"

"Allah ya baka nasara, babu abinda zamu yi kenan?" Sarkin yaki ya tambaya.

"Babu abinda zaku min yakin nawa ne, ba na kowa ba. Idan kuka shiga bani da bakin da zan kare al'umma ta balle Mata ta, idan nayi kuwa har abada ina cikin kundin tarihin masarautar Gobir."

Shiru suka yi na wani lokaci, kafin ruwa ya tsaya aka cigaba da tafiya, har zuwa filin da mutanen Sahil suke.

**

Masarautan Sahil

Kallon tursi yayi da take murmushi, sannan ta shafa kokon kan dan adam da wani irin ruwan dalma tana faɗin.

"Arkhan! Leka ka ga uwar Sarkin gobe duba kyakyawar surar da Allah ya mata"

Lekewa yayi, yana murmushin jin dadi, kallon Aminatu yayi da Innayoh take rike da ita.

"Amma ina ɗaya abokiyar tafiyar take?"

"Ba a san inda take ba, duk iya bincike na bamu ga inda take ba, amma nan da wasu shekaru zata bayyana abinda Uwa hil ta gaya min kenan"

"Dukkan su jini daya ne, bayyanar ta zai kuma haifar da wata tarzoma ne?"

"Idan muradin ka bai cika ba, dole sai bayyanar ta zai cika maka duk wani muradin ka"

"Bana fatar haka"

Dan d'ago kai tayi ta ce mishi.

"Sakon mu ya shiga cikin gidan, amma kalli yadda karfin abin jikin ta ya lalata shi" kurawa kokon kan yayi idanu.

Lokacin da Aminatu ta ture baiwar da tazo rike ta, wani irin siririn kifiya ne yayi wani irin fitar bazata daga hannun ta.

"Tabbas ita ce!"

"Dama na gaya maka tana nan"

Wani irin dariya yake fadar yana ɗauka, sannan ya ce mata.

"A shiga shirya min turaka na, yau akai min Yan mata masu tashen balaga, dasu zan gurje amarcina kafin zuwan ta "

A duk lokacin da sarki yake cikin fara'a da farin ciki ana ware mishi yan mata masu tashen balaga, wadanda nonuwar kirjin su basu kai ga girma ainun ba, masu cikakken budurci wadanda zai kwanta da wannan zai sauka da wannan, haka tsarin shi yake, idan aka gama da su za a kai su can cikin gidan shi n bayan masarautar a iya yanzun ba 'a san iya adadin matan shi ba, domin a labarin kunne ya girmi kaka, an ce sun kai dari da wani abu, kuma bai fasa kudirin shi ba.

Har dakaru zasu mike ya ce musu.

"A nima min har a can wurin dattijon nan domin matan su, sun fi sauran matan nan tsafta, wani irin kamshi yake fita a kasar su, jikin su kamar ana wanke su da ruwan madara" gyada mishi kai suka yi, duk da su matan wadancan kabilar idan ya kwanta dasu, bada jinin su ake ga hil, sauran dake nasu ne babu abinda yake faruwa.

Dan haka kafin Sa'a uku, an shirya yan matan an kai mishi turakar shi, sa nan aka zo aka gaya mishi.

Murmushi yayi sannan ya ce.

"Tursi me zaki bani, domin naji dadin juya kwankwasona."

Rufe idanu tayi sannan ta bude da sauri.

"Ka kori yarinyar wurin dattijon nan babu alkhairi a tare da ita, kashe ka zata yi" sannan ta mika mishi wani kofin zinari, shanyewa yayi sannan ya kalle ta.

"Toh naji zan Kore ta" ya fada bayan ya mike, ran shi ya gama biyawa akan yarinyar tursi ta shigo da wani magana ba zai tab'a yarda ba, sai ya lashe kirjin ta zuwa kasar ta da yake fitar da kamshi nan.

*

Fulani Aminatu

Sai da rana ta fadi sannan ta bude idanunta, kanta yana sarawa a hankali ta mike tana kallon Innayoh.

"Baki tashe ni sallah ba?"

"Eh wai naga baki jin dadi ne" a hankali ta shiga ban daki, ta tsuguna zata yi fitsari jini ya sauko mata, sai da ta gama fitsarin ta wanke wurin sannan ya haɗa ruwa tayi wanka, sai da tayi wanka sosai, sannan ta shirya ta fito,

"Innayoh bani kayan wankina" ta fada tana neman wurin zama. Dauko kayan tayi ta mika mata, sai kamshin turaren suke, ta koma ban daki ra gyara jikinta, sannan ta fito saka wani riga tayi iya kwanjin ta, sannan ta kwanta tana kallon tagar dakinta.

"Ba zaki ci abinci ba?"

"Innayoh na koshi" ta fada tana kallon waje.

Yadda ta juya baya ba karamin damuwa ta saka Innayoh ba, dan haka ta zauna a wurin har aka kira sallah Isha sannan ta fita, sai lokacin ta fara kuka, kuka sosai take tana jin kamar ta mutu ta huta da wannan yanayin da take ciki. Har taji motsin Innayoh sannan tayi shiru kamar tana barci.

"Gashi inji Galadima wai a baki wannan kisha"

Tashi tayi zaune tana ƙwaryan zuma ce me hadi,sai da ta sha sosai sannan ta koma ta kwanta.

*

A can wurin kuwa har dare ruwa ake, dan haka sarki Bello da jama'ar shi, komawa ƙasar dutse suka yi aka kwana, bayan sun yi sallah asuba. Aka tura dan aike ya gaya musu ga sarki Bello da tawagar shi.

Aikuwa kamar jira suke suka fara maguzanci, ta hanyar bubuga abu ana ihu.

Sai da aka bari rana ta fara ketowa, sannan dukkan su runduna biyun suka bayyana a filin,

Shugaban rundunar sahil, ya fara magana da cewa.

"Zamu kyale alummarka idan ka bamu Aminatu, idan kuma ka ki zamu yake ka har zuwa masarautar ka"

Murmushi sarki Bello yayi sannan ya ce mishi.

"Toh Allah ya baka sa'a, amma da sharadi idan kayi nasara a kaina, ka ɗauki Aminatu. Domin Ni daya zan yi yaki da kai, sannan na baka damar kwace masarautar. Da yardan Allah idan ni nayi nasara akan ka, zan kashe ku baki daya kuma ba zaku kai labari ba"

Dariya suka saka mishi, musamman da suka lura da sarki Bello bai kai shugaban runduna wato Murad.

"Toh shikenan, Hil ta bani nasara" shugaban runduna ya ce.

"Alhamdulillahi Ubangiji ka bani nasara" inji Sarki Bello,

Komawa gefe lati yayi tare da shugaban runduna ya ce mishi.

"Ya shugaba shi daya zai yi yakin ba tare da yaji tsoron yawan rundunar mu ba, sannan kaga jama'ar shi basu da yawa, akwai abinda ya taka matukar bamu samu yadda muke so ba, zai karar damu dan haka ka wakilta wasu, yaki da shi muga yadda zamu shawo kan shi a yaƙin"

"Na gamsu da bayanin ka dan haka a ware mutane na musamman mutum goma su ji dashi"

Haka kuwa aka yi, ba wani dauki lokaci ba aka fara yaƙin, kamar zasu samu nasara akan shi, amma Allah ya bashi nasara, bai kashe su ba amma kuma ya nakasa su. Sannan ya koma gefe yana haki ya ce musu.

"Ka haɗa kan rundunar ka, ku bar min da'irar wankina" inji Sarki Bello.

"Ba a san maci tuwo ba sai miya ta kare."

"Toh Allah ya bamu nasara" aka sake turo mishi su.

Allah ya kuma bashi Sa'a kan su, haka yakin ya kasance babu sassauci sai lokacin sallah ne kaɗai ya sa sarki Bello hakura da yakin akan sai bayan la'asar, haka ce ta faru.

...

"Lati gaba dani zai kara na ga dai jikata min dakaru yake kuma yana yaƙin kamar wanda yake da karfin ifiritai" Murad ya fada cikin matsanancin bacin rai.

"Ai yaki yarda a yi yakin gamayya ce, dan haka ka shiga da shi muga karyan kare matar shi."

Haka suka yi ta tattaunawa,

*

A can wurin su sarki Bello, bayan an yi sallah kallon shi, sarkin yaki yayi tare da cewa.

"Mai Martaba ban tab'a ganin yakin ka ba sai yau, a zaman da nayi da ahalin ku baki daya yakin su akan kasa ce da kara karfin mulki yau naga yaki akan mace da kare kimarta. Ya shugaba na, wacce irin kauna kake mata haka? Dukkan mu muna da mata da yara, matan mu har da sa'o'in yaran mu, ya shugaba bamu tab'a damuwa akan muna son su haka ba, kai kuwa a cikin Masarautan ka nuna Fulani Aminatu tafi kowa me yarinayr tafi sauran da shi"

Gyara zama yayi yana kallon Sarkin yaki gyatsa yayi a hankali, sannan ya kalle shi da kyau ya ce mishi.

"Ita din renon mashahurin marubuci ne, na san soyayya tun kafin na hadu da Aminatu, na karanta hikayoyin soyayya da kauna, sannan na rubuta labaru akan soyayya, yau da na samu matar da nake so idan ban mata soyayyar da na ke ji a raina ba me zan yi? Yarinya ce na same ta a lokacin, bata da hankali, bata da kome akan ta sai shirme duk abinda Aminatu zata yi koyarwa na ne, sannan bana jin koda xan mutu zata yarda ta zauna da wani namijin dan Ni daya nake gaban ta, nine murmushin ta nine dariyar ta, na mai da kaina sa'anta, sannan na zama abokin ta mijin ta, tana hira dani sama da yadda take da Jakadiyar ta Innayoh, na koya mata abubuwa da idan bana rayuwar ta zata iya kasa yin kome. Ba matan ku tafi ba a'a Tarbiyyar da na bata ne yake da bambanci da na kowa."

"Ikon Allah, dama akwai wata soyayya ne da ta wuce ka auri mace ta haifa maka yara idan baiwa ce ka mai da ita sad'akar ka." Inji Sarkin yaƙi.

"Kazo daidai kuwa. Toh duk ranar da ka ware macen da kake so, ba zaka tab'a farin cikin ganin ta cikin damuwa ba, Sarkin yaki kar dai kuna cikin.mazan da basu iya dauke Damuwar iyalin su sai ta kwanciyar aure?"

Sosa kai sarkin yaki yayi yana kame-kame.

"Kawai idan kuka ji bindin ku ta kumbura sai ku kai ta wurin abinda take bukata ba mamaki ma haka kuke hake musu" ya fada yana kallon sarkin yaki da yayi tsamo-tsamo kamar kazar da ruwa yayi mata duka.

Murmushi sarki Bello yayi tana cewa.

"Nasan yanzun tana can tana kuka. Insha Allah ina samun nasara zan tafi gare ta"

"Allah ya baka nasara"

"Amin Ya Allah"

Bayan la'asar suka fito, anan suka ga ikon Allah, domin shugaban rundunar ne da kan shi, dan haka suka shiga filin.

Kallon sarki Bello yayi cikin nutsuwa ya ce.

"Me yasa ba zaka bamu ita ba kawai akwai mata dayawa sai ka samu sauran" zaro takobi sarki Bello yayi cikin takaici ya ce mishi.

"Ban ji zan iya wannan kasadar ba"

"Toh zaka gani domin ba zan kashe ka ba, akan idanun ka zan tafi da ita waye yasan me zan mata a hanya kafin na isa da ita Sahil tunda naji ance yarinya ce qarama daidai tashen balaga take kome ya daidaita a tare da ita zata ji sabon kugun" cikin wani irin fusata sarki Bello yayi kan shi da azazzaben kishi....

_____

*Anya kuna tsoron Allah 😂 wai page biyar a rana yo ko dari na baku sai kun bukaci kari mu lallaba juna kawai a page ɗaya Ƣamma babu wasu dabarbarun da zan yi gaisuwar wannan shafin naku ne yan Fitilar hikayar Mai_Dambu**

 Nima nayi kan ku da azzababen sauri domin nayi posting kome zai faru oho....?

#Mai_Dambu

[5/16, 5:30 PM] Pearl crystal: KALLABI..!

A Tsakanin Rawuna

Na

Mai_Dambu

EWF

https://www.wattpad.com/1225030646?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=share_published

BABI NA ASHIRIN DA UKU

Kaurewa wurin yayi da azababben yaki, me cike da kishi. Wato duk da bai cika shiga yaki ba. Amma yau sai da ya kure Sarkin Yakin sahil, domin baki daya sauya mishi salo yake.

"Duk akan Matarka kake yakin nan?"

"Toh dama akan ka zan yi yaƙin" ya fada a fusace, bayan ya kai wata gagarumar sara, Murad ya tare da sauri. Duk da yasan bakar magana ya gaya mishi bai hana shi takalar shi da wata maganar ba

"Idan na kashe ka ɗauke ta zan yi" ya gaya mishi haka,

"Sai dai idan bana numfashi matukar ina raye sai inda karfina ya kare."

Haka suka yi ta yakin babu wanda ya samu nasarar koda lakatar jikin dan uwan shi, sai da rana ta fadi dai-dai lokacin sallah, Murad ya samu nasarar yankar Baffa'm a kirjin shi. Sai da ya durkusa,. Sake kawo mishi sara yayi ya kare da takobin shi. Dole aka buga tamburan a tsayar da yaki, lokacin ibada ya kusa, jinin da yake zuba ba na wasa bane.

"Idan ka sake ka dawo gawar ka za a dauka wannan shine gargadina da kai ka bani Aminatu" bai tanka mishi ba, ya koma wurin su, yana isa suka taso zasu rike shi ya d'aga musu hannu, sai ya shiga tantin ya cire kayan, yayi wanka sannan yayi alola ya gabatar da sallah, yana idarwa ya kira Sarkin yakin shi, ya dinke mishi ciwon, duk da zafin da yake ji bai kai zafin kishin da yake ji ba. Dan haka cikin karfin hali ya kalli sarkin yaki.

"Idan muka yi sallah Isha a gaya mishi za a cigaba"

Da sauri ya kalli Baffa'm.

"A cikin daren ka zubda jini fa?"

"Umarni na baka" da sauri ya fita ya isar da sakon Baffa'm, bayan sallah isha aka kewaye filin da wuta yadda ko ina zasu ga yadda ake yakin sosai.

Bayan ya idar ko abinci bai ci ba, sai niman nasara a wurin Ubangiji, sannan ya fito filin.

*

Ta dauki kofin kindirmo zata kai baki, kamar wacce aka mata wani abu, sake kofin tayi ta fita da gudu kafarta babu takalmi. Tare tare ake da ita. Dakyar Waziri

Zakaria ya samu nasarar cafke ta. Wani irin ihu take tana dukar shi da yakushin sa. A lokacin Innayoh suka iso da hansiya. Suka rike ta,

"Fulani ina zaki da alumuru nan, yanzu aka shiga sallah fa."

"Don Allah ku kyale ni, wani abu ya same shi."

"Innayoh ki tafi da ita, insha Allah Baffa'm zai dawo" kuka ta saka tana kara kokarin kwacewa, amma haka Innayoh ta wuce da ita, dakyar aka samu ta nutse, amma burinta shine ta tafi wurin shi.

A masallaci Waziri yake labartawa Galadima, kallon shi galadima yayi.

"Ba mamaki taji hakan ne a jikin ta, son da sukewa juna ne ya haifar da ko ya dayan su, ya shiga wani hali zai ji a jikin shi." Yana gama fadar haka, ya wuce, daga gidan shi ya bada sako aka kaiwa Innayoh, dakyar ta sha. Daga nan sai barci.

*

Tunda suka dawo yakin, Shugaban runduna yake samun galaba akan Baffa'm, amma Naci da taurin kai, a duk lokacin da ta tafi zai fadi, sautin kukan ta yake ji, sai ya koma ya tsaya, da wannan yanayin yake yaƙin tare da rokon Allah ya bashi sa'a. Har kusan goshin asuba, kafin Allah ya bashi sa'a,ya sari shugaba runduna a kirjin shi, faduwa yayi. Ya kuma kai mishi sara, duk da Baffa'm baya gani sai yayi amfani da sautin numfashin sa, da haka baffa'm yayi ta saran shi, har sai da ya daina numfashi.sannan ya fadi akan gwiwar shi yana aman jini.

Da gudu sarkin dakarun suka zo su dauke shi, daga nan shima shugaban rundunar Sahil aka dauke shi domin ya jikata, Baffa'm kan sai da ya share awa biyar kafin ya farka, sallah yayi saboda jikin shi akwai raunika.

Sannan ya saka kayan shi na sarauta ya nufi inda rundunar Sahil take, suna ganin shi suka fara ja da baya, tantin Murad ya shiga yana kwance magashiya wato rai kwai-kwai mutu kwai-, kwai, murmushi yayi sannan ya ce.

"Allah ne ya bani nasara akan ka, sannan na Barka ne a raye domin na nuna maka karfin Addinin Musulunci, ku tattara naku ya naku, ku bar min da'irar ta, na baku sa'a daya, idan kuka sake naji labarin kuna nan zan muku kisar wulakanci. Yanzun kan ku tafi ku rayu"

"Mutanen da suke kewaye da kai, ba masoyan ka bane. Makiya ne da suka bamu damar fuskantar ka. Kayi yakin neman su waye suke maka yankan baya?"

Gyada kai yayi tare da cewa.

"Ba zan yarda da kai ba, domin an hada kai da kai dan tozarta Ni, dan haka kai da wata tsiyar na rundunar ka ku tattara ku bar min Alkarya ta"

"Babu shakka, kai mutum ne me nagarta, na yarda da kai na roke ka da Allahn ku kar ka bari wani abu ya same ta, domin tana tsakiyar kaddaran ta ne"

Kura mishi ido yayi kafin ya saka kai zai fita Murad ya ce mishi.

"Tunda ka bani damar na rayu, ni kuma zan tabbatar ba biyaka halaccin da ka min."

Fita Baffa'm yayi, ba'a yana jin dadi bane amma yau ya kudiri Aniyar ido hudu da Minanin shi. Har ya fara tafiya, jiri ya kwashe shi, kama sarkin yayi yayi, aka nufi Masarautan da shi.

**

Tana tsaye a saman wurin shan iska, ta hango kura na tashi daga nesa, haka ya kara tabbatar mata da shine ya dawo domin ta ga tutar Masarautar ce, dan haka ta sauko tare da murar waje, da gudu tana me ratsa kofofin cikin masarautan har ta iso wajen Masarautan, sama labari ya zo an yi nasara tun safe ita ce dai ba a gaya mata, ba, domin xata iya shiga kuncin son ganin shi.

Bata tsaya ba, duk da kuwa Innayoh tana biye da ita, haka ta wuce cikin kasuwar da yake wajen Masarautan tana kara tunkarar kofar garin da kafarta, tana isa ta tsaya daga bakin kofar bayan an bude mata, kurawa ƙurar da take kara tunkaro su tayi Idanu.

Yadda take sauke numfashi, zaka rantse da Allah mutuwa zata yi, sai lokacin Galadima da waziri suka iso, tana kallon inda dawakan suke kara zuwa a guje, a hankali ta d'aga kafarta, ta fara takawa cikin wani irin kaduwa sakamakon hango shi da a goye a bayan Sarkin yaki, ji take kowani numfashin ta da sunan shi take fita, lumshe idanun ta tayi ta fara kokarin isa wurin su, da suke gab da isowa kofar Masarautan.

Linzamin dokin shi yayi a gaban Fulani Aminatu, kama kama akayi tare da saukar da shi, keken dokin aka kawo aka shiga da shi, itama Aminatu ta shiga, har lokacin bata iya ko magana, daukar kan shi tayi ta daura akan cinyarta, ta fashe da wani irin kuka, wanda ba zaka iua fassara shi ba, domin ba kukan farin ciki ba kukan bakin ciki ba, rungume kan shi tayi har suka shiga da shi cikin turakar shi, yaga rigar jikin shi aka yi take aka fi aka kona bushashen ganyen kaba, aka kona shi tare

da dutsen kwalin, aka shigar barbada mishi a ciwon. Sannan suka fita bayan sun gyara mishi kwanciyar shi. Tunda suka dawo aka yi ta bada labarin abinda ya faru, kowa jinjina mishi yake, ita kan tana makale da shi kamar zata koma jikin shi. Har qashin gari, tana barci a kasa hannun ta yana cikin hannun shi, ta jingina kan ta da shimfidar shi, bude ido yayi a hankali yana kallon dakin, kamshin turaren shi ya tabbatar mishi da cewa yana dakin shi ne, jin dumin yayi a hannun shi.

A hankali ya juya yana kallon ta, tana rike da hannun shi ga shi ta jingina bata jin dadi kwanciyar kawai babu yadda ta iya ne ma, haka ya saka shi mikewa a hankali ya zare hannun shi cikin nata, ya sannan ya sauka ya gyara mata kwanciya, yana zaune cikin so da kauna, Tausayin ta da yadda ta rame yasa zuciyar shi yayi sanyi.

Tashi yayi ya tafi ban daki ya gabatar da alola, sannan ya fito yayi sallah da ake bin shi, sannan ya gabatar da Wanda ya ce shi, sannan ya koma bakin gadon ya zauna yana kallon ta, yana jin wani irin sonta na kara fisgar zuciyar shi, a fisge yake jin tana kara samun matsuguni, hannun shi me lafiya ya kai yana shafa fuskar ta, kasancewar bata san ya farka ba.

A hankali ya koma ya gyara mata kwanciyar ta, sannan ya shigar ta ita jikin shi, shafa fuskar ta yayi yana mamakin ramar da tayi s cikin kwanaki biyu, gashi har nonuwar ta sun rame, ya gane haka ne da ya cusa hannun shi cikin rigarta, hadiye yawu, yayi yana kara jin kewar ta, kallon hancin ta yayi yana jin idan ta haifa mishi yarinya mace, zai yi fatar ta dauko siririn hancin ta, domin yafi kome daukar hankalin shi, sumbatar bakin yayi....

_____

Ban gane ba□□☹ kowa sai cewa yake zan kashe wani dan nice me hannun shika 😭😒😫 na kuma jin tarin ku sai na kashe Fulani Aminatu kowa ya huta

Ku yi hakuri pagen ba tsawo. Thank □□□

#Mai_Dambu

[5/16, 5:30 PM] Pearl crystal: KALLABI...!

A Tsakanin Rawuna.

Mai_Dambu

EWF

BABI NA ASHIRIN DA HUDU

A hankali yake isar mata da sakon isowar shi, a tunanin ta mafarki take, sai da ta bude idanunta tarr akan shi, sannan ta fahimci shine ba wani, rike hannun shi tayi tana girgiza mishi kai.

Dan sumbatar bakin ta yana jin kewarta na kara samun matsuguni a ranshi, zai kuma kai hannu ta mike zubur, kafin ya riko ta ta dira da sauri ta shige ban daki, wanka tayi sannan ta gyara jikin ta kasancewar har lokacin bata gama Al'adar ta ba, ta fito ta same shi kwance, sassanyar murmushi ya sakar mata,

"Yaushe kishiya na yazo?" Ya nuna mata gefen shi ta zauna.

Zama tayi, tana wasa da hannun ta, yau da ta gan shi sai ta nime duk wani damuwar ta, ta rasa. Riko hannun ta yayi yana wasa da shi.

"Fulani Aminatu" ai kamar jira take ta fashe da kuka.

Sosai bai hanata kukan ba, dan haka ya zuba mata ido, sai da tayi ta koshi sannan ta mike zata fita.

Riko hannun ta yayi.

"Dawo ki gaya Meye na Miki?"

Ya tambaye ta,

Cikin shashekar kuka ta ce.

"Babu kome" rungume ta yayi tare da cewa.

"Toh shine zaki tafi ki bar ni? Baki tunanin ciwo na ne?" Girgiza kai tayi sannan ya zauna a gefen shi tana shafa kan shi. Wani gyara kwanciyar shi yayi tare da narke mata kamar me jin zafin ciwon jikin shi. Ita kanta mantaewa tayi da kome, haka suka kasance a dakin yunwa ya fidda su, bayan sun karya, ya dawo dakin yayi wanka ita kuma ta koma bangaren ta, ta shirya amma bata kome ba, dan tasan dole za'a zo gaishe shi, dan haka ita da Innayoh suka shiga babban zauren girkin ta, suka fara abinci ana fita da shi bangaren mai Martaba, kuma kamar yadda tayi hasashe ne, an jama'ar da suke ta shigowa ba iyaka, sai dare ta samu damar zuwa wurin shi, a daddafe haka aka yi ta hidima a gidan kamar ana biki, na tsawon kwana takwas, kafin jama'a suka tsagaita.

Duk da ciwon shi akwai wasu a kirji da damtsen hannun shi, bai hana yau da yake ganin jama'a sun tsagaita ya janyo ta jikin shi ba, kura mata ido yayi, a hankali na tura hannun shi kan lallausar matashin audigar shi, wato kirjin ta, da dukiyar Fulanin ta da yake fisgar shi. A hankali ya daura hannun shi, ya ji sun cika mishi hannu sama da kullum, murmushi yayi yana kallon yadda ta lumshe idanun ta. Murmushi yayi domin yasan ba makawa zai buga shagali yau, aikuwa yadda ya saka a ranshi haka ya shiga lugwaigwaita yar mutane, tun daga sama har zuwa ƙasa, baki daya yasata mantaewa da sunanta sai sunan shi.(□□☹😭 Wallahi mutumin nan

ya isa da ciwon amma yake shirin buga isa) aikuwa bai kuma rikicewa ba, sai da ya d'aga buje, ya fahimci iya shi daya ne a wurin, sai gashi har da wata irin shashekar yaushe gamo, itama Yar banza shiru kuke ji, ta mika mishi rayuwar ta da kome nata, sai yadda yayi da ita. Aikuwa taga aya domin Baffa'm sai da ya juye mata ruwan jikin shi a kanta, sannan ya rungume ta, dan ma jikin shi da ciwo, haka ya hakura da sauran ya barta. Itama almura ko a jikin ta.

Haka zaman jinyar su ya kasance, domin gefe guda ba jinya ake ba, soyayya ake shanyewa. Sai da suka kwashe sati biyu, sai dai ta fita bada umarnin abinda za'a girka. Har ya warke sumul kamar ba shi ba, kafin ya kome fada. Ko hutawa bai yi ba, Chiroma ya gabatar mishi, da Kwarkwarah biyu. Shiru yayi kafin ya ce musu.

"Amma!"

"Ka amsa tunda ai yarjejeniya ce" hankalin shi idan yayi dubu sai da ya tashi. Yana cikin wannan yanayin Wanbai ya bashi wasu biyun, zasu kara mishi Galadima ya ce musu.

"A ka'ida hudu sun isa, idan kuma aka kara toh wallahi ba zamu amshi sauran ba ma balle ƙarin" dake yana cike da Galadima dauke kai yayi yana kallon ƙasa. Haka aka gama zaman fadar. A lokacin sarki Ibrahim kwarkwarah daya yayi sannan zamanin mahaifin su kwarkwarah daya yayi itace ya haifi Yara mata daya tana aure a kwantogora, daya tana aure a daura. Dan haka babu wasu yan uwa da suke cikin fadar sai galadima, koda ya dawo maganar kwarkwarah ya fada kunnen Aminatu, tana zaune a dakin shi. Ya shigo da sallama, kallon shi tayi sannan ta mike tana me cire Damuwar ta a gefe guda, ta taimaka mishi ya rage damuwa. Nasihat Innayoh yana dawo mata akan labarin da ya iso su.

Karki sake ya fahimci baki girme tashin hankali ba, haka zai ajiye ki a ran shi. Ban hana ki jin kishin shi ba amma maganar ki mishi yaji bai taso ba, shima tilasta shi aka yi, sai ki nuna musu kina maraba da zuwan su, matukar kika rike mutunci mutanen banza ma mutumtaki zasu yi

Da wannan ta shiga Taimaka masa, har ya shiga wanka, yana fitowa ya samu ta cire mishi wasu kayan sawa, zai da ya shirya ta rike hannun shi zuwa inda zai ci abinci. Zama yayi yana wasa da abincin.

"Allah ya baka nasara, kaci abinci" wani irin fisgota yayi tare da rungume ta, ita kuwa ta bashi wani irin lafiyayyen runguma, ba tare da sun fahimci kome ba, kawai suka fada wata irin duniya, sanin cewa bakin kofar akwai dogarai yasa shi daukar ta cak zuwa turakar shi. Daga shi har ita burin su,.shine amanta da damuwar su, bai san wani irin so da bukatar ta yake ba, sai dai wannan ita ce rana na farko da suka zama kamar basu ba, domin gata nan yar mitsitsiya, ta dauke nauyin shi da bukatar shi, tsabar jaraba tun daga gado saman Kilishi, wurin hutawa duk sai da suka yada zango a wuraren, kafin suka samu nutsuwa a lokacin suna kwance a tsakar dakin.

Juya mishi baya tayi tana murmushin jin kunya.

"Fulani Minani" ya kira sunanta yana shafa bayan ta, ita kuwa burin ta bai wuce ta dauko mayafin da zata rufe jikin ta ba, janyo ta yayi yana kara yaba halayyar ta, na kunya da kawaici. Tashi yayi ya dauke ta yana faɗin.

"Ni ba mijin ki ne kuma sirrin ki, idan har kika cigaba da kunya ta wacece zata min yadda kike min?" Boye fuskartar tayi a kirjin shi, haka suka yi wanka har aka gama, bata d'ago kai ta kalle shi ba, asalima yau ya lura wani irin yanayi yake ciki, domin taki saka kaya amawali ta daure a kirjinta, kuma har a dare sallah ne kaɗai yake bada damar saka kaya. Taki yarda su kuma magana akan kwarkwarah, asalima mantar da shi zancen tayi sai ma shagalin da take mishi, tsawon kwanaki suna kara kaunar juna, da ɗaukar bukatar juna.

Da fari burin magauta ita Fulani Aminatu tace ba ta amince ba, sai a goranta mata tare da tuna mata ai ita yar kwarkwarah ce, sai aka yi rashin dace bata nuna haka, musamman wani hidimar da aka yi a gidan galadima, suka hadu akayi ta jefa mata habaici yar batalikan nan bata d'ago kai ta lalle su ba, asalima nunawa tayi bata san suna yi ba. Kuma haka ya faru ne sakamakon kokarin Innayoh ta ce mata.

Zasu nemi gaya Miki magana! Zasu takale ki da haibai ci. Zasu bakanta musu ki nuna musu ke mutum ce ba dabba irin su ba, don Allah kar ki nuna ko akan fuskar ki

Shi yasa suna fara cusguna mata, suka ga fuskar ta sau murmushi take. Asalima tashi tayi ta koma wurin matar galadima, babu abinda yake kara bawa kowa haushi yadda shigar ta, nutsuwar ta kamalarta. Bata yi kama da mutanen da basu san ciwon kan su ba, har suka bar gidan bata d'aga ido ta kalle su ba, asalima sai suka fara kokarin dakatar da junan su, domin an ce shiru ma magana ce.

Tsakanin ta da mijin ta, kamar hanta da jini domin babu ruwan su, duk abinda za a yi sai ayi.

A ranar wata juma'a, aka shigo da kwarkwarorin cikin masarauta. Sai da aka kawo mata su, tana kallon su daya bayan daya. Idanun ta ne ya sauka akan Bingel, cike da mamaki take kallon ta. Kafin ta cewa Innayoh.

"Innayoh na gan su, Allah ya basu Sa'a da iya daukar kome"

"Amin uwar ɗakina" sannan aka wuce da su,. Shiru tayi tana nazarin wannan al'amarin domin gudun kar ce zata hana shi zama da mace yasa bata yi wani abu ba.

Da daddare, tana turakar shi shi, kanta a sunkuye tana yanka mishi lemo ta ce mishi.

"An kawo yan matan fa"

"Sai aka yi Ya?"

Ya tambaye ta,

"Wai dama na tuna maka ne, daga gobe zasu fara amsar ragamar aikina."

"Guduna kike Aminatu?"

"A'a ba haka bane" ta fada tana mika mishi lemon,

"Toh ki kyale su, a wurin"

"Amma"

"Amma me?"

"A'a babu kome" daga haka ya janyo ta jikin shi, sannan ya shiga bata labarin abinda ya faru, nan ta manta da batun kwarkwarah ta shiga dariya.

--

"Wai kuna ganin har sarki Bello zai nime mu?" Daya cikin kwarkwarah ta tambaye sauran,

"Me zai hana, mun fi matar shi kome fa me zata nuna mana da ya ce farin fata."

Bingel na gefe bata ce musu kome ba, har suka gama hiran su.

--

Kamar yadda dai suka saba, haka ya shiga karatun d'aga buje, babu ruwan shi da wani abu wai da aka ajiye mishi, sosai ya gurje matar shi. Ai kuwa yana zuwa fada aka kawo korafin an kawo mishi mata amma Fulani Aminatu ta hana su isa gare su, zasu dauki mataki akan shi da Aminatu.

Murmushi yayi tare da cewa.

"Idan kun dauki matakin iya kaci kuce na bar muku mulkin ku, kuma dama kamar kun san akan k'aya nake, idan kuka amsa sai na dauki mata na mu bar Masarautan babu wanda zai kuma ganin mu balle ya dame mu. Suma matan da kuka bani kazamai ne da suna da tsafta ba zan guje su ba," daga haka ya kade alkyabbar shi ya bar su a wurin tunda sune suka zabi haka bai ji yayi danasanin maganar da ya gaya musu ba, tunda suka fahimci hanyar da zai balle mulkin ma yake sai suka shafawa kan su ruwan sanyi, domin haka ba karamin koma baya bane a cigaban su.

Bayan wata guda, lokacin Fulani Aminatu tana hutun Sallah, a lokacin Innayoh ta mata magana akan lallai a shirya daya daga cikin kwarkwarah ta tafi wurin mai Martaba, bata so ba domin shiru tayi taki magana, ita kuwa Innayoh bata kuma mata magana ba, amma tayi gaban kanta, domin kuwa bata jira abinda Fulani Aminatu zata ce ba, ta bada umarnin a shirya daya daya cikin yan matan nan, a kai wa Mai Martaba....

_____

Wayar Charge na ya kone, wannan ma dakyar na muku wannan domin muna fama da rashin wuta ga kuma bani da abin Charge sai kun ganni kawai

Please vote and Comments share...

#Mai_Dambu..

[5/16, 5:30 PM] Pearl crystal: https://www.wattpad.com/1225391554?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=share_published

KALLABI...

A Tsakanin Rawuna

Mai_Dambu.

EWF

Gaisuwar wannan shafin naki ne Asli Smasher Kaunarki da Fulani Aminatu ta musamman ne❤ma taya Fulani Aminatu kaunarki tace a mika sakon godiya Sosai sosai amma zama da Kwarkwarah fa jazamun ne

BABI NA ASHIRIN DA BIYAR

Sosai Innayoh ta tura aka gyara daya daga cikin yan matan, sannan ta dawo wurin Fulani Aminatu.

"Na miki abinda ban tab'a b'ata ba, amma qaddarar mutum yana zane ne tun daga ranar da aka haife shi, kiyi hakuri da abinda nayi amma ya zama dole ne nayi haka, na tura mishi daya daga cikin su."

Kallon Innayoh tayi taga ta cika mata Idanu, dan haka tayi kasa da kai tace mata.

"Duk yadda kika yi daya ne." Daga haka ta cigaba da gyara kumbar ta, ta wani dauke kai kamar bata taɓa magana ba, murmushi Innayoh tayi domin bata dauka Fulani Aminatu zata iya bayyana kishin ta kai tsaye haka ba, har zata bar wurin ta ce mata.

"Duk abinda zan yi ba zan taba yi dan jin dadin kaina ba, kuma ba zan yi dan na kuntatta miki ba, zan yi ne domin kare mutuncin ki" daga haka ta bar wurin, bata ji zafin yadda Fulani Aminatu tayi ba dan tasan dole tayi kishin Mijinta, abu na gaba shine addu'a kawai domin abinda tayi ya samo asali ne daga Inna Marwa. Ita din kusan Gwaggo takewa Sarki Bello kuma yau kwana huɗu kenan da zuwan ta. Sun je sun gaida da ita da Fulani Aminatu, kuma Alhamdulillahi Innah Marwa ta yaba da Aminatu sai dai bayan sun bar shashin ta, Ajuji ta ke fadawa Inna Marwa cewa.

"Uwa yarinyar nan bata haihuwa, kuma an bawaai Mai Martaba kwarkwarah yaki amsa"

Juyawa Inna Marwada tayi sannan tace mata.

"A kira min Jakadiyar Gobir"

"Wo!" Ta rike bakin ta, sannan tace mata.

"Baki da labarin Sarki Bello yasa a kashe ta, amma don Allah karki ce a bakina kika ji" shiru Inna Marwa tayi sannan ta ce mata.

"Toh tashi ki ban wuri, kuma a kira wacce take matsayin Jakadiya yanzun"

"Ai Innayoh ce wacce suka shigo tare da Aminatu"

"A kira min ita"

"TOH" kowa da aka kira Innayoh, tazo ta durkusa a gaban Inna Marwa, ta kuma kira Sarki Bello da galadima, suka taru a gaban ta.

Shiru tayi kafin ta d'ago kai, sannan ta ce musu.

"Innayoh kece Jakadiya ko?"

Gyara durkuson tayi, kafin ta ce mata.

"Eh Fulani Inna Marwa" murmushi dattijuwar tayi sannan tace mata.

"A matsayin ki ba iya Jakadiya ya kamata ki dauka ba, hatta fannin uwa ya ka mata ki dauka, shin uwar arziki zata so ganin ana jin ciwon abinda yake faruwa sanadin Yar ta?" Sunkuyar da kai tayi tare da damke zaninta, sannan ta girgiza kai.

"Toh me yasa Fulani bata bawa kwarkwarorin nan damar shiga wurin mai Martaba ba?"

"Laifina ne Fulani Inna Marwa. Nice ban tunatar da ita ba, insha Allah haka ba zai kuma faruwa ba"

"Yana da kai ki kara mata kima ta hanyar nasiha da tunatarwa, idan haka samu haka ba makawa an kashe bakin masu kaiwa da komawa, duk lokacin da Fulani ta shiga kwanakin ta na al'ada a tura mishi wacce zata dauke mishi laluran kwanakin, idan ta dawo kuma a dakatar da kowacce mace shiga turakar shi sai ta sake shiga kwanakin" idanun Innayoh ne ya cika da kwalla ta rasa kuka zata yi ko farin ciki, sannan ta cigabq da cewa.

"Yan mata hudu sun mishi yawa a bar daya me kyakyawar sura da nutsuwa"

"Toh Fulani Inna Marwa an gama" haka ta gama tsara kome, sannan ta sallami Innayoh, juyawa kan Galadima tayi sannan ta ce.

"Wani kokari kayi na matsalar Aminatu da Bello" gyara zama yayi tare da sunkuyar da kai kasa ya ce.

"Inna Marwa, basu da matsalar kome. Jinkiri ne kawai daga Allah, idan da zaa yi hakuri sai abin ya kasance"

"Ban gane ba?" Ta kuma tambayar shi,

"Dukkan su lafiyar su lau" ya fada a hankali, Inna Marwa irin matan nan ne da suka taso cikin iko da bada umarni, abinda ta sani shine mulki ya bi jikin da ta jinin ta, sannan tana cikin manyan matan masarautan Sokoto, domin tun zuwan shehu Usmanu danfodiyo, aka bada auren ta ga Wazirin Sokoto kuma babban Almajiri Shehu Usmanu danfodiyo, sai kuma aka yi dace mijin ta an bashi Sarkin rikon kwarya, har ya rasu, wannan dalilin yasa ta jin gaba da baya mulki ya samar da ita, bata cika zuwa ba daga biyar ko goma, amma idan tazo kowa na fadar nutsuwa yaƙe, (zamu iya kiran da da dowager Mother she is not empress but she has a more powerful than king) Dan haka ko a Sokoton tana da tarin Darajojinta, ga ilimin addini da Allah ya bata, haka ya cire mata kyashi da hassada, sannan kaifi daya ce bata magana biyu, idan tana wuri ba a kawo mata wargi, asalin bagobiyar ce da ta samu damar yin rayuwa kamar kowacce matar sarki, sannan tana Tausayin Fulani Aminatu, domin tana tsakiyar makiya ne, tun kafin ta iso aka gaya mata cewa Bello ya amshi auren bafulatana kuma sai yadda tayi da shi, a tunanin ta zata samu hamshaqiyar mace abin tausayi sai ta ga yarinyar kusan sa'ar jikan ta na goma sha biyar ce, sannan tasan tasirin kiyayyar kowacce masarautar domin ita ɗaya ce bagobiyar a cikin masarautar Sokoto, dan haka ta sha wahala da mijin su da kuma

kishiyoyin ta da kwarkwarorin sarki a lokacin, kai tun kafin ya zama sarki ma yana da kwarkwarorin biyar da yazo ya zama sarki sai abin ya ta'azzara har ta kai sai tayi sama da wata biyu bata saka shi a idanun ba, domin ko tace tana son ganin shi basu barinta ta isa gare shi. Idanun ta ne ya cika da kwalla. Domin tuno rayuwar ta, yana yawan saka ta kuka domin bata mori miji ba, sai rabon Yara ne idan ya tsaga toh ko da rana ne sai ya tura Jakadiya ta dauko ta, haka ya faru ne sakamakon mugun son da yake mata, da Kwarkwarah ce ba za'a tab'a damuwa ba sabida sun san ba matar sarki bace, amma matar sarki matukar sarki zai so ta tashiga uku.

"Ka koyawa kanka boye soyayyar ta, domin shine makamin da za a yake ku, ka rungume abinda suka baka." D'ago kai yayi ya kura mata ido. Sannan ya ce mata.

"Inna Marwa idan na ajiye sarautar akwai me tuhumata ne da naso mata ta" rike hannun shi Galadima yayi yana girgiza mishi kai.

Tabbas dan dan uwan ta yayi nisa, itama da haka ta samu yanci a Sokoto da yau bata yi kuka ba.

Sai dai ita mijin yayi kokarin yaki da soyayyar ta ya kuma zauna lafiya, a duk lokacin da yake tare da ita yana yawan gaya mata ya nisan ta kan shi ne domin ta zauna lafiya da sauran matan da Alummomin masarautan,. Kasancewar ta bagobiyar a cikin Masarautan fulani. Dan haka dukkan hanyar da zai nisanta shi da ita yake bi, ba wai dan baya son ta ba. Idan ta kama ya nisanta kan shi da ita har abada toh zai yi kuma zai iya domin ita da yaran ta su zama abin alfahari a cikin Masarautan, kuma izuwa yau itace mahaifiyar Sarkin da yake mulki.

Gyada kai tayi kwalla zuba mata ta ce mishi.

"Kana zaton dan ka ajiye mulki zasu fasa yakar ka ne? Kana zaton ko kayi nisa da gida zasu fasa bibiyar ka ne? Kowani motsinka suna tare da kai ita ce basu kauna a cikin Masarautan. Zuwan ta ua kuma karawa mulkin ka albarka, zuwan ta ya saka kaf nahiyar nan babu na biyun ka, daga shekarun da ka aure ta zuwa yanzu ka duba sauran yankunan da suke kewaye da kai? Ka san ko yaki babu wanda ya tunkare ka da shi? Shin kasan me yasa hil ta nime aba da ita? Domin karfin tsafin su ya kara samun daraja, sannan a kodayaushe ko wani lokaci ta haifawa sarki Arkhan da namiji, kenan Masarautan nan kowa yasan abinda yake faruwa kai ne basu bukatar da cigaba dan haka ruwan ka ka zauna da matan ruwan ka ka rabu da su amma tabbas shirin su akan Aminatu rubutacciyar al'amari ne ko ba yau ba" sannan ta juya ga galadima.

"Sarkin gida ya gaya min abinda ya faru, waye kuke zargi da sakawa a tare Ku?" Shiru tayi tana kallon galadima. Nan ya shiga mata bayani tare da abinda ya sani, sannan ya kara da cewa.

"Ina zargin Yakubu ne, domin na a an zane min shi kwanakin baya, idan ba shi ba toh ban san waye zan kama ba"

"Toh ka tabbatar yayi alaka da Kwarkwarah da aka zab'a mishi sauran a maidawa Chiroma a gaya musu ni Marwa na dawo mishi da tarkacen shi, kwarkwarah daya ta wadatar da shi. Alakar ka da Kwarkwarah ba shi zai saka Aminatu ta wanke kanta ba, sai dai idan yau ta zubda jinin haihu shine kawai zai dakatar da kome, ba naki aminatu bane kiyayyar da ake mata idan baka da lissafi kaima shiga cikin su zaka yi tashi ku bani wuri"

Daga haka ta juya kanta, dakyar ya mike tsaye kamar zai fadi, tana halkance da shi, amma ta dauke kai. Yana fita kuwa ya nemi wuri ya zauna, wani irin zafi yake ji.

"Dama abinda ya hanaka tsayawa a tsagina kenan?"

"Abubuwa dayawa sun faru amma yanzu a dakatar da wannan batun mu fuskanci gaba."

"Amma kasan ina sonta ko?"

Ya tambayi galadima.

"Na sani" idanun shi ne suka yi wani irin ja...

Wannan shine abinda ya faru, dan haka Inna Marwa tana cikin masarautan kuma ba a daina kawo mata gulmace-gulmace ba, dan ma ta toshe kunnen ta, ta kima fatattaki masu kawo mata gulmar.

Koda Innayoh ta tafi dakin bayan tare da taimakon wasu manyan bayi mata suka shiga duba yan matan sai dai cikin ikon Allah zun zabi Bingel duk yadda aka yi sai da ta fi sauran matan dan haka suka tambayi sunan ta.

"Ya sunanki?"

"Yahanasu" janta aka yi zuwa wani sashi na daban, aka shiga mata gyaran jiki, tsawon kwanaki uku ana gyara mata jiki, sannan Innayoh ta sallame sauran yan matan, ita kuma aka kai ta wurin Inna Marwa. Kallon fuskar ta yayi sannan ta ce mata.

"Ki sani ba wai zaki iya zama wata abu me daraja bane ke kamar juji ce, a duk lokacin da ya kwaso sharan shi akan ki zai watsa, bari na gaya miki ko me zaki yi ba zaki tab'a samun damar inda kike ba, ki ajiye a ranki Aminatu bata miki kome ba, idan kuma wani abu ya biyo baya, zamu saka a zartas da hukuncin bisa ga abinda kika aikata"

Shiru tayi, bata tab'a tsannan kanta ba sai yau dan haka bata iya magana ba, domin akan ta isa ga sarki Bello sai da aka gaya mata magana. Dan haka Inna Marwa ta cewa Innayoh.

"Ki sanar da Fulani Aminatu, za'a kai Bingel ga Bello tayi hakuri duk wanda ya zabi tafarkin gaskiya Allah zai bashi ikon cimma inda yake."

Gyada kai Innayoh tayi sannan ta fitar da Bingel, aka mai da ita inda suke, sannan aka ware mata bayi mata biyu, daya babba me suna Lanta da Goshi,. Aka bata su zasu taimaka mata da duk abinda take bukata, sai gefe guda kuma aka bata wata dattijuwa me suna Larai, ita kuma tana saka ido ne akan duk wani motsin ta. Wannan shine abinda ya faru.

*

Tunda Innayoh ta gaya mata cewa ai za a tura kwarkwarah sashinsa, ta shiga daki ta rufe kofar, shima da kan shi yazo amma fir taki bude mishi kofa, abin ya bashi haushi dan haka ko da ya fusata dukar kofar yayi sai da kofar ta karye. Nufarta yayi tana zaune. Durkusawa yayi a gaban ta.

"Ko duniya zata juya Miki baya ina tare dake, me yasa zaki tona min asiri domin jin dadin wasu? Me yasa zaki juya min baya domin wasu? Kin san yadda nake jin ki a raina? Kin san yadda na damu dake? Me yasa ba zaki gane ba, don Allah kar ki kuma nisanta kan ki dani, ina iya tasa rawa farin cikin, indai ke zaki rayu cikin salama...

#Mai_Dambu

[5/16, 5:31 PM] Pearl crystal: KALLABI....!

A Tsakanin Rawuna

Mai_Dambu

EWF

BABI NA ASHIRIN DA SHIDA

Muryan shi na rawa ya rike hannun ta.

"Zai fi kyau ki min duk borin da zaki yi, kin ji ki yarda Sarki Muhammad Bello bawan ki ne ke daya." Ya rike hannun ta, idan mutum yaga yadda sarki Bello ya koma sai ya tausaya mishi, domin baki daya ya sussuce, rufe mishi kofa tayi amma ji yake kamar zuciyar shi tana ciwo. Saka hannun ta yayi a kirjin shi.

"Kin ji yadda yake bugawa, daga ranar da aka ce babu ke wallahi azim bata da amfani a jikina, kece zuciya ta. Wannan domin na rayu nake tare da ita, bayan nan ke kece dukkan min nasara ta, idan na rasa ki toh ba mamaki ba zan kuma amfanar rayuwa ta ba, don Allah ki rufa min asiri, motsin ki kawai ake bukatar kiyi iya shi zai iya hana ni sukuni. Kwarkwarah ce bata da iko, kawo kunnen ki na gaya miki dan ko dakin bana son yaji abinda xan gaya miki" share kwalla tayi ya mika mishi kunnen.

Magana yayi mata, ta d'ago kai tana kallon shi, rike hannun ta yayi tare da cewa.

"Na rantse da Allah sarki na miki alkawarin haka ko muna tare ko bamu tare"

Ya fada yana kallon yadda ta kuma narke mishi, babu wani bacin rai a fuskar ta, sai dai kishin da yake hangowa,motsa baki tayi zata mishi magana ya kai bakin shi kan nata, kallon shi tayi ido cikin ido, kashe mata ido yayi, ya shiga taune bakin kamar zai cinye ta,, a hankali ya tura hannun shi cikin rigarta, kafin ta san me yake shiri yayi sama da rigar ya wulli da ita, tun daga bakin ta yake lashe ta, wani irin yanayi ya wurgata. Abin sai ya hadu biyu, ga sarkar jinin al'ada gata Ni'imar da ake tsokano ta, kai bakin shi yayi wuyar ta, yana wani shegen lasarta ya kuma dawowa habb'arta yana lasar wurin da cizon shi. K'amk'ame shi tayi ta fashe da kuka tana faɗin.

"Baffa'm don Allah ka bari zan bata jikina"

"Minani ba zan bari ba, duk ranar da na kuma kamaki da laifin rufe min daki, sai nasan me xan Miki amshi horon ki" ya dukkufa da aikin arziki, bai kuma haukata ta ba, sai da ya tsaya akam Cibiyar ta, wani irin mika take tana kuka tare da niman ya kyale ta, amma bawan Allah nan ta shiga jifarta ta da salon shi masu mantar da mace (□😂 malam Bingel na jiran Zariyar wandon ka□😂)

Ai fa kamar zata suma wani irin rawa jikinta ya kama sai dai na shi rawan da jikin shi yake Naci kaniyar nata, wani matse cinyoyin ta yayi tare danna Zariyar shi akan tsakanin cinyarta, ya haɗe cinyoyinta ya matse yana wani irin gurnanin (□😂 yau sai hakuri mun sake layi dayawa ayi ta salati 😂😹□) zur-xur ya watsa mata ruwan shi a jikin ta, janyo matashi tayi ta rufe fuskar ta, sam taki yarda ta kalle shi, dariya yayi ta mata karshe da yaga taki kula shi kawai ya fara mata cakulkuli, babu shiri ya shiga zillo, har ta fada kirjin shi. Kwantar da kanta tayi a kirjin shi tana ajiyar zuciya. Shafa Bayan ta ya shiga yi yana rarrashinta,

"Ki gyara jikin ki kin ji ko!" Ya fada bayan ya ja mayafi ya bar dakin shima bangaren shi ya nufa yayi wanka tare da sallah da ta kubce mishi, yana murmushin jin dadi. Sai yanzu yake kara jin kaunar Yarinyar sama da koda yaushe.

Bayan sallah Isha aka shigo da Bingel bangaren shi, yana rubutu tare da saka kan shi aikin zanen Fulani Aminatu. D'ago kai yayi ya kalle ta sanye take da farar alkyabbar, sau daya ya Kalle ta bai kuma sha'awan kallon ta ba, tun fil azal Allah ya saka mishi kyamar kwarkwarori, abubuwa dayawa na faruwa da su, dan haka yaji har ya koma ga Allah ba zai tab'a ajiye ta ba, sai dai ƙaddara ta riga fata. Yana zaune ta sabule alkyabbar, sanye take da wasu irin kananun zanin saki, K'ugunta cike yake da dam da jigida, irin ta mutanen kurmi, mazaunanta zuwa kirjinta an rufe shi da mayafan, a hankali ta shiga warware su.

"Koma inda kika fito" cike da mamaki ta kalle shi. Mikewa yayi a hankali sannan ya tako gaban ta.

"Har abada ba zan taba kallon wata mace ba, dan haka bana jin kin cika macen da xan kalla idan ina bukatar mace Ni xan nimawa kaina wata wasu ba, kin zata dan mun je garin ku sai na amshe ki? Ke baki san wani abu ba, yar da take da Albarkan iyaye da a Ubangiji nake nima bake da kika yi gudun wuce Sa'a kar na kuma ganin ki a turaka ta, domin xan baki mamaki fita nace, sarkin gida kar a kuma kawo min inuwar ta ma"

"Maza fito, an gama ranka shi dade" tisa keyarta aka yi gaba, sannan ya sauke ajiyar zuciya yayi sannan ya ce a ran shi.

Taya zata burge ni? Duk abinda ake nima a wurin mace Aminatu na dasu, tun babu kome nake taɓa su, balle kuma yanzun da suka cika kirji

Ya fada yana murmushin jin dadi, har sai da wakilin babban birnin hada soyayya ya motsa matse shi yayi domin baya son RIGIMA irin na shi.

*

Washi gari haka labarin bai kwanta da Bingel ba ya zaga Masarautan, Inna Marwa ta mata tass, domin tasan ta gayawa Iyayen gidanta ne, su kuma suka sake labarin shi da ya fisu danyen kai yasa aka kawo ta gaban bayin Masarautan za'a zane ta.

....

"Don Allah ki tashi kiyi wani abu zane ta za ayi."

Cikin ko in kula ta ce.

"Toh Innayoh ina ruwan mu"

"Tashi muje zaki gane haka" babu shiri Innayoh ta fita da ita, daidai ana daure ta, sarkin gida yana shafawa dorinar shi mai.

Sai kuka take shi kuwa mai martaba ya bar wurin ma, yana tafiya daga nesa Innayoh ta mata alama da fuskar roko. Yana magana da galadima da yake tausar shi yaji muryan annurin zuciyar shi ta kwaso da gudu tana faɗin.

"Saurayi!!" Wani irin abu ya ji ya cika mishi kai ya tsaya cak.

"Yawwa jima! Dan dakata ai baka gama aikin ba!" Ta zare mayafin ta ta daura a K'ugunta tam, sannan ta sake murmushin. Takowa take cikin ganiyar kuruciya da yarinta, ita kanta bata san tana wani abun ba, sai dai shi ya hangota tana juye Kuruciyar ta. Dan gulma shi kan shi galadima yaki tafiya. Kamar wacce aka ingiza ta ya kwashi wani mahaukacin gudu. Ta nufe shi. Tana isa gaban shi ta fada kirjin shi, wani ajiyar zuciya ya sauke zuciyar shi tana bugawa a guje kamar wanda yayi wasan tsare.

Bakin ta ta kai kan na shi, sannan ta kyalkyale da dariya tana fadin.

"Baffa'm a yafe mata bata san dokokin Masarauta ba, shigar sojar badakare ta mishi kaji saurayi" yadda tayi maganar yasa shi dauke ta cak ya nufi bangaren shi yana cewa galadima.

"Toh Galadima ka dai ji abinda tace a yafe mata dan haka ayi yadda ta ce"

"Toh Sarkin Gida ka dai ji Fulani tace a yafe mata, Uwa Mabada mama kenan An gama Ranki shi dade Mahaifiyar Sarkin gobe" inji Galadima, dan dole aka janye zane Bingel, cike da wata irin kiyayyar Fulani Aminatu Chiroma ya bisu da idanu,babban burin shi ya mallaki Aminatu domin an gaya mishi itace kashin bayan dukkanin mulkin Bello, shi yasa yayi fatan sanadin da zai raba su, shi ya same ta, amma kullum kullum kara mannewa junan su, suke.

  Ita kuwa makira wani narkewa tai a jikin shi tana wasa da rawanin shi, sai ga fadawa da sauran yan majalisar sarki sun shiga juyawa cike da kunya, kowa na cewa lallai mai martaba da Fulani basu da kunya a gaban jama'a ma!

(Ji fa sai kace akan su ake! So karku manta hawai asalin al'adar nake son watsi da shi ba, duk wanda ya ga cover din shi yasan ancient love story ne ba wai old model ne, dan haka ayi hakuri dani labarin d'aga buje dai ba zamu fasa shi ba😂😹 sai dai mun iya takun mu ko me kuka ce?)

Yana shiga cikin bangaren shi ya dire ta, ya shiga kallon kugun ta, cire alkyabbar yayi da babban rigar shi ya watsar ya kuma cire rawanin shi.

"Don Allah maimaita min tafiyar nan" juyi tayi a gaban shi tana dariya, aikuwa ya shiga takun kamar mazaunin ta zasu sauko kasa, wani dadduma ya kai mata tare da mannata da kirjin shi yana jin wani tulin amabaliyar son kasancewa da ita, juyar

da ita yayi ya shiga matse ta yana kara Haukace mata, karshe Fadar da bai je ba kenan (😂😹 chaii)

Aikuwa cikin fushi Chiroma ya nufin bangaren Inna Marwa, ya gaishe ta cikin girmamawa.

"Chiroma da alamu kana ta cewa" gyara zama yayi tare da kwashe Abinda ya faru ya gaya mata. Murmushi tayi tana me ajiye Alqur'anin hannun ta.

"Hana shi hukunta yarinyar da tayi ne ko kuma akwai abinda yake kasan ranka bayan haka?" Ta tambaye shi, jikin shi da bakin shine ya fara rawa. Murmushi tayi, Inna Marwa Allah ya mata wani irin baiwa ne na kana zuwa gaban ta domin wani manufa take iya d'ago ka, daga maganar ka kawai Allah yake bata sa'ar fahimtar ka, idan kuma ta kalli fuskar ka, jikin ta yana bata wani abu na daban akan ka, shi yasa dayawan yan majalisar sarki sun ki yarda su isa wurin ta, ba karamin abu bane ta wurga musu magana a bakin su, sannan su fitar da abinda yake ran su.

"Fisabilillahi Inna Marwa, taya zai dauko bafulatana a cikin masarautan gobir, baya ji baya gani akan ta. Dan kawai ance mishi ita yar baiwa ce,.tana bunkasa mishi mulkin shi."

"Eh toh ban fahimci abinda kake kokarin fada, Imma ka min bayani yadda majiyyai na zasu tsinkaya Imma ka kwashi sawayen ka ,.kabar min bangare na"

Kamar wanda ake tsikaran shi da allura ya fara gaya mata, abun da yake ran shi, sai da ta bar shi ya gama bata labarin ta ce mishi.

"Ba Bello bane matsalar ku ita Fulanin ce baku bukatar ta, sannan kowa ya samu Fulani ba zai taba barin wanin shi ya samu ba, Chiroma ban san me zan gaya maka ba, amma ka boye ciwon da yake ranka, ba iya yau na fahimci adawar ka ba, idan ka boye yayi maka amfani idan ka cigaba da bayyana shi zaka wahala, kamata yayi ka haɗa kan su, ba wai ka raba kan su ba, na sha mamaki akan abinda ka fada wato Bello bai da ce da Aminatu ba, toh shi kenan zaka iya tafiya"

Daga haka ta nuna mishi illar hassadar da ya kasa boyewa,ta mishi hannun ka me sanda, yadda me hankali zai fahimci abinda ta gaya mishi gaskiya take fada.

A bangaren Bingel ba karamin al'amari ta tsinci kanta ba, domin bata san zata fuskanci tozarci haka ba, daga can ɓangaren Inna Marwa ta tura a kira ta, ta mata tass sannan ta tura aka kira matan Masarautar baki daya, ta ci mutuncin su baki daya har sai da suka yi fatan Allah yasa ta bar masarautan akan lokaci.

Ta ce musu.

"Kuna renon akuya da fatar kura ku ajiye a ranku matukar baku nime takunkumi ba, zata cinye duk abinda ta samu maza ku bar min bangare na."

A can bangaren Baffa'm, mantaewa suka yi da duniyar kowa suka shiga duniyar su iya su daya suka fahimci yaren su, ai kamar yadda ya saka a ran shi bayan magariba ya dawo da ita, Innayoh ta saka ta agaba da gyaran jiki wani irin gyara ake mata, sannan Inna Marwa ta sa Innayoh hanata fita, aka tura mishi Bingel aikuwa ya koro ta, abin dariya idan kuma ya nime ganin Fulani Aminatu a hana shi, wannan abin haushin kamar zai tadda fadar karshe daina zuwa zaman fada yayi....

#Mai_Dambu